


# TAMBAYOYIN

## YARA AKAN IMANI

ABDULLAH HAMD ARRAKF

# TAMBAYOYIN YARA AKAN IMANI

ABDULLAH HAMD ARRAKF



مركز أصول
OsoulCenter

This book has been conceived, prepared and designed by the Osoul Centre. All photos used in the book belong to the Osoul Centre. The Centre hereby permits all Sunni Muslims to reprint and publish the book in any method and format on condition that 1) acknowledgement of the Osoul Centre is clearly stated on all editions; and 2) no alteration or amendment of the text is introduced without reference to the Osoul Centre. In the case of reprinting this book, the Centre strongly recommends maintaining high quality.

+966 11 445 4900
+966 11 497 0126
P.O.BOX 29465 Riyadh 11457
www.osoulcenter.com

بسم الله الرحمن الرحيم

DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA,
MAI JINKAI



# GABATARWA

DUKKAN GODIYA TA TABBATA GA ALLAH, TSIRA DA AMINCI SU TABBATA GA MAFIFICIN ANNABAWA DA MANZANNI, ANNABINMU MUHAMMAD ((S.A.W)) DA MUTANEN GIDANSA DA SAHABBAN SA BAKI DAYA,

BAYAN HAKA:

A SHEKARUN FARKO NA YARO YANA DA MUHIMMANCI SOSAI A GINA YADDA HANGEN YARO YAKE GAME DA SAMUWAR ABUBUWA, TA INDA AKE KIRGA FAHIMTAR DA AKA GINA HANKALIN YARO AKANTA A MATSAYIN TUSHEN FARKO NA GINA MUTUNTAKARSA A DUKKAN BANGARORIN RAYUWARSA, WACCA YA KAMATA ACE TA KASANCE TA DACE DA BUKATUWAR YARO TA RAYUWA DA ZAMANTAKEWA DA ADDINI, KUMA AIKI NE NA GINA YARO CIKAKKEN GINI DA ZAI TAIMAKA MAI WAJEN TABBATUWA DON YA TSALLAKE MATSALOLIN RAYUWA YA KUMA CI GABA DA TAFIYA A MATSAYIN SHI NA DAN ADAM MAI AUNA ABUBUWA DA KIRKIRAR ABABE DA AIKATA SU DA KYAU, DAGA ABIN DA YAKE JI YAKE KUMA GANI YARO ZAI TSARA ABUBUWAN DA SUKA KEBANCE SHI A WANNAN DUNIYAR DA DUKKAN ABINDA ZAI SAURA A RAYUWAR SHI BAYAN HAKA, BABU WANI ABU FACE CANZAWA DA KUMA CI GABA GA WANNAN HANGE MAI TUSHE GWARGWADON YANAYIN DA ZAI BI.

KUMA TUSHEN ILIMIN DA YARO YAKE DOGARO AKANSU A WANNAN MATAKIN SUNE IYAYENSA, DON HAKA, SHIRYUWAR YARO TANA DAGA INGANCIN TARBIYYAR IYAYE NE, ALHAKIN KOYAR DA YARAN YANA KAN SU. SHIYASA MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE: ((DUKKAN KU MASU KIWO NE KUMA DUKKAN KU ABIN TAMBAYA NE AKAN KIWON KU)) [BUKHARY 2558, MUSLIM 1829]. WANNAN NAUYIN DOLE NE A KULA DA SHI KUMA A DAGE WAJEN TARBIYYA DA ILIMANTARWA.

TUNDA MUNA RAYUWA NE A ZAMANIN DA SHA`AWA DA KUMA SHUBUHA TAYI YAWA, YA ZAMA WAJIBI GA IYAYE SU DAGE SUYI TARBIYYAR `YA`YAN SU DA KUMA DAGEWA YA ZAMA MAI CIKE DA GASKIYA DA KWADAYI DA DAGEWA. WANI IRIN DA IYAYE SUKA DASA A ZUKATAN `YA`YAN SU YANA FITAR DA TSURO AIKI NE MAI CI GABA GA IYAYEN BAYAN MUTUWARSU, SAI DAN YA ZAMA SHI NE ABIN DA YA RAGE NA AIKIN KIRKI GA IYAYE WANDA ZAI CI GABA DA YADUWA BAYAN MUTUWA. KAMAR YADDA MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE: (KO YARO NAGARI DA ZAI YI MAI ADDU`A). [MUSLIM 1631]

`YA`YA A TAKAICE ALLAH YAYI MA IYAYE WASICI AKAN SU INDA YACE:

{ALLAH YANA YI MUKU WASIYYA GAME DA `YA`YAYEN KU} [AL-NISA`I: 11].

MA`ANA:

`YA`YANKU YA KU TARON IYAYE AMANA NE AWAJENKU, ALLAH YA MUKU WASICI AKAN SU DA KU TSAYA KU KARE ABINDA ZAI AMFANE SU A ADDINI DA DUNIYA, KU KARANTAR DA SU KU LADABTAR DA SU KU KIYAYE SU DAGA BARNA KU YI MUSU UMURNI DA YIN BIYAYYA GA ALLAH DA LAZUMTAR TSORON ALLAH A KOYAUSHE. KAMAR YADDA ALLAH ((S.W.T)) YA CE: {YAKU WADANDA SUKA YI IMANI KU KARE KAWUNAN KU DA NA IYALAN KU DAGA WUTA} [AL-TAHRIM:6]. AN YI MA IYAYE WASICI AKAN `YA`YAN SU, KODAI SU TSAYU AKAN WANNAN WASICIN KO KUMA SU BAR SU SU FADA WUTAMAI RADADIN AZABA DA UKUBA TA TABBATA A KAN SU, WANNAN NA NUNI AKAN CEWA ALLAH ((S.W.T)) YAFI RAHMA SAMA DA BAYINSA, KUMA FIYE DA IYAYE SABODA YAYI WASICI GA IYAYE AKAN `YA`YA DUKDA TAUSAYIN SU AKAN SU.

IDAN TARBIYYAR YARO TA KASANCE TA INGANTA TUN ACIKIN GIDA TO ZAI IYA MU`AMALA DA MUTANEN WAJE TA FUSKA MAI KYAU,SANNAN DUK LOKACIN DA AKA SAMI WATA TAWAYA A BANGAREN TARBIYYAR YARO TA IMANI WACCE AKA GINA SHI AKANTA ZA`A SAME SHI DA RASHIN DABI`U NAGARI. TARBIYYA BA ITA CE GYARAN KUSA-KURAI BA, A`A ITA CE KOYAR DA YARO HALAYYAR ADDINI DA HUKUNCE-HUKUNCEN SHARI`A DA YIN AMFANI DA HANYOYI DABAN-DABAN WAJEN ASSASSA MAI YADDA AKE SURANTA ABUBUWA DA TABBATAR DA SU ACIKIN KWAKWALWARSA. YANA DAGA CIKIN TARBIYYA MAI BADA TARBIYYA YA ZAMA MUDUBI YA KUMA RINKA YIN WA`AZI KO NASIHA TARE DA BADA KISSOSHI NA MUTANE NAGARI DA ABUBUWAN DA SUKA FARU A ZAMUNAN BAYA DOMIN A FITAR DA INGANTACCEN MUTUM A RAYUWA.

AN KASA LITTAFIN NAN ZUWA FASALI BIYU:

FASALI NA FARKO:

TARBIYYAR GINA IMANI: KUMA YA KUNSHI ABUBUWA DA YAWA AKAN TUSHE DA GINSHIKI WADANDA ZASU TAIMAKI IYAYE WAJEN TARBIYYAR `YA`YANSU DA YARDAR ALLAH,


AMMA BABI NA BIYU, YANA MAGANA NE AKAN (SAMFURA NA ZAHIRI NA AMSAR IRIN TAMBAYOYIN DA YARA KAN YI GAME DA IMANI), WANDA A CIKI AKWAI TARIN TAMBAYOYIN DA SUKA FI YADUWA TSAKANIN MATASA NA KOWANE ZAMANI, MUSAMMAN WAƊANDA SUKA SHAFI RUKUNAN IMANI GUDA SHIDA, DA KUMA BAYANI GAME DA YADDA ZA A MAGANCE IRIN WAƊANNAN TAMBAYOYIN.

**ALLAH YA DATAR DA MU IZUWA HANYAR SHIRIYA.**

**ABDULLAH BIN HAMD ARRAKF**

# ABUBUWAN DA KE CIKIN LITTAFIN


10 GAME DA TARBIYYAR IMANI





TARBIYYAR IMANI GA YARO 26

52 RUKUNAN TARBIYYAR DASA IMANI







AMSAR
TAMBAYOYI
74

92
MISALI NA ILIMI DON AMSA
TAMBAYOYIN YARA NA IMANI




# GAME
# DA TARBIYYAR IMANI






# TARBIYYA

TARBIYYA ABIN BUKATUWA CE NA DAN ADAM, TANA DAGA CIKIN LALURORIN GINA MUTUM, ITACE KAYAN GINA YARO DA BUNKASA SHI TA DUKKAN BANGARORIN RAYUWA. TA HANYAR TARBIYYA NE AKE GINA HALAYYAN YARO NA ZAMANTAKEWA DA ILIMI DA RAYUWA DA LAFIYA DA SAURAN SU. KAFIN MU FARA MAGANA AKAN TARBIYYAR GINA IMANI DA MUHIMMANCIN TA, ZAI YI KYAU MU FAHIMCI MECECE TARBIYYAR ITA KAN TA, ME AKE NUFI DA ITA? KUMA ME MA`ABOTA TARBIYYA KE BUKATA GAME DA ITA?

## MA`ANAR
# TARBIYYA



TARBIYYA AIKI NE MAI MANUFA, WACCA MANUFARTA ITA CE CI GABA , KUMA TANA DA DOKOKI DA KA`IDOJI, TANA KAI WA ZUWA GA GINA DABI`U NAGARI TA HANYAR SHIRYARWA DA HORARWA DA WAYARWA DA TARBIYYANTARWA DA YAWAN AIKI. KUMA TARBIYYA NA NUFIN KIYAYE ABINDA AKA GINA YARO AKAN SHI DA KUMA KULA DA SHI, TARE DA BUNKASA BAIWAR SHI A RAYUWA, SANNAN A FUSKANTAR DA ASALIN HALITTAR YARO ZUWA GABA DA ZUWA GA ABINDA ZAI TABBATAR DA GYARUWA DA CIKAR TA DA TA DACE DA ITA, WACCA TAKE TAIMAKAWA WAJEN SHIRYA MUTUM YA ZAMA NAGARI DAN YA GINA KAN SHI. KUMA TARBIYYA ITA CE MAKAMMASHIN DAKE SAITA MUTUM A DUKKAN FANNONIN RAYUWA.

## MUHIMMANCIN
# TARBIYYAR IMANI



IMANI SHINE HAKIKANIN SAMUWA BABBA DA KUMA ABU MAI GIRMA DA YA SHAFI MUTUM, YANA DA HANYOYI MABANBANTA ACIKIN TAFIYAR MUTUM A RAYUWAR DUNIYA. ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA CE:

{DAGA CIKIN SU AKWAI WADANDA SUKAYI IMANI, KUMA DAGA CIKIN SU AKWAI WADANDA SUKA KAFIRCE.} [AL-BAKARAT: 253].

KUMA AKAN SHI AKE GINA HALAYYARSU DA AYYUKAN SU, KUMA SHINE ABINDA ZAI BANBANCE MAKOMARSU A RAYUWAR LAHIRA. DAGA CIKIN MATAKAN RARRABEWA A RAYUWAR MUTUM SHI NE RAYUWAR YARINTA SABODA ABINDA AKE DASAWA A ZUCIYAR YARO A WANNAN MATAKIN NA DAGA AKIDU DA DABI`U DA AL`ADU TA FUSKOKIN DA ZAI WAHALAR KO YA CI TURA WAJEN CANZA SHI MAIMAKON TABBATAR DA SHI. KILA MA TABONSA YA ZAUNA A ZUCIYAR MUTUM TSAWON RAYUWASA; DON HAKA TARBIYYAR IMANI A MATAKIN YARINTA TANA DAGA CIKIN MATAKAN GINI DA AKE GINA RAYUWAR MUTUM AKAN TA TSAWON RAYUWARSA A WANNAN DUNIYA.

TARBIYYA A DUNKULE ITACE KULA. BABU TARBIYYA IN BA KULA, KUMA MAFI ABINDA ZA A FI KULA DA SHI SHI NE YA KASANCE A BANGAREN IMANI. MUNA CIKIN ZAMANIN DA MAFI YAWAN MASU BINCIKE AKAN TARBIYYA SUN FI KARKATA A FANNIN TARBIYYAR HANKALI DA JIKI TARE DA WOFANTAR DA BANGAREN IMANI DA RUHI, SUNA FUSKANTAR DA TUNANIN SU WAJEN TABBATUWAR CIN NASARA DA TSIRA A DUNIYA DA SAMUN DUKIYA, BA TARE DA BADA MUHIMMANCI AKAN SHIRIYA WADDA ZATA KAI SU ZUWA GA JIN DADIN LAHIRA BA, WANNAN NE YASA KALLON MU GA TARBIYYA YA BANBANTA SOSAI DA IRIN KALLON DA SU SUKE MA TARBIYYAR.

KUMA BABU TANTAMA CEWA TARBIYYAR IMANI ACIKIN MUSULUNCI ITA CE DAYA DAGA CIKIN RUKUNAN GINA TARBIYYA A RAYUWAR MANZON ALLAH ((S.A.W)) MAI TSARKI. DAGA IBN UMAR ((R.A)) YA CE:NA JI MANZAON ALLAH ((S.A.W)) YANA CEWA: ((DUKKAN KU MASU KIWO NE KUMA KOWANENKU ABIN TAMBAYA NE AKAN KIWON SHI, SHUGABA MAI KIWO NE KUMA ZA A TAMBAYE SHI AKAN KIWON SHI, MACE MAI KIWO CE A GIDAN MIJIN TA KUMA ZA`A TAMBAYE TA AKAN KIWON TA.)) [BUKHARY 2558, MUSLIM 1829].



MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA TUNASAR AKAN GIRMAN NAUYIN DAKE RATAYE AWUYAN KOWANNEN MU, KUMA NAUYI NE DA BA MAKAWA KOWA SAI AN TAMBAYE SHI AKAN SHI: MAI KA GABATAR GA WANDA KE KARKASHIN KULAWAR KA? KUMA YA ZO DAGA MANZON ALLAH ((S.A.W)): (( DUK WANDA ALLAH YA BASHI KIWO BE KULA DA KIWON NAN TA HANYAR NASIHA BA TO, BA ZAI JI KAMSHIN ALJANNAH BA.)) [BUKHARY 7150]. ANAN MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA YI ISHARA ZUWA GA MUHIMMANCIN GABATAR DA NASIHA TA GASKIYA DA AMANA, TA YADDA NASIHA ZATA MAGANCE MATSALAR WANDA AKE MA NASIHA TA KOWANE GEFE. KUMA YANA DAGA CIKIN ABINDA AKE RAWAITOWA A WANNAN BABIN MAGANAR IBN UMAR ((R.A)) CEWA: (KA LADABTAR DA DAN KA DOMIN ZA`A TANBAYE KA AKAN SHI. AKAN ME KA LADABTAR DA SHI? KUMA ME KA KOYA MAI? KUMA SHI ABIN TAMBAYA NE AKAN YI MAKA BIYAYYA DA KUMA BIN UMURNIN KA). [SHU`ABUL IMAN:8141]. ANAN IBN UMAR YANA TABBATAR MANA DA CEWA NAUYIN `YA`YA NA RATAYE NE AKAN WUYAN IYAYE, SUNE MAKOMA TA FARKO WAJEN KARANTAR DA SU DA LADABTAR DA SU.

AN KUMA RAWAITO CEWA TARBIYYA TAFI SADAKA ALKHAIRI, IN DA AKA CE: (MUTUM YA LADABTAR DA DAN SHI YA FI ALKHAIRI FIYE DA YAYI SADAKA DA SA`I DAYA) [ TIRMIZIY:1951] KAMAR YADDA AKA RAWAITO CEWA KOYA MA YARO DABI`U NAGARI YAFI FIYE DA ABUBUWAN DA AKE BASHI. KUMA YANA DAGA CIKIN ABINDA AKE RAWAITOWA (UBA BE TABA BAMA DAN SHI WANI ABU BA FIYE DA DABI`U NAGARI) [TIRMIZI 1952]. DUKKAN WADANNAN NASSOSHIN DA SAURAN SU SUNA NUNI AKAN TARBIYYA DA KARANTARWA SU NE MAFI MUHIMMANCIN ABINDA IYAYE ZASU BAMA DANSU.

MUN KASANCE A BAYA MUNA TARBIYYAR IYALAN MU A YANAYI WANDA YAKE KAMAR A RUFE, AMMA YANZU MUNA TARIBIYYAR AMMA KOFOFIN GIDAJEN MU DA WINDUNAN MU SUNA BUDE




AKAN DUNIYA, DAN HAKA SUNA GANIN ABUBUWA MASU KYAU DA MARA SA KYAU GAME DA DUNIYA. AMMA IDAN BA MU KULA MUN SAN ME KE GUDANA BA DA KYAU HAKIKA MUNANAN ABUBUWA ZA SU KORE KYAWAWA, ZAMU IYA FAHIMTAR ALAMUN CANJE-CANJEN ABUBUWAN DA KE FARUWA IDAN MUKA BADA MUHIMMANCI WAJEN BIBIYAR SAURIN CANJIN DA KE FARUWA A KEWAYEN MU DA KUMA KARANTAR CIGABAN TARBIYYA SOSAI DA KUMA BADA MUHIMMANCIN MAI TARBIYYA AKAN WANNAN, ZAI BASHI DAMA WAJEN KOKARIN DASA IMANI ACIKIN ZUKATAN YARA TUN DAGA GIDA, WANDA KOWA ZAI TAIMAKA WAJEN GINA SHI TA HANYAR ZABAR MAKARANTAR DA ZA A SA YARO TUN DAGA NURSERY HAR ZUWA FIRAMARE DA SAKANDARE WADANDA SUKE KULA DA WANNAN FANNIN NA DASA IMANI. GAFALA DAGA FAHIMTAR ABINDA KE FARUWA A KEWAYEN MU NA NUFIN FARUWAR ASARAR DA BA WATA HANYAR DA ZAMU IYA MAYAR DA ITA. SAI DAI A CI GABA DA TARBIYYA DA HAKURI ZAMU SAMU BABBAN SAKAMAKO DA YARDAR ALLAH. TARBIYYA BA IYA LURAR DA SHI NA WANI DAN LOKACI BANE KADAI, TANA BUKATAR BIBIYA DA CI GABA DA DORA SHI AKAN HANYA.



## TARBIYYAR

# IMANI DOLE CE





LALLAI YARA MASU TASOWA A WANNAN ZAMANI SUNA FAMA DA WATA IRIN FIZGA A ZUKATANSU DA TUNNINSU, SAKAMAKON YADDA ABUBUWA SUKE A BUDE HANHAI, WANNAN YASA IRE-IREN ABUBUWAN DA SUKE KEWAYE DA MATASA SUKE FIZGAR SU TA KO INA SUNADA MATUKAR HATSARIN DA BAI KAMATA MUYI WASA DASU BA, MU KUMA TASHI TSAYE MU KAMA AIKI MAFI WAHALA A SAMUWAR DAN ADAM WANDA SHI NE TARBIYYA. DAGA CIKIN ABINDA KE NUNI AKAN DOLE A GINA YARO AKAN TARBIYYA TA IMANI DA KUMA TSANANIN BUKATUWAR AL`UMMA AKAN HAKA SHINE: ANNABAWA DA SALIHAN BAYI DA MAGABATA SUN KASANCE SUNA BADA MUHIMMANCI WAJEN GINA IMANI DA KARANTAR DA SU AKAN SHI MUSAMMAN MA GA YARA. KADAN DAGA CIKIN MISALAI AKAN HAKA SHI NE FADAR ALLAH MADAUKAKIN SARKI GAME DA ANNABI NUHU ACIKIN KIRAN SHI GAME DA DAN SHI DA KUMA TSORATAR DA SHI GAME DA ABOKANTAKA DA MA`ABOTA BATA, INDA YACE: { YA KAI DANA ZO KA HAU TARE DA MU KADA KA KASANCE TARE DA KAFIRAI.} [HUD:42]. HAKA KUMA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YANA BAMU LABARIN WASIYYAR ANNABI IBRAHIM GA DANSA CEWA: { KUMA IBRAHIM YAYI WASIYYA DA ITA GA `YA`YAN SHI HAKA MA YA`AKUB YA KU `YA`YA NA LALLAI NE ALLAH YA ZABA MUKU ADDINI, DAN HAKA KADA KU MUTU FACE SAI KUNA MUSULMAI} [BAKARA: 132]. KUMA A FARKON WASIIYAR ANNABI LUKUMAN YANA TSORATAR DA DAN SHI AKAN SHIRKA YA CE: {YA KAI DANA KADA KAYI SHIRKA DOMIN SHIRKA ZALUNCI NE MAI GIRMA} [LUKMAN:13]. ANNABI ((S.A.W)) YANA YIMA IBN ABBAS WASIYYA YANA CEWA (( YA KAI YARO ZAN SANAR DA KAI WASU KALMOMI. KA KIYAYE ALLAH ZAI KIYAYE KA, KA KIYAYE ALLAH ZAKA SAME SHI GABAN KA, IDAN ZAKA YI ROKO TO KA ROKI ALLAH, KUMA IDAN ZAKA NEMI TAIMAKO TO KA NEMA TAIMAKON ALLAH.)) [TIRMIZIYYU:2516]. AKWAI KWADAITARWA AKAN GINA IMANI ACIKIN WANNAN.

KUMA DAGA CIKIN ABIN DA KE NUNI AKAN TARBIYYA DOLE CE SHI NE SANIN CEWA KOYAR DA IMANI SHINE GINSHIKIN ILIMOMI DA TUSHEN SHI, IDAN YARO YA SAN IMANI KUMA AKA DASA MAI SHI A ZUCIYA KAMAR YADDA ANNABI ((S.A.W)) YAZO DA SHI, TO IBADU DA SAURAN FANNONAN ADDINI ZASU ZO DAGA BAYA, BADA MUHIMMANCI AKAN HAKAN DALILI NE NA DACEWA DA SHIRIYA DA YARDAR ALLAH. DA YAWA DAGA CIKIN AL`AMURA AN KULLA SU NE DA IMANI DA ALLAH DA RANAR LAHIRA, SHI KUMA IMANI DUK LOKACIN DA YA KASANCE ANA HALARTO DA SHI DA KARFI TO YANA TOSHE MA MUTUM BIN HANYAR DA AKA HANA BI.

HAKA, DAGA CIKIN ABINDA KE BAYYANA MUHIMMANCIN TARBIYYA SHI NE ABIN DA MUKE GANI DAGA WAJEN WASU IYAYE NA WOFANTAR DA KARANTARA DA YARANSU AL`AMURAN DA SUKA SHAFI IMANI DA HUJJAR CEWA YARA NE WANDA IDAN SUN GIRMA KUMA BA ZASU IYA KARANTAR DASU HAKAN BA. DUK WANDA YA WOFANTAR DA KARANTAR DA DAN SHI ABINDA ZAI AMFANE SHI YA BARSHI HAKANAN SAKAKA HAKIKA YA SABA MATUKAR SABAWA, DA YAWA DAGA CIKIN YARA LALACEWARSU TA ZO NE DAGA IYAYENSU SANADIN SAKACINSU DA RASHIN KARANTAR DASU FARILLAN ADDINI DA SUNNONIN SHI, SUKA BATA MUSU LOKACIN YARINTARSU BASU AMFANAR DA KAN SU BA KUMA BASU AMFANI IYAYEN BA BAYAN SUN GIRMA.

DAGA CIKIN MUHIMMANCIN HAKA SHI NE YAWAN SHIRYE-SHIRYEN DA AKE GABATAR DA SU GA YARA A TASHOHIN TALABIJIN DA REDIYO DA JARIDU WANDA SUKE YADA TUNANI MAI YAWA WANDA HAKAN KE GURBATA ABUBUWAN DA YARO KE SURANTAWA DA KUMA MUMMUNAR FAHIMTA AZUKATAN YARA. DAN HAKA YA ZAMA DOLE YA KASANCE AN FUSKANCI WANNAN MAS`ALAR. ITA TARBIYYAR IMANI AIKI NE DA AKA SHAR`ANTA, KUMA AIKI NE NA RIGAFIN GUJEMA AFKAWAR YARO GA MATSALOLIN TARBIYYA KAFIN YA AFKA MUSU KUMA ZAI YI MAGANIN TA IDAN TA AFKA. KUMA HAKKI NE DAGA CIKIN HAKKOKAN `YA`YA AKAN IYAYE KIYAYE HAKAN. KUMA DALILI NE NA JIN DADIN DUNIYA DA TSIRA A LAHIRA IN ALLAH YA YARDA KUMA DALILI NE DA ZAI BANBANTA MUTANE A RAYUWAR SU.

A KARSHE TARBIYYAR IMANI ITA CE NUTSUWAR RUHI DA AMINTAR DA ZUKATAN YARA DOMIN TANA BADA AMSA AKAN MANYAN TAMBAYOYI NA RAYUWA. BAKOMAI BACE FACE SHIRIYAR LITTAFIN ALLAH DA HASKAKUWA DA SUNNAR MANZONSA - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI - WANDA AKA BANBANTA SHI TA HANYAR TSARKAKEKKEN TUSHE, BAYYANANNIYAR HANYA DA SANYA ALLAH A CIKIN MANUFOFI, TARE DA SANIN BUKATUN YARO DA SANIN HAKIKANINSA DA KUMA GASKIYAR ILIMINSA. DON ISA GA KAMALA DA DAIDAITO A CIKIN HALAYEN YARON.

# MANUFOFIN
# TARBIYYAR IMANI





**BABBAR MANUFAR TARBIYYAR IMANI ITA CE TABBATAR DA GASKIYAR BAUTA GA ALLAH MADAUKAKIN SARKI. WANNAN MANUFAR NA BUKATAR TABBATAR DA MANUFOFI DABAN`DABAN MASU YAWA. DAGA CIKIN SU AKWAI:**

**NA FARKO:** DASA INGANTACCIYYAR AKIDA GA `YA`YAN MUSULMI DOMIN A SAMAR DA MUTUM NAGARI DA ZAI BAUTA MA ALLAH AKAN SHIRIYA DA HANGEN NESA.

**NA BIYU:** MUTUM YA DABI`ANTU DA DABI`U NAGARI ACIKIN AL`UMMAN MUSULMAI YANA MAI KOYI DA MANZON ALLAH ((S.A.W)) ACKIN HAKA. WANDA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YAYI SHAIDAR SHI AKAN HAKAN INDA YACE: { KUMA HAKIKA LALLAI KANA KAN HALAYEN KIRKI MANYA} [KALAM:4] DA KUMA AIKI DA FADAN SA ((S.A.W)) (( AN AIKO NI NE DAN IN CIKA DABI`U NAGARI)) [AHMAD 8939]

**NA UKU:** YADA FAHIMTAR CEWA MUSULMAI AL`UMMA DAYA CE, TA YADDA MUTUM ZAI JI CEWA SHI WANI YANKI NE NA MUSULMAI, YA DAMU DA ALAMURANSU DA DAMUWARSU, YA DANFARU DA `YAN`UWAN SHI SABODA FADAR SA MADAUKAKIN SARKI: { LALLAI MUMINAI `YAN UWA NE} [ HUJURAT: 10]. MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE: ((MUMINI DA MUMINI KAMAR GINI NE SASHINSA NA KARFAFA SASHI)) [BUKHARY; 6026]. SANNAN KUMA YA SAKE CEWA A WANI HADISIN (( ZA KA GA MUMINAI ACIKIN SOYAYYARSU DA TAUSAYINSU KAMAR JIKI NE, IDAN WATA GABA BATA DA LAFIYA SAI DUKKAN JIKIN YA KAMU DA RASHIN BACCI DA ZAZZABI.)) [BUKHARI: 6011]. DAN HAKA IYAYE DA MASU JIBINTAR LAMARIN YARO SU TABBATAR DA KULLA `YAN`UWANTAKA AKAN IMANI TA GASKIYA TSAKANIN YAYAN MUSULMAI.

**NA HUDU:** SAMAR DA MUTUM MAI DAIDAITON ZUCIYA DA TAUSAYI WANDA HAKAN ZAI TAIMAKA WAJEN SAMAR DA MUTUM MAI AMFANAR DA JAMA`AR SHI, WANDA ZAI IYA TSAYUWA DA AIKIN SHI DA AKA DORA MAI WAJEN JAGORANCI DA KUMA GINA KASA, DA KUMA IYA GUDANAR DA JAGORANCI A DORON KASA DA SAUKE NAUYE NAUYEN DA ALLAH YA SANYA SHI SHUGABA AKANSU.

DAGA NAN; BUKATAR FARAWA DA TARBIYYAR IMANI - DA MA'ANARTA TA DAIDAI - YA BAYYANA, WANDA KE CI GABA DA AIKI DON SAMAR DA ƘARFI NA RUHI, HAƁAKA BUNKASAR KAI, ƘARFAFA HANKALI, DA YADA SANIN YA-KAMATA CIKIN KALMOMI DA AYYUKA, SANNAN KUMA SAUƘAƘA WA MUTUM BAYANI DON YIN AYYUKAN DA AKE BUƘATA DON CIMMA BURIN TARBIYYAR HALAYYAR MUTUM DA NA MOTSA JIKI.

# GINSHIKAN
# TARBIYYA



**AKWAI TARIN GINSHIKAI DA GININ TARBIYYA TA DOGARA DA SU KUMA ZAMU IYA TAKAIKATA SU AKAN GINSHIKAI GUDA BIYU:**

**1- GINSHIKI NA ILIMI.**


**2- GINSHIKI NA AIKI.**

**GINSHIKI NA ILIMI YA KASU GIDA BIYU:**

**A-ILIMI B--IMANI.**

**KASHI NA FARKO:** ILIMI SHI MABUDI NE BABBA NA FAHIMTA DA GYARA DABI`U. ALLAH YACE: {KACE ASHE WADANDA SUKA SANI SUNA DAIDAITA DA WADANDA BASU SANI BA? MASU HANKALI NE KAWAI KE YIN TUNATUWA.} [ZUMAR; 9]. MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA KWADAITAR DA SAHABBAN SHI ILIMI MAI AMFANI, KUMA YA KOYAR DA SU NEMAN TSARI DAGA ILIMI MARA AMFANI. YANA CEWA ACIKIN ADDU`AR DA YA KOYAR DA SU (( YA ALLAH INA NEMAN TSARIN KA DAGA ILIMI MARA AMFANI DA ZUCIYAR DA BATA TSORON KA)) [MUSLIM: 2722]

**KASHI NA BIYU:** SHI NE ABINDA ZAI TABBATA A ZUKATAN YARA NA DAGA IMANI DA RUKUNAN MUSULUNCI GUDA SHIDA, SHI NE ABINDA YA KE ZAGAYE DA RAYUWA DA MUTUWA. MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA KWADAITAR DA DASA INGANTACCEN IMANI KUMA TSAYAYYE A ZUKATAN YARA DA SUKE A ZAMANIN SHI.



**GINSHIKI NA AIKI: SHI KUMA YA KASU GIDA UKU:**

**A- BAUTA B- AIKI C- DABI`U**

**KASHI NA FARKO:** **BAUTA;** TARBIYYA DOLE CE TA KASANCE CIKIN TSARI NA ZAHIRI, HALAYE NA MUSAMMAN, WAƊANDA YARA ZASU IYA GINUWA AKANSU, DON YA FUSKANCI RAYUWARSA DA GASKE KUMA KOYAUSHE YA ZAMA YANA DA ALAƘA DA ALLAHNSA, DON HALAYENSA DA TUNANINSA SU ZAMA MADAIDAITA, HAR MA DA FATANSA DA BURINSA, DOMIN GA ANNABI – (SA.W)- YANA CEWA MU`AZ: WALLAHI, INA KAUNAR KA, KAR KA BAR WANNAN ADDU'AR BAYAN KOWACCE SALLA, KA CE: «YA ALLAH, KA TAIMAKE NI WAJEN BAUTARKA, DA GODE MAKA, DA KUMA KYAUTATA BAUTARKA» (ABU DAWUD (1522)), KUMA YA KOYAR DA SHI CEWA IBADA FALALA CE DAGA ALLAH ZUWA GARE SHI KUMA BA WAI KAWAI KWAZON MUTUM BA NE, DACE NE NA ALLAH .HAKA KUMA KUMA A SANAR DA SHI CEWA IBADA KOYAUSHE TANA BUKATAR TAIMAKON ALLAH, DON HAKA YA SA A ZUCIYARSA CEWA IDAN MUMINI YA BAUTAWA UBANGIJINSA, DOLE NE YA NEMI TAIMAKONSA KUMA YA AMINCE DA SHI A BAUTARSA. DOMIN SHI, ALLAH TSARKI YA TABBATA A GARE SHI, SHI NE WANDA KE DATARWA WAJEN YI MASA BIYAYYA.

**KASHI NA BIYU:** **AIKATAWA:** BABU ILIMI IN BABU AIKI, AIKI SHI NE HANYAR DAUKAKA A TSAKANIN BAYI A LAHIRA, WATO SHI NE ABINDA KE SA DARAJAR WANI TAFI TA WANI A RANAR LAHIRA. ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA CE:{ WANDA YA AIKATA ALKHAIRI GWARGWADON KWAYAR ZARRA ZAI GAN SHI, HAKA WANDA YA AIKATA SHARRI GWARGWADON KWAYAR ZARRA ZAI GAN SHI} [ZALZALAT: 7-8]

**KASHI NA UKU:** **DABI`U:** ADDININ MUSULUNCI YANA GINA MUTUM NE AKAN HALAYE NAGARI, HATTA MANZON ALLAH ((S.A.W)) YANA GANIN CEWA SAKON DA YAKE ISARWA GABADAYANSA YANA TANA TATTARUWA NE AKAN ABU DAYA WANDA SHI NE KYAWAWAN DABI`U DA TARBIYYANTARWA AKAN SU. DA KAN SHI YAKE CEWA: ((AN AIKO NI NE DAN IN CIKA DABI`U NAGARI.)) [AHMAD: 8939] KUMA YANA ZABURAR DA SAHABBABSA IZUWA GA DABI`U NAGARI, IN DA YAKE CEWA ((MAFI SOYUWA DA KUMA KUSANCIN WAJEN ZAMA AGARE NI A RANAR ALKIYAMA SHI NE WANDA YA FI KU DABI`U NAGARI.)) [TIRMIZI: 2018]. DABI`U NAGARI SU NE ABINDA KE NUNAR DA TARBIYYAR IMANI A BAYYANE.

## MISALAI

# NA TARBIYYA



BUGA MISALAI A AIKACE NA DAGA CIKIN AL`AMURA MASU MUHIMMANCI DA KE TAIMAKAWA WAJEN TABBATAR DA DOKOKI DA TSARE-TSARE, DAN HAKA GA WASU MISALAI DA ZASU BAYYANA MANA YADDA MANZON ALLAH ((S.A.W)) DA SAHABBAN SHI SUKE GINA YARA AKAN IMANI.



1. DAGA IBN ABBAS ((R.A)) YA CE: MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA KASANCE YANA NEMA MA HASAN DA HUSAINI TSARI YANA CEWA: ((BABANKU YA KASANCE YANA NEMA MA ISMA`IL DA ISHAK TSARI DASU (DA WANNAN ADDU`AR): A`UZU BI KALIMATILLAHITTAMMATI MIN KULLI SHAITANIN WA HAMMATI WA MIN KULLI AINILLAMMATI)) [BUKHARY: 3371].

2. DAGA ABI HURAIRATA ((R.A)) YA CE: MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE: ((BABU WANI YARO FACE AN HAIFE SHI AKAN TURBA, SAI DAI IYAYEN SHI SU YAHUDANTAR DA SHI KO SU NASARANTAR DA SHI KO SU MAJUSANTAR DA SHI.)) [BUKHARY: 1358].

3. DAGA UMAR BIN ABI SALAMATA ((R.A)) YA CE: NA KASANCE INA KAN CINYAR MANZON ALLAH ((S.A.W)) A LOKACIN INA YARO, SAI INA TA YAWO DA HANNUNA ACIKIN KWANO (BAYA CIN GABAN SHI, YACI NAN YA CI CAN) SAI MANZON ALLAH ((S.A.W)) YACE MIN: ((YA KAI YARO, AMBACI ALLAH, KUMA KACI DA HANNUN DAMA, KUMA KA CI ABINDA KE GABANKA)) [BUKHARY: 5376, MUSLIM: 2022].



4. DAGA IBN ABBAS ((R.A)) YA CE: ((WATA RANA NA KASANCE A BAYAN MANZON ALLAH ((S.A.W)) SAI YA CE: ((YA KAI YARO, ZAN SANAR DA KAI WASU KALMOMI, KA KIYAYE ALLAH ZAI KIYAYE KA, KA KIYAYE ALLAH ZAKA SAME SHI A GABAN KA, IDAN ZAKA YI ROKO TO KA ROKI ALLAH, KUMA IDAN ZAKA NEMA TAIMAKO TO KA NEMI TAIMAKO WAJEN ALLAH, KUMA KA SANI CEWA LALLAI DA ACE AL`UMMA ZASU TARU DAN SU AMFANAR DA KAI AKAN WANI ABU, TO, BA ZASU AMFANE KA DA KOMAI BA FACE ABINDA ALLAH YA RUBUTA MAKA….)) [TIRMIZIY: 2156]

5. DAGA ALHASAN BIN ALIYU ((R.A)) YA CE: MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA KOYA MIN WASU KALMOMI DA ZAN FADA ACIKIN KUNUTI NA SALLAR WITIRI: ((ALLAHUMMAH DINI FI MAN HADAITA, WA AFINI FI MAN AFAITA WA TAWALLANI FI MAN TAWALLAIT WA BARIK LI FI MA A`ATAITA WA KINI SHARRA MA KADAIT, INNAKA TAKDI WA LA YUKDA ALAIKA INNAHU LA YAZILLU MAN WALAITA, TABARAKTA RABBANA WA TA`ALAITA.)) [ABU-DAWUD: 1425]

6. DAGA ANAS ((R.A)) YA CE: MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE MIN: (( YA DANA, IDAN ZAKA SHIGA WAJEN IYALAN KA KA YI SALLAMA, DOMIN HAKAN ZAI KASANCE ALBARKA A GAREKA TARE DA IYALAN KA)) [TIRMIZI: 2698]


7. DAGA JUNDUB AL-BAJALIYYU ((R.A)) YA CE: MUN KASANCE TARE DA MANZON ALLAH ((S.A.W)) A LOKACIN MUNA YARA, SAI MUKA KOYI IMANI KAFIN MU KOYI ALKUR`ANI, SANNAN SAI MUKA ZO MUKA KOYI ALKUR`ANI SAI MUKA KARA IMANI DA SHI (SABODA QUR`ANI) [IBN MAJAH (61)]

8. UMMU SULAIM WATO RUNAISA`U MAHAIFIYAR ANAS BN MALIK (R.A) TA MUSULUNTA A LOKACIN ANAS YANA YARO BA`A YAYE SHI BA, SAI TA RINKA LAKKANA MA ANAS TANA CE MAI KACE: LAI`ILAHA ILLALLAH, KACE: ASH`HADU ANNA MUHAMMAN RASULULLAHI. SAI ANAS YA FADI HAKAN

9. DAGA IBRAHIM ATTAIMIYYU ALLAH YA YI MASA RAHAMA, YA CE: SUN KASANCE SUNA SON YA ZAMA FARKON ABINDA YARO ZAI FARA FADA SHI NE LA`ILAHA ILLALLAH SAU BAKWAI, SAI YA KASANCE SHI NE FARKON ABINDA YA FARA MAGANA DA SHI.



# TARBIYYAR IMANI GA YARO





DAGA CIKIN MAUDU`AI MASU MUHIMMANCI A FANNIN TARBIYYA SHI NE TARBIYYAR DASA IMANI A ZUCIYAR YARO DOMIN TANA SANYA DABI`U NAGARI TA KUMA TABBATAR DA SU, TA KUMA DASA INGANTACCIYAR AKIDA A CIKIN TUNANI DA ZUCIYAR YARO. YA KUMA NUSASSHE DA YARO ZUWA DA HALAYYA TAGARI DA AIKATA WANNAN HALAYYAR A DUKKAN AYYUKAN SHI. ACIKIN WANNAN MATAKIN SHEKARUN, YARO ZAI GINA HANGEN SHI GA YANAYIN YADDA DUNIYA KE TAFIYA, DAGA FAHIMTAR HAKA NE ZAI SAN YADDA ZAI GINA DABI`UN SHI DA MU`AMALAR SHI DA MUTANE, DAGA CIMMA WANNAN MANUFAR NE ZAI SAMU JIN DADIN DUNIYA YA KUMA TSIRA A LAHIRAR SHI, WANNAN NAUYIN NA ABUBUWAN DA AKA AMBATA YANA KAN IYAYE NE, TUN TARBIYYAR SHI NA KARKASHINSU NE, SU ZASU DORA SHI KAN HANYA DA ZAI CIMMA WANNAN MANUFAR HAR YA ZAMA MUTUM NAGARI. ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA CE: {ALLAH YANA YI MUKU WASIYYA GAME DA `YA`YANKU} [ANNISA: 11]. MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA BAYYANA HAKAN INDA YACE: (( BABU WANI YARO FACE AN HAIFE SHI AKAN TURBA SAI DAI IYAYEN SHI SU YAHUDANTAR DA SHI KO SU NASARANTAR DA SHI KO SU MAJUSANTAR DA SHI.)) [BUKHARY: 1359]. HADISIN YANA NUNI AKAN AL`AMURA MASU YAWA, DAGA CIKIN SU:

1. IMANI FIDRA CE TA MUTUM KUMA WANDA YA CANZA MAI SHI YA CANZA MISHI SABODA MATSALA DAGA CIKIN MATSALOLIN `YAN ADAM.
2. HADISIN YA BAYYANA NAUYIN DAKE KAN IYAYE DA KUMA MATSAYINSU MAI GIRMA ACIKIN TARBIYYA.
3. YA YI NUNI IZUWA TASIRIN INDA MUTUM KE RAYUWA ACIKIN TARBIYYA.

DAGA CIKIN FALALAR ALLAH AKAN MUTUM SHI NE TSARKAKE ZUCIYAR SHI TUN FARKON RAYUWAR SHI GA IMANI BA TARE DA BUKATAR WATA HUJJA DA DALILI BA, MA`ANA TUN KAFIN YA SAN CIWON KAN SHI. DA WANNAN SAI MU CE IYAYE YA KAMATA SU TSAYU AKAN KARIYA TA HANYAR DASA MAI AKIDA INGANTACCIYA DA GASKIYAR TSAYUWA, SU KUMA TSARKAKE TURBAR DA TUN ASALI AKANTA KOWA YAKE, SU TARBIYYANTAR DA `YA`YANSU AKAN INGANTACCEN ADDINI DA ALKUR`ANI DA SUNNAH SUKA ZO DA SHI. KUMA KADA SUYI KASALA WAJEN TARBIYYANTAR DA WAJEN DA SUKE ZAUNE WANDA FAHIMTAR YARO KE DOGARO DA IRIN FAHIMTAR YANAYIN WAJEN.

TSARKAKAKKIYAR ZUCIYAR YARO ITA CE ZINARIYAR DA BABU KOWANE IRIN ZANE DA HOTO A KANTA, KUMA TA DACE DA KOWANE IRIN ZANE, DOMIN SABAWA DA ALHERI DA SANINSA YA GIRMA AKANSHI KUMA YAYI FARIN CIKI DUNIYA DA LAHIRA, IYAYENSA DA MALAMANSA KUMA SU YI TARAYYAR LADAN KOWANE MALAMI DA LADABI TARE DA SHI A CIKIN LADANSA, KUMA SABAWA DA SHARRI DA WATSI DA GAFALA IRIN TA DABBOBI YA HALAKA SU, KUMA NAUYIN YA KASANCE A WUYAN MAI KULA DA LAMARINSA; DOMIN GYARA MAFI KYAU NA KASANCEWA NE TUN MUTUM NA ƘARAMI, AMMA IDAN AKA BAR YARON, AKA SANGARCE, CI GABA A HAKA, GYARA SHI NA DA WUYA.

YARON DA YA GIRMA A CIKIN DANGI MASU IMANI MAI ƘARFI YANA HIMMATUWA DA KOYARWAR MUSULUNCI DAIDAI, YANA KUMA YIN KOYI DA IYAYENSA A CIKIN KOMAI, KUMA YANA SAMAR DA NASA RA'AYOYIN TA MAHANGAR IYAYENSA, DON HAKA MUKE GANIN WAƊANDA SUKE GABATAR DA KA'IDOJIN SHARI'A CIKIN TSANANTAWA DA TSATTSAURAN YANAYI WANDA KE HAIFAR DA MUMMUNAN SAKAMAKO GA YARA, KAMAR YADDA YARO IDAN YA GIRMA YA SAMI IYAYENSA BA SU DA KOYARWAR MUSULUNCI; YANA DA WAHALA A GARE SHI YA SAMI SHA'AWAR ADDINI A NAN GABA. DOMIN LOKACIN DA YAKE KARAMI BAI GA ALAMAR ADDINI BA, DON HAKA BAI DA WATA FAHIMTA GAME DA ADDINI.



## BUNKASA

# ADDINI GA YARO



ADDINI YANA FARAWA NE AWAJEN YARO DA TUNANI GUDA DAYA, SHI NE TUNANIN SAMUWAR ALLAH, DAGA NAN SAI WASU TUNANUKA TA WANI GEFEN SU FARA BAYYANAR MAI KAMAR TUNANIN HALITTA DA LAHIRA DA MALA'IKA DA SHAIDANU. KUMA ANA BANBANCE TUNANIN BUNKASAR ADDININ YARO A ABUBUWA GUDA HUDU:

**A ABINDA KE FARUWA:**

ANAN FAHIMTAR YARO GAME DA ADDINI ZATA KARKATA NE GA ABINDA KE FARUWA YAKE KUMA IYA GANI KO TABAWA, YANA KARA GIRMA TUNANIN SHI NA KARUWA KADAN-KADAN HAR YA KAI GA GANO GASKIYA, YA SANYA TA A INDA YAKE GANIN TA DACE A LOKACIN DA YA KAI SHEKARUN BALAGA.

## B SURANTAWA:

ANAN YARO ZAI RINKA KWAIKWAYON YADDA MANYA KE IBADUNSU DA ADDU'O'INSU BABTARE DA YA SAN MA'ANARSU KO YA SAN GIRMANSU A ZUCIYA BA, SHIYA SA YA KAMATA GA MAI TARBIYYA YA SAN ABINDA YARO YAFI KARKATA AKAN SHI AWANNAN SHEKARUN NA YARINTA DAN YA KOYAR DA SHI RUKUNAN MUSULUNCI DA DABI'UN SHI DA RUKANAN IMANI DA TASIRIN SHI GA MUTUM.

## C AMFANI.

YARO ZAI FAHIMCI FARIN-CIKIN IYAYEN SHI DA MALAMAN SHI DA WADANDA KE KEWAYE DA SHI SABODA ABINDA YAKE AIKATAWA NA WASU IBADU, SAI YA RINGA AIKATA HAKAN DAN SAMUN SOYAYYARSU DA KUMA CIMMA MANUFAR WASU DAGA CIKIN ABUBUWAN AMFANUWAR SHI KO DAN TUNKUDE WATA CUTARWA DA KA IYA SAMUN SHI.

## D TSATTSAURAN RA'AYI:

HAKAN NA KASANCEWA NE A LOKACIN DA YARO YA ZAMA MAI TSATTSAURAN RA`AYI GAME DA ADDININSA YANA MAI SHA'AWAR HAKAN TA HANYAR JINGINUWA GA ADDININ DA KUMA JINGINUWA ZUWA GA ALLAH - MADAUKAKI.

DAGA ABINDA YA GABATA ZAMU FAHIMCI MUHIMMANCIN MAI DA HANKALI AKAN TARBIYYAR DASA IMANI, DA KUMA CEWA WAJIBI NE AKAN IYAYE DA MASU TARBIYYA SU MAI DA HANKALI WAJEN KUSANTO DA IMANI A ZUCIYAR YARO MUSAMMAN MA A WANNAN ZAMANIN DA FITINTINU SUKA YI YAWA DA JUYA ABUBUWA DA SHAGALA DA SAUYE-SAUYE. DAGA CIKIN AL'AMURA DA YA KAMATA ACE SUN AIKATA SU SUNE:

1- TABBATAR DA FIDIRA A ZUCIYAR YARO WANDA SHI NE KOYA MA YARO KALMAR TAUHIDI.

2- TABBATAR DA IMANI TA HANYAR SANAR DA SU RUKUNAN IMANI GUDA SHIDA, WANDA HAKAN ZAI TAIMAKAWA WAJEN SON ALLAH MADAUKAKIN SARKI DA SON MANZON ALLAH ((S.A.W)) DA KOYAR DA ALKUR'ANI.

SAMUWAR FIDIRA TA ADDINI DA TAKE BOYE A ZUKATA NA DAGA CIKIN ABIN DA KE TAIMAKAWA IYAYE WAJEN TSAYUWA AKAN ABINDA YA KAMACE SU A TARBIYYA, FIDIRA TANA NUNI ZUWA GA SHA'AWA TA ADDINI. KUMA ITA WANNAN SHA'AWAR KAMAR IRIN SAURAN SHA'AWOWI NE DA BA ZA'A IYA CANZA SU BA, SAI DAI CI GABA DA FADAKARWA DA SAMUN CI GABA AKAN HAKAN. KUMA ANA IYA AMFANI DA WANNAN FIDIRAR TA FUSKOKI DABAN-DABAN BANDA FUSKAR DA AKA HALICCI MUTUM ASALI DOMIN TA. SHI KO ADDININ MUSULUNCI YANA KIRA NE ZUWA GA DORA MUTUM AKAN FIDIRAR DA AKA HALICCE SHI SABODA ITA.

DAGA CIKIN MUHIMMAN ABUBUWAN DA YA KAMATA A RAINI DAN MUSULMI AKAN SU NE RUKUNAN MUSULUNCI GUDA SHIDA, KUMA MAFI MUHIMMANCI ACIKINSU DA YA KAMATA A KARANTAR DA SHI SHI NE IMANI DA ALLAH, IMANI DA ALLAH DA SON ALLAH SHI NE ZAI SA YAYI SAURIN FAHIMTAR SAURAN RUKUNAN IDAN YA ZO KANSU. ALLAH ((S.W.T)) YA SANYA SOYAYYAR SHI YA ZAMA MAFI GIRMAN SHARUDDAN IMANI DA KUMA KANKAN DA KAI GA ALLAH. MA'ANA SON SHI WAJIBI NE WAJEN YI MAI BIYAYYA DA KUMA ADAWA DA MAKIYAN SHI, WATO SAI KA SO SHI KAFIN KA YI MAI BIYAYYA KUMA KAKI MAKIYAN SHI. KUMA YA WAJABTAR DA WANNAN SON NA SHI YA ZAMA YAFI NA KOWA ACIKIN DUNIYA. ALLAH MADAUKAKIN SARKI YANA CEWA: { KA CE IDAN UBANNIN KU DA 'YA'YAN KU DA 'YAN`UWANKU DA MATAN KU DA DANGIN KU DA DUKIYOYI, WADANDA KUKA YI TSIWIRWIRIN SU DA FATAUCI WANDA KUKE TSORON TASGARONSA DA GIDAJE WADANDA KUKE YARDA DA SU , SUN KASANCE MAFIYA SOYUWA AGARE KU DAGA ALLAH DA MANZON SA , DA YIN JIHADI GA HANYAR SA, TO, KUYI JIRA HAR ALLAH YA ZO DA UMURNIN SA. KUMA ALLAH BA YA SHIRYAR DA MUTANE FASIKAI.} [TAUBAH: 24]. KUMA SAI YA SANYA SIFFAN FARKO TA BAYIN DA YA YARDA DA SU TA ZAMA SON SHI. YA CE: {YA KU WADANDA SUKA YI IMANI, WANDA YAYI RIDDA DAGA CIKIN KU DAGA ADDININ SA TO, ALLAH ZAI ZO DA WASU MUTANE, YANA SON SU KUMA SUMA SUNA SON SHI, MASU TAWALU'I AKAN MUMINAI MASU IZZA AKAN KAFIRAI, SUNA YIN JIHADI ACIKIN HANYAR ALLAH KUMA BA SA TSORON ZARGIN WANI MAI ZARGI, WACCAN FALALAR ALLAH CE, YANA BAYAR DA ITA GA WANDA YAKE SO, KUMA ALLAH MAYALWACI NE MAI ILIMI.} [MA'IDAH: 54]. YA KUMA BAYYANA CEWA TSARKAKAKKEN TAUHIDI BAYA KASANCEWA FACE SAI DA KADAITA ALLAH DA TSANTSAR SOYAYYA YA CE: {DAGA CIKIN MUTANE AKWAI WADANDA SUKA RIKE WANIN ALLAH KISHIYA SUNA SON SHI KAMAR YADDA SUKE SON ALLAH, WADANDA SUKA YI IMANI SUNA TSANANIN SON ALLAH} [AL-BAKARAT: 165]. KUMA IBADAR DA ALLAH YA HALICCE MU DOMIN TA ITA CE MAFI GIRMA A MATAKAN SOYAYYA, ASALIN TAUHEEDI SHI NE TSARKAKE SOYAYYA GA ALLAH SHI KADAI, SHI NE ASALIN KADAITAWA, SHI NE MA HAKIKANIN BAUTA, KUMA TAUHIDI BAYA CIKA HAR SAI SON BAWA GA UBANGIJINSA YA CIKA KUMA YAFI DUKKAN WANI ABU DA YAKE SO YA KUMA RINJAYE SHI. SAI YA KASANCE DA SHI ZA A YI HUKUNCI, TA YADDA SAURAN ABUBUWA DA YAKE SO DUK SUNA BAYAN SON DA YAKE MA ALLAH NE WANDA SHI NE JIN DADIN MUTUM DA KUMA TSIRAN SHI A LAHIRA.

KUMA WANNAN SOYAYYAR DA AKA GINA TA AKAN IMANI NA DAGA CIKIN MANYAN HANYOYIN KARFAFA DABI'UN YARA DA TABBATAR DA SU AKAN ADDININ MUSULUNCI DA KUMA BIYAYYA GA ALLAH DA MANZON SHI ((S.A.W)), DUK WANDA AKA DASA SON ALLAH DA MANZON SA ACIKIN ZUCIYAR SHI HAKIKA YAFI KASANCEWA TSAYAYYE A AKIDAR SHI DA IBADAR SHI DA DABI'UN SHI, KUMA DUK YADDA ZA A JUYAR DA WASU MAS'ALALOLI KO WANI YANKI NA ADDINI KO GAFALA TA ZO MISHI KO

MANTUWA, SOYAYAYYAR NAN DAKE CIKIN ZUCIYAR SHI TA ALLAH DA MANZON SHI SAI SUN DAWO DA SHI KAN HANYAR DAIDAI DA YARDAR ALLAH TA'ALA, SABODA AKWAI SOYAYYA TA CIKI, BA WAI TA WAJE KADAI BA.

MAHANGAR DA AKIDAR MUSULUNCI TAKE BAYARWA GA RAYUWA TAYI FICE KASANCEWARTA TA DACE DA ASALIN HALITTAR DAN ADAM DA KUMA YADDA DABI'AR SHI TAKE, KUMA TANA TAFIYA KAFADA DA KAFADA DA LAFIYAYYEN HANKALI KUMA BABU CIN KARO A TSAKANINSU, KAMAR YADDA TAYI FICE DA WASU ABUBUWA KYAWAWA WADANDA BA A SAMUN SU A WATA AKIDA DOMIN KUWA TSARI NA TUNANI DA NA AKIDA DA NAGARTA DA SHARI'A SUN CIKA ACIKIN TA, IDAN KA KALLE TA ZAKA GA CEWA TSARI NE NA TUNANI DA AKIDA ZATA BAKA FASSARAR ASALIN SAMUWAR HALITTU DA MAKOMARSU DA HAKIKANIN ABUBUWAN DA KE CIKIN SU DA ABINDA ZA SU ZO BAYA, WATO BAYAN MUTUWA, TO, AKIDAR MUSULUNCI ITA KE BAKA AINIHIN BAYANI CIKAKKE DA HANKALI ZAI DAUKA KUMA TUNANI ZAI DAUKA BA TARE DA AN SAMU CIN KARO BA, SABANIN SAURAN AKIDU, KUMA TANA BAYYANA FARKON RAYUWAR MUTUM DA KARSHEN SHI, SANNAN YANA IYAKANCE FA'IDAR ABINDA YA SA AKA HALICCI MUTUM SABODA SHI, DA KUMA FA'IDA WACCA TASA AKA HALICCI MUTUM DAN A CIMMA MANUFAR TA, SHIYASA AMSA TAMBAYOYIN MUTUM AKAN RAYUWA WACCA BABU MAKAWA DOLE SAI MUTUM YAYI TAMBAYA AKAN SU SABODA YANAYIN DABI'A TA HANKALI WANDA IN MUTUM BE SAMU AMSAR SU GAMSASSU BA BA ZAI SAMU NATSUWA BA, IN KO BA HAKA BA ZAI RAYU NE CIKIN RUDANI DA DAMUWA AKODA YAUSHE SABODA BAI SAN MEYE MA'ANAR RAYUWAR DA YAKE ACIKI BA.



## FA'IDAR

# TARBIYYAR IMANI



AKWAI TARIN FA'IDAJI WADANDA MAI TARBIYYA ZAI IYA TATTARA SU AKAN TARBIYYAR IMANI. DAGA CIKINSU AKWAI:

1 GAGGAWA WAJEN AIKATA ALKHAIRAI, YA DUBA DUK WATA KAFA TA AIKI DA ZATA KUSANTAR DA SHI ZUWA GA YARDAR ALLAH DA KUMA RAHAMAR SHI.

2 KARFAFA DUK WANI ABU DA ZAI HANA SHI AIKATA MUMMUNAN ABU, INGANTACCEN IMANI SHI KE DAIDAITA DABI'UN MUTUM.

3 GUDUN DUNIYA, KADA ZUCIYAR SHI TA ZAMA TA DANFARU DA SON DUNIYA HAR YA ZAMA SHI DAI KULLUN BURIN SHI YA ZAI SAMU DUNIYA.

4 DACEWA DA ABINDA ALLAH KE SO, ALLAH SUBHANAHU WA TA'ALA ZAI RINKA JIBINTAR LAMARIN BAWAN SHI MUMINI, TA YANDA ZAI JANYO MAI MASLAHA DA KUMA JIN DADIN DUNIYA DA LAHIRA.

5 KWADAITARWA ZUWA GA ALLAH, DUK SANDA IMANI YA KARU, TO BAWA ZAI KARA YARDA DA UBANGIJIN SHI DA KWADAITA ZUWA GARE SHI DA JUYA BAYA GA BARIN HALITTAR SHI.


6 BOYE ABUBUWA DA SUKE MARASA KYAU DA KUMA RAGE MATSALOLI TSAKANIN MUTANE, ADUK LOKACIN DA IMANI YA KARU A ZUCIYA, TASIRIN SON ZUCIYA ZAI RAGU AKAN TA, TA KAI MUTUM ZUWA GA DABI'U NAGARI MADAUKAKA.

7 TASIRI NA KWARAI A ZUKATAN MUTANE; MUMININ KWARAI NA KOKARIN GYARA KANSA NE DA KUMA WADANDA KE KEWAYE DA SHI.

8 JIN NUTSUWA DA KWANCIYAR HANKALI; GWARGWADON YADDA WANNAN IMANI YA TABBATA A ZUCIYAR BAWA, GWARGWADON YADDA TSORON DA KE FIRGITA MUTANE ZAI GUSHE DAGA GARE SHI.

## BATUTUWAN

# TARBIYYAR IMANI



ABINDA YAKE WAJIBI AKAN IYAYE SHI NE SU KOYA MA 'YA'YAN SU ABINDA ZAI KARFAFA IMANINSU, KUMA YA KYAUTATA DABI'UNSU, KUMA YA KARFAFA MISHI JIN JINGINUWA ZUWA GA AL'UMMAR ANNABI MUHAMMAD ((S.A.W)). DAGA CIKIN ABINDA KE KARKASHIN HAKA SHINE:

1. KOYAR DA RUKANAN IMANI GUDA SHIDA, IMANI A DUNKULE WANDA YA DACE DA SHARI'AH DA DABI'AR MUTUM, TARE DA NISANTAR AIKATA ABU A AIKACE AGABAN YARO WANDA ZAI SA YA RASA IMANI, DA KOKARIN AIKATA AIKIN DA ZAI FARKAR DA ZUKATA YA SAITA KWAKWALWA YA KUMA INGANTA DABI'U.
2. TARBIYYANTAR DA YARA AKAN SON MANZON ALLAH ((S.A.W)) DA SON IYALANSA DA MATAN SHI DA SAHABBAN SHI BAKI DAYA BA TARE DA WUCE GONA DA IRI.
3. KOYAR DA YARA GIRMAMA ADDINI DA ABUWAN DA YA SHAR'ANTA DA KUMA TSORATAR DA SU AKAN YIN IZGILANCI DA SHI DA RASHIN DAMUWA DA SHI.
4. KARANTAR DA SU CEWA CIKAKKEN IMANI BAYA KASANCEWA SAI DA AYYUKA NAGARI DA KUMA CEWA IMANI YANA KARUWA DA AIYUKA NAGARI KUMA YANA RAGUWA SANADIN AIKATA ZUNUBAI. TARBIYYAR DASA INGANTACCEN IMANI DOLE CE, HAR DADIN TA YA ZO ACIKIN DABI'U NAGARI DA IBADA.
5. TABBATAR DA IMANI DA RANAR ALKIYAMA A ZUKATAN SU DA GIRMAN RANAR, DA KUMA SAKAMAKO MAI KYAU KO MARA KYAU DA BAWA ZAI SAMU TA DALILIN AIYUKAN SHI A DUNIYA, WANDA YA KYAUTATA YA SAMU ALJANNAH, WANDA KUMA YA MUNANA YA SHIGA WUTA.



6. TABBATAR DA CEWA SUNA KIYAYE ALLAH ACIKIN IDADUNSU, SU SAN CEWA YANA GANIN SU YANA KUMA JIN SU, KUMA BA ABINDA KE BOYUWA AGARE SHI, YANA GANIN KOMAI DA KOWA. YA SAN KOMAI DA KOWA.

7. ZURFAFA MAI JIN CEWA YANA KAN GASKIYA, WANNAN ZAI SA YA RIKE ADDININ SHI DA KARFIN GASKE.



## HANYOYIN DASA

# TARBIYYAR IMANI

ZAMU IYA KASA WADANNAN HANYOYIN ZUWA GIDA BIYU:

1- SHEKARUN KAFIN WAYO GA YARO.

2- SHEKARUN BAYAN WAYO GA YARO.

**DAGA CIKIN ABUBUWANDA SUKE TAIMAKAWA WAJAN KARFAFA IMANI KAFIN SHEKARUN FAHIMTA:**

1. YIN BAYANI AKAN SUNAYE NA BAUTA DA YA SABA JIN SU KAMAR: ABDULLAHI, ABDUR-RAHMAN, ABDUL-KARIM, DA KOKARIN BAYYANA DUKKAN MA'ANONIN SU (SUNAYEN) A DUNKULE, DA BADA MUHIMMANCI WAJEN JIYAR DA SHI KIRAN SALLAH, DA KOYAR DA SHI ZIKIRAN YAU DA KULLUM, DA ADDU'O'I DA KIYAYE SU DA AMBATONSU A GABAN SHI, DA TUNATAR DA SHI NI'IMOMIN ALLAH A GARE SHI, MUSAMMAN LOKACIN CIN ABINCI; DA MAIMAITA SHI DA KOYAR DA SHI BASMALA A FARKON CIN ABINCI DA HAMDALA A KARSHEN CIN ABINCIN.
2. HADDATAR DA SHI WASU DAGA SURORIN AL-QUR'AN, TARE DA FAHIMTAR DA SHI CEWA MAGANAR ALLAH TA'ALA CE. KUMA FARKON ABINDA ZA A FARA KOYA MAI SHI NE ; SURATUL FATIHA, IKHLAAS DA QUL'A'UZAI. HAKA ZA'A IYA A HADDATAR DA SHI WASU ƘASIDU DA WAƘOƘIN DA YA KAMATA A KOYAR DA YARA SU NA DAGA ABINDA KE NUNI AKAN MA'ANONIN INGANTACCEN IMANI.
3. A KULA DA AMBATON SUNAN ALLAH GA YARO TA HANYAR ABUBUWAN DA AKE SO DA SUKE FARANTA RAI. YA KUMA WAJABA KAR A GWAMA AMBATON ALLAH TA'ALA DA ƘEKASHEWA DA AZABTARWA A SHEKARUN YARINTA, KAR A YAWAITA MAGANA AKAN FUSHIN ALLAH DA AZABAR SHI DA WUTAR SHI (GA YARO).
4. FUSKANTAR DA YARO AKAN KYAWUN DAKE CIKIN HALITTA, DA KARFIN IKO DA HIKIMAR ALAKAR DA KE TATTARE DA HAKAN, DAN YA JI GIRMAN MAHALICCI DA IKON SHI, YA KUMA SO ALLAH TA'ALA; DOMIN SHI ALLAH NA SON SHI, KUMA YA DAUKAKA SHI SAMA DA SAURAN HALITTU.

**5.** HORAR DA YARO AKAN LADUBBAN DABI’U, DA SABAR MASA DA JIN KAI, DA TAIMAKON JUNA, DA LADUBBAN MAGANA DA SAURARO YAYIN DA YAKE TATTAUNAWA DA WANI, DA DASA MAI DABI’UN MUSULUNCI TA HANYAR HALAYE NAGARI, LAMARIN DA ZAI SANYA SHI RAYUWA CIKIN YANAYIN DAUKAKA, DA KOYON DUKKAN ALKAHIRAI DAGA WADANDA KE KEWAYE DA SHI.



AMMA BAYAN SHEKARUN DA YARO KE IYA TANTANCE ABUBUWA, SAI A KARA DA WADANNAN HANYOYIN TARE DA LURA DA SANYA TUNANI. HANYOYIN SU NE:

1. SANAR DA YARO GIRMAN WANNAN DUNIYAR DA KYAWUN HALITTUNTA DA KYAUTATUWARTA, ZA A YI HAKAN NE DAN MUTUM YA GIRMAMA UBANGIJIN SHI YA KUMA DAUKAKA SHI. ALLAH TA'ALA YA CE: {HALITTAR ALLAH WANDA YA KYAUTATA KOWANE ABU.} [NAML: 88]

2. TUNASAR DA SHI HIKIMAR ALLAH TA'ALA ACIKIN AYYUKAN SHI DA HALITTUN SHI, ZA A TUNASAR DA SHI HAKAN NE DOMIN YA SO ALLAH YA KUMA GODE MAI, KAMAR HIKIMAR DA KE CIKIN HALITTAR DARE DA YINI, DA RANA DA WATA DA HIKIMAR HALITTAR GABBAN JI, (GUDA BIYAR) KAMAR JI DA GANI DA HARSHE DA SAURAN SU. ALLAH TA'ALA YA CE: {SHIN BA ZASU YI TUNANI ACIKIN ZUKATAN SU CEWA ALLAH BAI HALICCI SAMMAI DA KASSAI DA ABINDA KE TSAKANIN SU BA FACE DA GASKIYA.}[RUM: 8]

3. FA'IDANTUWA DA DAMAR DA AKA SAMU DON NUSASSHE DA YARO ABUBUWAN DA KE FARUWA TA HANYAR HIKMA DA ZAI SA SHI YASO AIKIN ALKHAIRI YA KUMA GUJE MA SHARRI. MISALI: IDAN YAYI RASHIN LAFIYA ZUCIYAR SHI TA DANFARU DA ALLAH, MU KOYA MAI ADDU'A DAN SAMUN WARAKA, MU KOYA MISHI KYAUTATA ZATO GA ALLAH. IDAN MUKA BASHI ALAWA KO KAYAN MARMARI DA YAKE SO TO, A NEMI YA GODE MA ALLAH DAGA WANNAN NI'IMAR KUMA MU FADA MISHI WANNAN KYAUTAR ALLAH NE YA BASHI, KUMA IYAYE SU GUJI KOYA MA YARO ABUBUWAN IMANI LOKACIN DA YAKE CIKIN HALI MARA DADI DOMIN BAI DA WAYON DA ZAI IYA BANBANCE TSAKANIN HAKAN.

4. DOLE MAI TARBIYYA YA ZAMANA YANA YAWAN AIKATA ABUBUWAN NA ADDINI DOMIN YARO YA GANI YA SABA DA AIKATA SU SHIMA, SHIYASA AKE SON MAI TARBIYYA YA ZAMA MAI DABI'U NAGARI DAN YARO YAYI KOYI DA SHI, ZAMA MUTUM MAI ADDINI GAMI DA DABI'U NAGARI NA DAGA CIKIN ABUBUWAN DA KE SANYA TARBIYYAR MU TA ZAMA TARBIYYA TA GASKIYA BA WAI A BAKI BA KAWAI

5. FA'IDANTUWA DAGA KISSOSHI MASU FA'IDA DA ZASU SA YARO YA GANE ABINDA AKE SO DA NISANTAR WANDA BA A SO, KUMA ANA IYA GABATAR DA KISSAR TA HANYAR WASAN KWAIKWAIYO TARE DA BAYYANA SAKON DA KISSAR KE ISARWA. HAKA ANA IYA BADA KISSAR TA HANYAR WAKA WADDA ITAMA TANA TAIMAKAWA WAJEN GYARA DABI'UN YARO. KUMA ANA IYA SA YARO YA SAN WAYE

ANNABI ((S.A.W)) TA HANYAR BA SHI TARIHIN SHI ((S.A.W)) DOMIN YA SO SHI YA KUMA YI MAI BIYAYYA MUSAMMAN ABINDA YA KEBANCI YARINTAR SHI DA ABUBUWAN DA SUKA FARU TSAKANIN SHI DA YARA NA KYAUTATA MU'AMALA A GARE SU DA TAUSAYIN SHI AGARE SU, DA SIFFANTA YANAYIN SHI DON HAKA ANA IYA BASHI TARIHIN SAHABBAI DA MATAN MUMINAI DA MUTANEN GIDAN MANZON ALLAH ((S.A.W)) BAKI DAYA.

6. DAIDAITUWA AKAN TARBIYYANTAR DA YARA AKAN ADDINI DA RASHIN DORA MUSU ABINDA BA ZASU IYA BA. KADA MU MANTA WASANNI SU NE DUNIYAR YARO TA ASALI, KADA MU DANKWAFAR DA SHI GA ABINDA ZAI HANA SHI CI GABAN DABI'UN SHI DA GYARAN ZUCIYAR SHI TA HANYAR DORA MAI NAUYIN BIN ABINDA BA ZAI IYA BA DA YAWAITA JAN SHI AKAN ABUNHWAN DA ZASU HARAMTA MAI JIN DADIN YARINTAR SHI, DOMIN WUCE GONA DA IRI AKAN HAKA YANA IYA JAWO SHARRUKA DA SANYA SHI YAJI YA CIKA AIKATA LAIFI. SO DA DAMA AN FI SAMUN HAKA AKAN DAN FARI (YARON DA AKA FARA HAIFA AGIDA) SABODA IYAYE GALIBI SUNA SON YA ZAMA ABIN MISALI GA 'YAN BAYA SAI SU TAKURA SHI BA SU SAN SUN TAKURA SHI BA.



7. YANA DA KYAU ARINKA BARIN YARO AKAN DABI'UN SHI BA TARE DA MANYA SUNA MAI SHISSHIGI AKODA YAUSHE BA SABODA YAJI DADIN BINCIKO WASANNI DA KAN SHI GWARGWADON WAYON SHI DA HANGEN SHI GA IRIN WURIN DA YAKE RAYUWA. ZA A BAR SHI AKAN HAKAN NE SABODA YARO NA SON BAYYANA ABINDA KE TARE DA SHI DA KUMA TSAYUWA AKAN KAYAN SHI.

8. KARFAFA MA YARO GUIWA YANA TASIRI A ZUCIYAR SHI TASIRI MAI KYAU, KUMA YANA KWADAITAR DA SHI WAJEN DAGEWA YA AIKATA ABINDA AKE SO YA AIKATA, KUMA IDAN TARBIYYAR YARO TA KASANCE ANA YIN TA NE TA HANYAR NUNA KAUNA DA KYAUTATAWA, TO, HAKAN ZAI KAI GA SA ASAMU HALAYYA TAGARI SOSAI AWAJEN YARON. KUMA DOLE A TAIMAKAMA YARO WAJEN SANIN HAKKOKIN SHI, YA SAN ME YA KAMATA A YI MAI ME KUMA SHI YA KAMATA YA YI, YA KUMA SAN MEYE DAIDAI DA WANDA BA DAIDAI BANE A AIKATA SHI, TARE DA SANYA SHI YA SAN MATSAYIN SHI DA GIRMAN SHI, A DAIDAITA SHI AGUJI SHAGWABA SHI.

9. DASA AKIDAR MUTUNTA ALKUR'ANI DA TABBATAR DA SHI A ZUCIYAR YARO, DAN YA JI GIRMAN TSARKAKAR SHI DA KUMA BIN UMURNIN ABINDA ALKUR'ANIN YA ZO DA SHI, ZA A YI HAKAN NE TA HANYA MAI JANYO HANKALI, YARO YA SAN CEWA IN DAI YA KYAUTATA TILAWAR ALKUR'ANI TO ZAI SAMI GIRMAN DARAJAR MALA'IKU KUBUTATTU. SANNAN YA KULA DA LADUBBAN TILAWA TUN DAGA FARAWA DA ISTI'AZA DA BASMALA DA GIRMAMA QUR'ANIN DA KYAUTATA SAURARON SHI. MU KUMA SABAWA YARO DA SAURARON AYOYIN ALKUR'ANI DOMIN WANNAN ZAI KARA MAI KARFIN LARABCI DA KUMA KARFAFA AKAN KARATUN QUR'ANI. KUMA ZA A IYA KOYA MAI TAFSIRIN WASU AYOYI DA SUKA SHAFI MA'ANONA NA AKIDA DAGA CIKIN SURORIN DA YAKE HADDACEWA KAMAR SURATUL FATIHA, IKHLAS, FALAK, NAS DA SAURAN SU, KUMA MU YAWAITA BIJIRO MUSU DA KISSOSHI DAGA ALKUR'ANI A TAKAICE TA YADDA YARO ZAI FAHIMTA, A RINKA MAIMATA HAKAN TA HANYOYI DABAN-DABAN.

10. ANA IYA AMFANI DA HANYAR TAMBAYA DA AMSA WAJEN TARBIYYAR YARO, TAMBAYOYIN KANSU SU ZAMANA AKAN IRIN SAKON DA AKE SON ISARWA GA YARO, SANNAN AMSAR TAMBAYAR TA ZAMA A TAKAICE TA YADDA YARO ZAI YI SAURIN RIKEWA, KUMA SU ZAMANA SUNDACE DA SHEKARUN SHI DA HANGEN NESAN SHI, YIN HAKAN NA DA MATUKAR TASIRI WAJEN SAMAR DA DABI'U NAGARI GA YARO DA KUMA CANZA MUNANAN DABI'UN SHI ZUWA NAGARI.

11. ANA IYA AMFANI DA KALOLI WAJEN TARBIYYA, INDA HOTUNAN DA ZA A SANYA MUSU KALA SUKA ZAMANA SUN KUNSHI MA'ANONI NA IMANI DA ZA A RINKA CANZA SU KODA YAUSHE. HAKA MA ZA A IYA KOYAR DA YARA TA HANYAR MUSABAKA TA HANYAYOYI DABAN-DABAN, KUMA AN FI SO MUSABAKAR TA ZAMA TA ABUBUWA MASU MOTSI, SABODA YARO NA SON IRIN WADANNAN KUMA YANA JAN HANKALINSU.







**12.** AYI MA YARO SHARHIN WASU HADISAI DA SUKA SHAFI AKIDA KO WANI YANKI DAGA CIKIN SU TA YADDA ZAI YI DAI-DAI DA TUNANIN SU KUMA ABI TA HANYA MAI SAUKI KUMA MAI SOYUWA GA YARO, KUMA AYI ANFANI DA GAJERIYAR KALA TA YADDA HANKALIN YARO ZAI DAUKA, TARE DA MAIMAITA KALAMAN DA ZASU KARFAFA IMANI A ZUCIYAR YARO DON YAYI AMFANI DA SU KAI TSAYE. MISALI «ABINDA ALLAH YA KADDARA KUMA YA SO SHI KE FARUWA» «KA DOGARA GA ALLAH» «ALLAH MAI IKO NE GA DUKKAN KOMAI». SANNAN IYAYE KO MASU TARBIYYA SU TAIMAKAWA YARO WAJEN KAWATA DAKIN SHI KO AJIN SHI DA KALMOMIN IMANI MASU KYAU KAMAR: «NI MUSULMI NE. NI INA SON UBANGIJI NA. RUKUNAN IMANI DA SAURAN SU». WADANNAN HANYOYIN KOYARWAR SUNA ZAUNAR DA ABINDA AKA KARANTAR GA YARO YA ZAUNA ACIKIN KWAKWALWAR SHI TARE DA YAWAN HALARTO DA SU.

**13.** A KARANTAR DA YARO CEWA BA WANDA KE KUBUTA DAGA BALA’I, DUKKAN MUTANEN DUNIYA ALLAH KAN JARRABE SU DA WASU BALA’O’A, KOWA DA IRIN JARRABAWAR SHI, MU KARANTAR DA SHI CEWA ALLAH BAI SA ABU YA FARU BA FACE SAI AKWAI WATA HIKIMA ACIKIN HAKAN, A DASA MAI CEWA MAI JANYO AMFANUWA GA MUTUM DA KUMA KARE SHI DAGA CUTUWA SHI NE ALLAH, KUMA RAHAMAR SHI TA RINJAYI FUSHIN SHI, KUMA A YI MAI BAYANIN CEWA KODAYAUSHE MAFITA KAN ZO NE BAYAN KUNCI, WANNAN SHI NE ABINDA MAGABATAN MU SUMA SUKA FUSKANTA, KUMA MU KARANTAR DA SHI KYAUTATA ZATO GA ALLAH, HAKAN SHIMA IBADA CE A KARAN KANTA, MU TABBATAR MAI DACEWA ZABIN ALLAH SHI NE ZABI BA ZABINMU BA, DUK ABINDA YA ZABA MANA SHI NE DAIDAI, DAN HAKA BA ABINDA YAFI MA MUTUM ALKHAIRI FIYE DA YIN HAKURI LOKACIN DA MUSIBA TA FADA MAI, KUMA YAYI AMFANI DA ABUBUWAN SHARI’A WAJEN MU’AMALA DA WADANNAN MUSIBUN, YA KUMA YARDA DA HUKUNCIN ALLAH SAI YA SAMU LADA. A KARSHE MU KOYA MAI RIKO DA ADDU’A KODA YAUSHE. HAKAN SHI NE KASUWANCI MAFI RIBA GA BAWA KODA YAUSHE.

# HANYOYIN

# TARBIYYA



**DAGA CIKIN MUHIMMAN HANYOYIN TARBIYYA DA ZASU TAIMAKA WAJEN DASA IMANI ACIKIN ZUCIYAR YARO SUNE:**

1. **ABIN KOYI NAGARI:** ANA KIRGA ZAMA ABIN KOYI NAGARI DAYA DAGA CIKIN MANYAN HANYOYIN TARBIYYA DA KUMA TASIRI AKAN YARO, MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA TUNASAR AKAN MUHIMMANCIN ZAMA ABIN KOYI NAGARI GA RAYUWAR YARO. YA ZO A HADISIN ABDILLAHI BINI AMIR ((R.A)) YA CE: (WATA RANA MAHAIFIYA TA TA KIRA NI ALHALI MANZON ALLAH ((S.A.W)) YANA WAJEN MU, SAI TA CE: YA ABDALLAHI ZO KA KARBA, SAI MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE: ((ME ZAKI BA SHI)) TA CE: INA SO IN BASHI DABINO NE, SAI MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE: ((DA ACE KE BAKI BASHI KOMAI BA DA AN RUBUTA MIKI KIN YI KARYA)) [ABU-DAWUD: 4991]. YA ZO ACIKIN WATA RUWAYA ((DUK WANDA YA CE MA YARO ZO KA KARBA KUMA YAKI BASHI KOMAI TO YAYI KARYA.)) [AHMAD: 9624]. WANNAN HADISIN YA NUSASSHE MU DA MUHIMMANCIN YIN GASKIYA AGABAN YARA.

2. **WA'AZI NA GASKIYA:** ANA IYA GABATAR DA WA'AZI TA HANYOYI DABAN-DABAN, KO DAI AYI SHI KAI TSAYE KO KUMA TA HANYAR BUGA MISALI, KO TA HANYAR BADA KISSA, KO TATTAUNAWA KO MAKAMANCIN HAKA, KUMA A TAKAITA MAI WA'AZIN DAN KAR YA KOSA.



3. **KWADAITARWA DA TSORATARWA:** WANNAN HANYAR, ANA KIRAN WADANNAN HANYOYI GUDA BIYU, KYAUTATAWA DA UKUBA, KUMA ANA KIRGA WANNAN SALON DAGA CIKIN MAFI BAYYANAR HANYOYIN TAUSAYI, TA INDA YAKE TABA FIDIRAR MUTUM DA ALLAH YA HALICCE SHI AKAI. WANDA SHI NE SON ABU MAI AMFANI DA KUMA JAWO SO GA YARO. DA TUNKUDE CUTUWA. HAKAN YANA WAJABA YA KASANCE DA ADALCI DA GASKIYA BA TARE DA WUCE GONA DA IRI AKAN HAKAN BA. YARO MUTUM NE ME TSARKAKEKKIYAR ZUCIYA, BAYA KAMATUWA A TSORATAR DA SHI KO A FIRGITA SHI SABODA ZUCIYA TANA DA SAURIN TASIRANTUWA, DAN HAKA YA KAMATA A RINJAYAR DA BANGAREN KWADAITARWA SABODA YARO A WADANNAN SHEKARUN YAFI BUKATAR KWADAITARWA FIYE DA TSORATARWA.

4. **HORARWA DA SABARWA DA YAWAITA YIN ABU:** A SABARMA YARO DA KWADAYIN NEMAN YARDAR ALLAH DA TSORON SHI DA JIN KUNYAR SHI, DA KUMA DOGARO DA SHI AKODA YAUSHE, A KUMA SANYA SHI YA SABA DA CEWA DUKKANIN AL'AMURA AGURIN ALLAH ((S.W.T)) SUKE. DUKKAN WADANNAN ABUBUWAN ZASU SA YA YI KWADAYI DA KUMA YIN RIKO DA RA'AYIN SHI AKAN KOWANE AIKI, ZAI KUMA HAIFAR MAI DA YARDA DA YAKINI DA ZUCIYAR SHI ZATA NATSU DA SHI YA SAMU JIN DADI A ZUCIYAR SHI.

5. **MAIMAITAWA:** HANYA CE TA TABBATAR DA ILIMI, YAWAN MAIMAITA ABU NA SA YA ZAUNA ACIKIN KWAKWALWA, BAMA GA YARO BA HATTA GA BABBA.

6. **TATTAUNAWA:** TATTAUNAWA DA YARO KAN SA SHI YA SAMU HANGEN NESA KUMA YA BUDE MAI KOFOFIN SANIN ABUBUWA, SAI DAI DOLE A GIRMAMA RA'AYIN YARO SHI KAN SHI A KUMA KYAUTATA SAURARON SHI TARE DA TATTAUNAWA DA SHI CIKIN NATSUWA DON A SAMU NASARA A CIKI. TA DALILIN TATTAUNAWAR ZA A IYA TARBIYYAR YARON DA NUSASSHE SHI AKAN ABUBUWA DA DAMA.

7. **LITTAFI:** DAGA CIKIN HANYOYI NA TARBIYYA AKWAI SAMAR DA DAKIN KARATU MAI KYAU DA YA DACE DA BUKATUWAN YARO DA WAYEWA DA IMANI, ZAI YI KYAU YA ZAMA NAU'I-NAU'I TSAKANIN NA JI DA GANI DA KUMA NA LANTARKI. MAFI MUHIMMANCI SHI NE DAKIN KARATUN YA ZAMANA YA KUNSHI BANGAREN KISSOSHI, DOMIN KISSA HANYA CE TA CI GABAN TARBIYYA, KUMA A CIKIN TARIHIN MANZON ALLAH ((S.A.W)), DA NA SAHABBAI ALLAH YA YARDA DA SU AKWAI KISSOSHI DA SUKE DA MANUFA GA ABUBUWA MASU YAWA DA ZA A FADA MA YARO.

8. **AMFANI DA KAYAN KARANTARWA NA ZAMANI:** WADANNAN KAYAYYAKIN SUNA BUDE TUNANIN YARO SU KUMA TABBATAR DA SHI SU MATSO MAI DA ABU KUSA, HAR YA IYA FAHIMTAR ABUN NAN YA HARARO MA'ANONINSA. TA YADDA ZA A BIJIRO MAI DA WADANNAN TUNANIKAN TA HANYA MAI DAUKAR HANKALI DA AMFANI DA LAUNUKA DA ZASU JA HANKALIN YARO SU KWANTAR MAI DA HANKALI SU KUMA DACE DA ABINDA YAKE SO.

9. **ABINDA AKA HALICCI MUTUM AKAN SHI:** AKWAI WASU ABUBUWA MASU YAWA GA YARO DA AKA HAIFE SHI DA SHI KAMAR; WASANNI DA TAIMAKO DA KWAIKWAYON MUTANE DA MAKAMANCIN HAKA, TA HANYAR WASA YARO ZAI IYA GANE IRIN DUNIYAR DA YAKE CIKI, DA KUMA FITAR DA ABINDA YAKE SURANTAWA DA KUMA IYAKACE HANGEN NESAN SHI, ZA A IYA FITAR DA HAKA TA HANYAR FAYYACE INGANTATTUN MA'ANONIN ABUBUWAN DAKE GEWAYE DA SHI, HAR WA YAU KUMA SABODA DASA DABI'U NAGARI A ZUCIYAR YARO, ZA A YI HAKAN NE TA HANYA MAFI SAUKI KUMA TA HANYAR DA TA DACE

10. **ADDU'A:** ADDU'A DALILI NE DA BAWA ZAI KANKAN DA KAI GA UBANGIJIN SHI DA BUKATUWAR SHI ZUWA GARESHI DA KUMA FATAN SHI GA FALALAR SHI ((S.W.T)), ALLAH YA KWADAITAR DA BAYAIN SHI AKAN YIN ADDU`A KUMA YAYI MUSU ALKAWARIN AMSAWA. ALLAH ((S.W.T)) YA CE: {KUMA UBANGIJIN KU YA CE KU ROKE NI ZAN AMSA MUKU.} [ GHAFIR: 60], KUMA ADDU'A NA DAGA CIKIN MAFI GIRMAN HANYOYIN DA MAI TARBIYYA ZAI KAI GA KOLOLUWAR ABINDA YAKE SO YA KAI A TARBIYYA, ITA CE HANYAR DA MANYAN MASU TARBIYYA SUKA YI AMFANI DA ITA WAJEN TARBIYYA, WATO ANNABAWAN ALLAH ALAIHIMUSSALAM DAN SU TABBATAR DA IMANI DA TAUHIDI. ALLAH ((S.W.T)) YA CE: {KA TUNA SANDA IBRAHIM YA CE: YA UBANGIJI NA KA SANYA WANNAN GARI AMINTACCE KUMA KA NISANTA NI DA 'YA'YA NA DAGA BAUTA MA GUMAKA [IBRAHIM: 35] ADDU'A GA YARO NA DA MUHIMMANCI MATUKA.

**11. KAMANTAWA DA KWAIKWAYO:** YARO A DABI'AR SHI YANA SON KWAIKWAYO, TUNDA HAKA NE, SAI A SAMU WATARANA MISALI YA ZAMA LIMAMIN MASALLACI, YAYI SALLAH YAYI KARATU, KO YA YI HUDUBA, YA TASHI YAYI MAGANA, KO YA TASHI A MATSAYIN MALAMI YA KOYAR TARE DA YIN BAYANI, DA MAKAMANTAN HAKA. WANNAN SHI NE ABINDA ZAI BAYYANA MAI ABUBUWAN DA AKE NUFI YA KUMA KIYAYE KIMAR WADANNAN ABUBUWAN AGARE SHI.



## SIFFOFIN

# ME TARBIYYAH



**1.** **TAUSAYI DA JIN KAI.** DADIN TARBIYYA BAYA ZUWA MATUKA BA IDAN BA A HADA DA TAUSAYI BA DAN ZUCIYA TA MAMAYE DA RAHMA, GA AKRA'U BIN HABIS YANA KALLON MANZON ALLAH. ((S.A.W)) YANA SUMBATAR HASAN DA HUSAIN, SAI YA CE: INA DA 'YA'YA GOMA BAN TABA SUMBATAR DAYA DAGA CIKIN SU BA, SAI MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE:(( DUK WANDA BAYA JIN KAI BA ZA A JI KAN SHI BA.)) [BUKHARY: 5997], KUMA MANZON ALLAH ((S.A.W)) YA CE (( MASU RAHMA AR-RAHMAN YANA JIN KAN SU, KU JI TAUSAYIN WADANDA KE DORON KASA, SAI WANDA KE SAMA YA JI KAN KU)) [ ABU-DAWUD: 4941]

**2.** **HAKURI DA YAFIYA:** MANZON ALLAH (S.A.W) YA KAI KOLOLUWA A WADANNAN DABI'UN, ANAS BIN MALIK (R.A) YA RAWAITO CEWA (WATA RANA INA TAFIYA TARE DA MANZON ALLAH (S.A.W) YANA SANYE DA MAYAFI DAN NAJRANA MAI CIN BAKI, SAI WANI BALARABEN KAUYE YA HADU DA SHI, SAI YA JA MAI MAYAFINSA DA KARFI HAR SAI DA NA GA KAFADAR MANZON ALLAH (S.A.W) BAKIN MAYAFIN YAYI MATA SHEDA SABODA TSANANIN FIZGAR DA YAYI MAI, SAI YA CE YA MUHAMMAD KA BANI DAGA DUKIYAR ALLAH DA KE WAJEN KA, SAI MANZON ALLAH (S.A.W) YA JUYA ZUWA GARE SHI YAYI DARIYA SANNAN YAYI UMURNIN A BASHI. [BUKHARY: 5809].

DAGA CIKIN AL'AMURAN DA SUKE TAFIYA TARE DA HAKURI AKWAI AFUWA. ALLAH (S.W.T) YA CE: {KA RIKI AFUWA KUMA KAYI UMURNI DA ABU MAI KYAU, KUMA KA KAU DA KAI GA BARIN JAHILAI} [A'ARAF: 199], DUK DAN A TABBATAR DA HAKURI MANZON ALLAH (S.A.W) YA KWADAITAR AKAN RASHIN YIN FUSHI KUMA YAYI HANI AKAN SHI, YA ZO A CIKIN HADISI INGANTACCE CEWA WANI MUTUM YA CE MA MANZON ALLAH (S.A.W) KAYI MIN WASIYYA, SAI ANNABI (S.A.W) YA CE: ((KADA KAYI FUSHI)) SAI MUTUMIN YA MAIMAITA, SAI YA CE MAI ((KADA KAYI FUSHI)) [BUKHARY: 6116]

**3.** **JURIYA:** YA WAJABA GA MAI TARBIYYA YA KAWATU DA JURIYA DA KUMA RASHIN GAGGAWA YAYIN TARBIYYA KO KARANTAR DA 'YA'YAN SHI, KUMA KADA MAI TARBIYYA YAYI GAGGAWA WAJEN BAYYANA SAKAMAKON ABINDA YA KE YI NA TARBIYYA, HAR YA



SANYA MA KAN SHI DEBE TSAMMANI DA KUMA JIN SAMUN MATSALA ACIKIN TARBIYYAR DA YAKE YI, IDAN MAI TARBIYYA YA ZAMANA BASHI DA HAKURI TO KAMAR MAI TAFIYA NE BA GUZURI.

4. **ADALCI:** IDAN AKA BANBANCE TSAKANIN MUTUM DA MUTUM BA TARE DA WANI DALILI BAYYANANNE BA TO, ZA A SAMU KARANCIN TASIRANTUWA DA CUREWA AWAJEN WADANDA AKE TARBIYYANTARWA, KUMA DUK SANDA AKA SAMU ZALUNCI ACIKIN WANI ABU TO SAI ZALUNCIN NAN YA MUNANA SHI.

5. **AMANA:** YA WAJABA GA MAI TARBIYYA YA KASANCE MAI GASKIYA KUMA AMINTACCE AWAJEN MU'AMALAR SHI GA WADANDA YAKE TARBIYYA, AMANA NA DAGA CIKIN SIFFAR MANZONNI, KUMA ITA CE BABBAR ABINDA AKE NEMA WAJEN KYAUTATA AIKI DA KAIWA GA KOLOLUWAR SHI DA CIN NASARAR SHI.

6. **TSORON ALLAH:** DUK WANDA YAJI TSORON ALLAH TO, ZAI DATAR DA SHI TA INDA BAYA TSAMMANI, TSORON ALLAH YANA SA A SAMU DACEWA DA TSIRA DA GYARUWA DA CIN NASARA DUNIYA DA LAHIRA.

7. **TSARKAKE ZUCIYA:** DUK AIKIN DA YA KASANCE BA DAN ALLAH BA TO ZA A MAYAR MA MUTUM DA ABIN SHI, KUMA ZAI ZAMANA BABU KOMAI ACIKIN AIKIN SHI FACE AIKIN BANZA.

**8.** **ILIMI:** SHI MAI ILIMI YA NA KASANCEWA NE MAI HANGEN ABINDA KE FARUWA YANZU DA WANDA ZAI BIYO BAYA, SABANIN JAHILI WANDA KE ASARAR ABINDA KE FARUWA YANZU YA KUMA MUNANA ABINDA ZAI ZO A GABA.

**9.** **HIKIMA:** ANAN, MAI TARBIYYA ZAI SANYA KOMAI INDA YA DACE A SANYA SHI, DOMIN AL'AMURA SUNA BADA AMFANINSU NE, SAI TARBIYYA TA FIDDA SAKAMAKON, AIKIN MAI TARBIYYA SHI NE YA SHIGA ZUWA CIKIN ZUCIYA YA CI GABA DA NUSASSHE DA YARO DA TARBIYYAR SHI.

**10.** **IMANI DA AIKIN TARBIYYA:** IMANI SADAUKARWAR ZUCIYA NE DA RUHI, WANDA BAI YI IMANI DA AIKIN TARBIYYA BA TO BA ZAI IYA GABATAR DA WANNAN NAU'IN NA SADAUKARWA BA.

**11.** **CI GABA:** MAI TARBIYYA YA BADA MUHIMMANCI WAJEN CI GABAN ABUBUWAN DA YAKE YI DOMIN YA KAI ZUWA GA MATAKIN BADA ABINDA YA KAMATA YA BADA NA TARBIYYA.







# RUKUNAN TARBIYYAR DASA IMANI



RUKUNI

RUKUNI NA FARKO:
**IMANI DA ALLAH**

RUKUNI NA BIYU:
**IMANI DA MALA’IKU**

RUKUNI NA UKU:
**IMANI DA LITTAFAI**

RUKUNI NA HUDU:
**IMANI DA MANZONNI**

RUKUNI NA BIYAR:
**IMANI DA RANAR LAHIRA**

RUKUNI NA SHIDA:
**IMANI DA KADDARA**

## RUKUNI NA FARKO:

# IMANI DA ALLAH



FIDIRA DA HANKALI DA SHARI'A SUN YI NUNI AKAN SAMUWAR ALLAH, KO WACCEE HALITTA TANA KAN IMANI DA ABIN HALITTARTA NE, HANKALI YAYI NUNI AKAN WADANNAN HALITTUN DOLE YA KASANCE AKWAI ABINDA YA SAMAR DA SU, ITA KUMA SHARI'A TA YI NUNI AKAN DUKKAN ADDINAN DUNIYA SUN TABBATAR DA SAMUWAR MAHALICCI. DAN HAKA IMANI DA ALLAH YA KUNSHI AL'AMURA GUDA HUDU:

1- SAMUWAR ALLAH.

2- IMANI DA RUBUBIYYAR SHI. DA KUMA CEWA SHINE ME BADAWA, MAHALICCI, MAI AZURTAWA, MAI KUMA JUJJUYA AL'AMURA.

3- IMANI DA KADAITUWAR ALLAH, BASHI DA ABOKIN TARAYYA.

4- IMANI DA SUNAYEN SHI DA SIFFOFIN SHI MASU TABBATAR DA CIKAR KAMALA DA KYAWUN.

ZAMU KOYA MA YARO WADANNAN ABUBUWAN GUDA HUDU, YA TARBIYYARTU AKAN SANIN ALLAH DA GIRMAMA SHI DA SON SHI. WANNAN RUKUNIN SHI NE TUSHEN SAURAN RUKUNAN. IN YA KIYAYE YA SAN SHI TO ZAI GANE SAURAN IN SHA ALLAH.

### ME YASA ZAMU KOYA MUSU SON ALLAH?

**1.** SABODA ALLAH DA SHA'ANIN SHI YA GIRMAMA SHI NE YA SAMAR DA MU DAGA RASHI, YA KUMA DAIDAITA HALITTAR MU YAYI MU DA SURA MAI KYAU, YA KUMA DAUKAKA MU AKAN DA YAWA DAGA SAURAN HALITTU, YA KUMA YI MANA MAFI GIRMAN NI'IMA WATO MUSULUNCI, SANNAN YA AZURTA MU DA ABUBUWA MASU YAWA DAGA FALALAR SA BA TARE DA MUN CANCANCI HAKAN BA, SANNAN SHI DIN ZAI MAI DA MU CIKIN ALJANNA SAKAMAKON AYYUKAN DA MUKA AIKATA, WANDA HAKAN KYAUTAR SHI CE DA FALALAR SHI A GARE MU. DAN HAKA ALLAH SHINE YA KAMATA A DAUKAKA TUN FARKO DA KARSHEN RAYUWA.

**2.** SABODA SO NA HAIFAR DA GIRMAMAWA DA KWARJINI A ASIRCE DA BAYYANE, AMMA BUKATUWAR MU ZUWA GA YARAN MU SU GIRMAMA UBANGIJIN SU SUJI KWARJININ SHI YAFI FIYE DA A CE ALAKAR SU DA SHI TA TSAYU NE AKAN TSORO DA UKUBAR SHI KO AZABAR JAHANNAMA KADAI. IN AKA GINA SU AKAN HAKAN, TO, SAI YA KASANCE SUNA JIN DADIN BAUTA MAI SU RAYU ACIKIN JIN DADI SABODA ITA, SU KUMA KU BUTA DAGA DUKKAN WATA ZAMIYA.

3. SABODA ALLAH SHINE RAYAYYE TSAYAYYE AKODA YAUSHE WANZAJJE WANDA BA YA MUTUWA, WANDA GYANGYADI KO BACCI BASA DAUKAR SHI, SHI YANA TARE DA SU A DUK INDA SUKE, SHI YAKE KIYAYE SU YA KULA DA SU FIYE DA IYAYEN SU, DAN HAKA, DANFARUWAR SU DA SHI DA SON SHI YA ZAMA DOLE HAR SU SAN CEWA SUNA DA ABIN DOGARO MAI KARFI WATO ALLAH (S.W.T).

4. SABODA KUMA IDAN SUN SO ALLAH AZZA WAJALLA TO ZA SU SO KUR'ANI, SU RINKA SALLAH. IDAN KUMA SUKA SAN ALLAH MAI KYAU NE YANA SO ABU MAI KYAU TO ZASU AIKATA DUK ABINDA SUKA SAN YANA DA KYAU,IDAN KUMA SUKA SAN ALLAH YANA SON MASU TUBA KUMA YANA SON TSARKAKKU, DA MASU KYAUTATAWA DA MASU GASKIYA DA MASU HAKURI DA MASU TAWAKKALI, DA MASU TSORON ALLAH, TO ZASU YI KOKARI DAN SU SIFFATU DA DUKKAN WADANNAN SIFFOFIN DOMIN NEMAN YARDAR SHI DA SOYAYYAR SHI DA TSIRA DA SAMUN YARDARSA AGARE SU DA KARIYAR SHI AGARE SU. IDAN KUMA SUKA SAN ALLAH BAYA SON MASU HA'INCI KUMA KAFIRAI MASU GIRMAN KAI DA TSAURIN IDO, DA ZALUNCI MASU FASADI A DORON KASA TO ZASU NISANCI WADANNAN MUNANAN AYYUKAN GWARGWADON IYAWAR SU. ZASU NISANCE SU NE DUKA DOMIN SON SU GA ALLAH DA KWADAYIN NEMAN YARDAR SHI.

5. SABODA SON ALLAH NA NUFIN JIN SAMUWAR ALLAH TARE DA MU WANDA YAKE SA MUTUM YA SAMU NATSUWA DA JIN DADI DA TABBATUWA, DA RASHIN SHIGA DAMUWA DA BAKINCIKI, DA KUBUTAR ZUCIYA DA JIKI DAGA CIWUKAN ZUCIYA DA GABBAI, WANDA YAFI WANNAN MUHIMMANCI SHI NE KUBUTA DAGA SABUKA DA ZUNUBAI.



## YAYA ZAMU KOYAWA 'YA'YANMU SON ALLAH (S.W.T)?

1. ANA KIRGA CEWA HANYA DAYA DA ZA A BI WAJEN DASA MA YARO TAUHIDI SHI NE TA HANYAR GANI KARARA, MA'ANA MU MUKAN DOGARA AKAN GABBAN JI WAJEN KARFAFA IMANIN YARO GA UBANGIJIN SHI, SAI MU YI AMFANI DA ABUBUWAN DA YAKE GANI A TARE DA SHI KAMAR RANA, RUWA, ISKA, DAGA WADANNAN ABUBUWAN DA YAKE GANI ZAMU KOYA MA YARO CEWA AKWAI MAHALICCI WANDA SHI KE JUYA WANNAN DUNIYAR, KUMA MU KWADAITAR DA SHI AKAN YA RINKA TAMBAYA ANA MAI BAYANIN ABINDA BE GANE BA ANA MAI BAYANI, MU KUMA YI KOKARI WAJEN NUNA MA YARO ABUBUWA DA ZASU KARA IMANI SU GANI DA IDO TA YADDA ZASU GANE HUJJAR CEWA LALLAI AKWAI ALLAH A DUKKAN KOMAI, A WARWARE MUSU SU, SANAR DA SHI FANNONIN ILIMI, MU NUNA MUSU IKON ALLAH AKAN MU`UJIZOZI NA ALLAH, DAGA CIKIN IRIN ABINDA ZA A NUNA MUSU WANDA DOLE ZAI SA SU GANE HAKAN SHI NE FARKON HALITTAR DAN ADAM WATO YADDA AKA HALICCI DAN ADAM, ALLAH (S.W.T) YA CE, { MUTUM YA DUBA DAGA ME AKA HALICCE SHI.) [TARIK:5], YA KUMA CE { KUMA ACIKIN KAWUNAN KU AKWAI AYOYI SHIN BA ZAKU DUBA BA? } [ZARIYAT: 21], HAKA MA DUBI ZUWA GA ABINCIN MUTUM DA YADDA ALLAH YA SAMAR DA SHI YA KUMA BAYYANA MATAKAN SHI. ALLAH (S.W.T) YA CE: {MUTUM YAYI DUBI ZUWA GA ABINCIN SHI.} [ABASA: 24], HAKA DUBA ZUWA GA IRIN IKO NA ALLAH TA HANYAR DUBA ZUWA GA HALITTUN SHI DA SUKE NUNI AKAN GIRMAN SHI KAMAR YADDA ALLAH (S.W.T) YA FADA: {ASHE BA KUYI DUBI ZUWA GA RAKUMI BA YADDA A KA HALICCE SHI (17) DA SAMA YADDA AKA DAGA TA (18) DA DUWATSU YADDA AKA KAFE SU (19) DA KASA YADDA AKA SHIMFIDA TA} [AL-GHASHIYAT: 17- 20]. ANA IYA MATSO DA WADANNAN MANYAN MA'ANONIN DA ABINDA KE CIKIN SU NA KYAWUN HALITTA DA GIRMAN MAHALICCI A KWAKWALWAR YARA DAI-DAI DA SHEKARUN SU, ARINKA CANZA MUSU HANYOYIN BAYANAN DON SAKON YA ISA TA HANYAR AMFANI DA HANYOYIN KOYARWA KALA-KALA NA DA DA NA ZAMANI. A YADDA YARO YAKE, ZAI SO WANDA YA HALITTA MAI IRIN WADANNAN KYAWAWAN ABUBUWAN MASU GIRMA.

2. KOYA MA YARO SUNAYEN ALLAH KYAWAWA DA SIFFOFIN SHI DA SUKE NUNI AKAN KAMALA DA KYAWUN SHI, ALLAH (S.W.T) SHI NE MAI RAHMA MAI JIN KAI, WANDA RAHAMAR SHI TA MAMAYE DUKKAN KOMAI, SHI NE MAI AFUWAN DA YAKE YAFIYAR KOWACCE IRIN ZAMIYAR DA MUTUM YA SAMU, KUMA SHI NE MAI GAFARAR DA YA TATTARA AFUWA MAI SITIRTAWA, KUMA MAI KARAMCI DA YAKE BAYARWA GA MABUKACI BA TARE DA DALILI BA, KUMA MAI SHIRYARWA DA YAKE SHIRYAR DA BAYI ZUWA GA DUKKAN ABUBUWA MASU AMFANI, MASOYI DA YAKE SO A KUMA SO SHI, SANIN WADANNAN ABUBUWAN BA MAKAWA ZASU TAIMAKAWA YARO WAJEN SON ALLAH.

3. YA WAJABA MU NISANCI FADA MA YARO CEWA IDAN BAKA JIN MAGANA TABA KUMA KA YI MIN BIYAYYA TO ALLAH ZAI MAKA UKUBA, AKWAI BANBANCI TSAKANIN SANAR DA YARO CEWA ALLAH NA YIN UKUBA GA WADANDA YA SABA MAI DA KUMA HADA UKUBAR ALLAH DA YIN BIYAYYA AKODA YAUSHE KAR A YI WA YARO BARAZANA AKAI, WANNAN NA DAGA CIKIN ABIN DA ZAI HANA DAN KU YIN TUNANI MAI ZURFI AKAN KUDIRAR ALLAH DA GIRMAN SHI, BAI KAMATA A DOGARA DA TARBIYYAR AKAN YI MAI BARAZANA DA UKUBAR ALLAH BA, SAI DAI WAJIBIN MU NE MU KOYA MAI SON ALLAH DA GIRMAMA SHI KADA MU JINGINA DUK ABINDA MUKA SAN ZAI MA YARO TASIRI A MAHANGAR SHI GAME DA ALLAH (S.W.T).

4. ALOKACIN DA YARO YA GA IYAYEN SHI SUNA GABATAR DA SALLAH KO WANI ABU NA FARILLA, KO SUNA YIN WANI ABU DA YAKE HARAMUN NE, SO DA DAMA YA KAN TAMBAYI DALIKIN AIKATA HAKAN, DOLE A WANNAN LOKACIN TAMBAYAR TA ZAMANA AMSAR DA ZA A BASU TA KUNSHI AMBATON ALLAH TA’ALA TARE DA YI MAI BIYAYYA, HAKAN SAI YA KASANCE TARBIYYA DA KOYI GA WANDA KE TARBIYYAR SHI AKAN SON ALLAH, SABODA SHI YARO YANA KWAIKWAYON IYAYEN SHI NE, KUMA DAGA ACIKIN ABUBUWAN DA KE DASA SON ALLAH ACIKIN ZUCIYAR YARO SHI NE BA SU LABARI AKAN ALJANNAH DA ABINDA ALLAH YA TANADAR ACIKIN TA GA BAYIN SHI MASU TSORON SHI NA DAGA NI’IMA DA BATA GUSHEWA.

5. IDAN YARO YA KAI SHEKARUN DA YA GANE ME AKE NUFI DA WAJIBI, TO SAI A KOYA MAI WAJABCIN WANNAN SON GA ALLAH, SABODA ALLAH (S.W.T) SHI NE WANDA YA HALICCE MU YA KUMA DAIDAITA HALITTAR MU YA AZURTA MU YA KUMA DAUKAKA MU AKAN DA YAWA DAGA CIKIN SAURAN HALITTUN SHI YA KUMA YI MANA NI’IMA DA MUSULUNCI, KUMA MU KOYA MA YARO CEWA DUKKAN NI’IMOMIN DA KE KEWAYE DA SHI DAGA ALLAH NE, MU KUMA KOYA MAI YADDA AKE GODEMA ALLAH AKAN WADANNAN NI’IMOMIN AKUMA TAMBAYE SHI KARI AKAI.



6. AKOYA MAI HANYOYIN DA ZAI DOGARA DA SU WAJEN SAMUN SOYAYYAR ALLAH DA MANZON SHI (S.A.W) NA DAGA MAGANGANU DA AYYUKAN SHI.

## RUKUNI NA BIYU:

# IMANI DA MALA'IKU





GASGATA SAMUWAR SU, DA IMANI DA ABINDA MUKA SANI NA SUNAYEN SU, DA ABINDA YA INGANTA NA DAGA LABARAI AKAN SU DA SOYAYYAR SU, DAGA CIKIN MANYAN ABINDA YA KAMATA A DASA MA YARO A ZUCIYAR SHI AGAME DA MALA'IKU SU NE:

1. SANAR DA SHI CEWA SU MALA'IKU HALITTU NE DA AKA HALICCE SU DAGA HASKE. DAGA AISHA (R.A) TA CE: MANZON ALLAH (S.A.W) YA CE: ((AN HALICCI MALA'IKU DAGA HASKE, KUMA AN HALICCI ALJANU DAGA WUTA, KUMA AN HALICCI ADAM DAGA ABINDA AKA SIFFANTA MUKU)) [MUSLIM: 2996], ASIFFANTA MUSU A DUNKULE BA TARE DA AN TSAYA RARRABE MUSU WANNAN HALITTA TA MALA`KU DA DABI`ARSU BA.

2. A KOYA MISHI SUNAYEN SU DA AYYUKAN SU, KAMAR ACE MAI JIBRIL SHI NE AMINTACCEN MALA'IKU KUMA SHI NE SHUGABAN SU SHI NE ALLAH YA SAUKAR DA AL KUR'ANI TA HANNUN SHI. MIKA'IL SHI NE ME KULA DA SAUKAR RUWAN SAMA, ISRAFIL SHI NE ME BUSA RAI, KUMA AKWAI MASU DAUKE DA AL'ARSHIN ALLAH, AKWAI MASU RUBUTA AYYUKAN BAYI, AKWAI MASU TSARON 'YAN ADAM DA SAURAN SU.

3. YI MUSU BAYANIN CEWA ADADIN MALA'IKU NA DA YAWA SOSAI DAN HAKA BA WANDA YA SAN ADADIN SU SAI ALLAH, KUMA AN HALICCE SU KAWAI DON YI MA ALLAH BIYAYYA DA BIN UMURNIN ALLAH, KUMA KO WANE MALA'IKA AKWAI AIKIN SHI DA AKA DORA MAI YAKE YI.

4. A SANAR DA SU CEWA SU BASA ZUNUBI, SUNA BAUTA MA ALLAH IBADAR DA BATA YANKEWA, BASA GAJIYA DA BAUTA MAI KUMA BASA GIRMAN KAI, KUMA SUNA SON MUMINAI SUNA TAIMAKON SU SUNA YI MUSU ADDU'A SUNA BASU KARIYA, KUMA SUNA HALATTAR MAJALISAN DA AKE AMBATON ALLAH SUNA BIBIYARSU.

5. A SANYA MA YARO SON MALA'IKU TA HANYAR SANAR DA SU YANAYIN AIKIN ALKHAIRI NA MALA'IKU DA NUNA MUSU HALAYEN MALA'IKU NA KULA DA KWADAYIN SU GA MUMINAI, INDA AKE SANYA SO GA WADANNAN HALITTUN MASU ALBARKA DA SALIHANCI, SABODA SUNA TASBIHI DA ISTIGFARI DA ADDU'A GA MUMINAI DA KUMA YIN BUSHARAR SHIGA ALJANNAH GA MUMINAN DA SUKA TSAYU AKAN HANYAR GASKIYA DA IMANI DA AIKI NAGARI, KUMA SUNA YIN SALATI GA MUMINAI SUNA TAIMAKON SU SU TABBATAR DA SU, DA KUMA CEWA SU MASU KIYAYEWA NE GA AYYUKAN SU, ALLAH YANA AIKO SU DON KIYAYE BAYI. ALLAH TA'ALA YA CE: { KOWANNEN KU YANA DA WADANSU MALA'IKU MASU MAYEWA JUNA A GABA GARE SHI DA BAYA GARE SHI, SUNA TSARE SHI DA UMURNIN ALLAH...} [ RA'AD: 11)]

6. IMANI DA SU SHI NE KE WAJABTA A GIRMAMA SU A DAUKAKA SU, SU BAYI NE MASU GIRMA BA SA SABA ABINDA ALLAH YA UMURCE SU, KUMA SUNA AIKATA ABINDA YA UMURCE SU, KUMA YA WAJABA A TSARKAKE SU DAGA SIFFOFIN DA BAI DACE DA SU BA.

7. KWADAITARWA GAME DA TSAFTA  TA YADDA MALA`IKU KAN CUTU DAGA IRIN ABINDA YAN ADAM KAN CUTU DAGA GARE SHI. DAGA JABIR (R.A) YA CE: MANZON ALLAH (S.A.W) YA CE: (( DUK WANDA YA CI DAGA WANNAN BAKLIYYAR, TAFARNUWA (BAKALIYYA SHI NE DUK ABINDA SHUKARTA KE FITOWA DAGA KASA KAMAR DOYA) SAI YA KUMA MAIMAITA; DUK WANDA YA CI ALBASA DA TAFARNUWA DA KURRAS TO KADA YA KUSANCI MASALLACIN MU, DOMIN MALA'IKU SUNA CUTUWA DAGA ABINDA 'YAN ADAM KE CUTUWA DA SHI [MUSLIM: 564]

8. ACIKIN SAMUWAR MALA'IKU AKWAI HIKIMOMI MASU YAWA; DAGA CIKI SHI NE DAN MUTUM YAKE SANIN GIRMAN ILIMIN ALLAH DA GIRMAN IKON SHI DA GIRMAN HIKIMAR SHI. DAGA CIKI SAMUWAR MALA'IKU NA SA MUTUM MUSULMI YA JI NATSUWA SABODA YA SAN AKWAI MASU BASHI KARIYA BISA UMURNIN ALLAH KUMA SUNA TAIMAKON SHI.

9. ALAKAR MALA'IKU DA MU WAJEN HALITTA DA SAMAR DA MU DA KULAWAR DA SUKE BAMU TUN KAFIN A SAMAR DA MU HAR AKA SAME MU  TANA SA ASAN CEWA LALLAI DAN ADAM YANA DA MUHIMMANCI, YANA DA KIMA, KUMA TANA KORE TUNANIN CEWA SHI BA KOWA BANE KO KUMA SHI KARAMIN ABU NE, DAN HAKA TA HAKA NE ZAI SAN GIRMAN KAN SHI, KUMA YAYI IYA KOKARIN SHI WAJEN SAUKAR DA ABUBUWAN DA YA KAMATA YAYI A RAYUWAR SHI TA DUNIYA.

## RUKUNI NA UKU:

# IMANI DA LITTAFAI

### IMANI DA LITTAFAI YA KUN SHI ABUBUWA KAMAR HAKA:

1. IMANI DA LITTAFAN DA ALLAH YA SAUKAR, KUMA WANNAN YANA DAGA CIKIN MANYAN RAHAMAR ALLAH GA BAYIN SHI, INDA YA SAUKAR DA LITTAFI GA KOWACE AL'UMMA DA YA ZAMA SHIRIYA A GARE SU TA YADDA YA DACE DA SU NA DAGA SHARI'O'A DA HUKUNCE-HUKUNCE. KUMA A BAYYANA MA YARO CEWA SAUKAR DA LITTAFAI DA ALLAH YAYI BA KARAMAR NI'IMA BA CE GA BAYI, SABODA DALILIN HAKAN MUKA SAN ALLAH DA RANAR LAHIRA MUKA KUMA SAN ABINDA YAKE DAI-DAI DA WANDA BA DAI-DAI BA.
2. GASGATAWA GA SUNAYEN SU DA AKA FADA MANA, KAMAR LITTAFIN ANNABI IBRAHIM, DA ATTAURAH DA AKA SAUKAR DA ITA GA ANNABI MUSA (A.S), DA ZABURA TA ANNABI DAWUD (A.S), DA INJILA DA AKA SAUKAR DA ITA GA ANNABI ISA (A.S), SAI ALKUR'ANI DA AKA SAUKAR DA SHI GA ANNABI MUHAMMAD (S.A.W).
3. CEWA WADANNAN LITATTAFAN SASHIN SU NA GASGATA SASHI, BABU KARYATAWA A TSAKANINSU, KUMA BABU TUFKA-DA-WARWARA DA CIN KARO A TSAKANIN SU. ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA CE: {... YANA ME GASGATAWA GA ABINDA YAKE GABA GARE SHI NA DAGA LITTAFI} [MA'IDAH:48]



4. GASGATA ABINDA YA INGANTA NA LABARAN DA SUKA ZO MANA GAME DA SU LITTAFAN, A SANAR DA SHI CEWA DUKKAN LITTAFAN DA ALLAH YA SAUKAR WADANDA SUKA GABATA AKWAI CANJE-CANJE ACIKIN SU SABODA SU SUN TAKAITU NE NA ZUWA WANI LOKACI KEBANTACCE IYA ZAMANIN DA AKA SAUKAR DA SU KAWAI, SAI DAI ALKUR'ANI SHI ALLAH YA KARE SHI BA ME IYA CANJA SHI.

5. ALKUR'ANI YA SHAFE HUKUNCE-HUKUNCEN DUKKAN SAURAN LITTAFAI DAKE GABANIN SHI, SANNAN AIKI DA HUKUNCE-HUKUNCE NA ALKUR'ANI DOLE NE HAR ZUWA RANAR TASHIN ALKIYAMAH. YA WAJABA A YI AIKI DA UMURNIN SHI A KUMA GUJE MA ABINDA YAYI HANI DA SHI, A HARAMTA ABINDA YA HARAMTA A KUMA HALASTA ABIN DA YA HALASTA, DA AIKI DA FAYYACACCEN BAYANIN SHI DA MIKA WUYA GA ABINDA KE DA RIKITARWA A CIKIN SHI, DA TSAYAWA INDA YACE A TSAYA DA KUMA TSAYUWA AKAN KOYARWAN SHI.

KUMA DAGA CIKIN AL'AMURA MASU MUHIMMANCI DA ZA SU SHIGA CIKIN BABIN IMANI DA LITTAFAI SU NE: MAS'ALAR HADDATAR DA YARA ALKUR'ANI TUN SUNA KANANA, KUMA ANA SANYA HADDAR ALKUR'ANI DAYA DAGA CIKIN ABUBUWA MASU MUHIMMANCI WAJEN KARA KAIFIN BASIRA GA YARA, IDAN AKA KYAUTATA SHI KUMA MAI TARBIYYA YA IYA SA YARON YA RAYU TARE DA TUNO MA'ANONIN AYOYI, ALKUR'ANI YANA KIRAN MU ZUWA GA LURA DA TUNANI AKAN HALITTUN SAMMAI DA KASSAI, DA KUMA HALITTAR DAN`ADAM DA ABUBUWAN DA AKA HALITTA A KEWAYE DA MU DON YA KARA MANA IMANI YA SA MUYI AIKI DA ILIMI, KUMA HADDAR ALKUR'ANI MAI GIRMA DA SANIN MA'ANONIN SHI YANA KAI MUTUM ZUWA GA ZAMA MAI WAYO SOSAI, KUMA YANA SA YARO YA ZAMA MAI FASAHA DA IYA BAYANI, WANNAN KUMA ZAI FARU NE TA DALILIN SABA MA HARSHEN YARO DA KARATUN KUR'ANI DA KYAU SANNAN YANA TARBIYYANTAR DA ZUCIWA WAJEN TUNA ALLAH DA SANYA TSORO, DA KHUSHU'I, DA KWADAITARWA DA TSORATARWA DA KUMA TAUSHIN ZUCIYA, KUMA YARO ZAI SABA DA AIKI DA ABINDA KUR'ANI YA KOYAR DA LADUBBAN SHI A KOWA NE BANGARE DAGA BANGARORIN RAYUWA NA YAU DA KULLUM, KUMA YARO ZAI TARBIYYARTU AKAN RAYUWA MAI TSARI DA DABI'U NAGARI. DAGA CIKIN FA'IDAR IMANI DA LITTAFAI SHI NE ABINDA MUTUM ZAI SAMU NA LADA MAI GIRMA DA FALALA MAI YAWA DAGA ALLAH MADAUKAKIN SARKI A HALKA TA HADDAR ALKUR'ANI.



## TA YAYA ZAMU KWADAITAR DA YARO YIN HADDAR ALKUR'ANI?

1. ZA A YI MISHI BAYANI YA SAN FALALAR ALKUR'ANI, DA FALALAR HADDACE SHI DA TILAWAR SHI DA AIKI DA SHI, KAMAR YADDA MANZON ALLAH (S.A.W) YA CE: «KU KARANTA ALKUR'ANI, DOMIN ZAI ZO A RANAR KIYAMA A MATSAYIN MAI CETO GA MA`ABOTANSA» (MUSLIM (804)), KUMA DA FADIN MANZON ALLAH TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI - YA CE: «ZA A CE WA MA'ABOCIN ALKUR'ANI: KARANTA, KA HAU, KA KARANTA KAMAR YADDA KAKE KARANTAWA A DUNIYA, SABODA MATSAYINKA YANA AYAR KARSHE DA ZAKA KARANTA». (TIRMIZI: 2914)), DA FADINSA – TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI: "MISALIN MUMINI WANDA YAKE KARANTA ALKUR'ANI KAMAR GWANDAR DAJI NE, KAMSHINTA MAI DADI NE KUMA DANDANOTSA YANA DA DADI, KUMA MISALIN MUMINI WANDA BA YA KARANTA ALKUR'ANI. KAMAR DABINO NE, BA SHI DA KANSHI AMMA YANA DA ZAKI, KUMA MISALIN MUNAFIKIN DA YAKE KARANTA ALKUR'ANI KAMAR FULAWA EE, TANA DA KANSHI AMMA TANA DA DACI, KUMA MISALIN MUNAFIKIN DA BA YA KARANTA ALKUR'ANI KAMAR GUNA NE, BATA DA KANSHI KUMA GATA DA DACI". (BUKHARI (5427)), DA FADINSA - ALLAH YA YI SALATI DA SALAMA A GARE SHI:» MAFIFICINKU SHI NE WANDA YA KOYI ALKUR'ANI KUMA YA KOYAR DA SHI". (BUKHARI (5027)), KUMA A AMBACI MISALAI NA MAGABATA GAME DA ALKUR'ANI, KUMA WANNAN YANA DAYA DAGA CIKIN MANYA-MANYAN HANYOYIN KARA KWAZO.
2. A SANYA SHI A MAKARANTU KO HALKOKI NA KOYAR DA ALKUR'ANI KO A NEMA MISHI MALAMI DA ZAI RINKA KOYAR DA SHI ALKUR'ANI. KUMA A SAMAR DA KYAUTUTTUKA DA WAJE ME KYAU DON SANYA GASA TSAKANIN YARA KO DALIBAI.
3. DOLE A BIYO MAI TA HANYAR SAUKI NA YIN





HADDAR DAGA FARKO DON YA SO ABIN SOSAI. SAI A FARA MAI HADDAR DAGA JUZU'IN (AMMA) SABODA YAFI SAUKIN HADDACEWA GA YARA TUNDA AYOYIN SU GAJERU NE KUMA SURORIN BASU DA TSAWO BARE YARO YAJI KOSAWA, KUMA SURORIN SUN KUN SHI ABUBUWAN DA SUKA SHAFI RUKUNAN IMANI, DON HAKA ZASU INGANTA IMANI SU KUMA GYARA DABI'UN YARO. KUMA ZASU KIYAYE LAFIYAR YARO SU AMINTAR DA SHI DOMIN SHI ALKUR'ANI TUNATARWA NE DA KUMA MAGANI. KARI AKAN HAKA SHI NE YANA SAITA HARSHEN YARO YA IYA MAGANA YA KUMA IYA BAYANI.

4. A MAIDA HANKALI WAJEN YIMA YARO SHARHIN WASU AYOYI ATAKAICE LOKACIN DA AKE MAI TILAWA KUMA AKE HADDATAR DA SHI QUR'ANI. KADA MU JI CEWA YARO NE BASHI DA BUKATAR HAKAN DOMIN KWAKWALWAR YARO TANA DA ABIN MAMAKI WAJEN HADDA DA KUMA FAHIMTA.

5. A FAHIMTAR DA SHI CEWA ALKUR'ANI WARAKA CE KUMA RAHAMA DA ALBARKA NE A RAYUWAR MUTUM. ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA CE: {KUMA MUNA SASSAUKARWA DAGA ALKUR'ANI ABINDA YA KE WARAKA NE DA RAHAMA GA MUMINAI..} [ISRA'I: 82]. SANNAN KUMA WANDA YA HADDACE SHI KO YA HADDACE WANI YANKI DAGA CIKI TO ZAI IYA YIWA KAN SHI ADDU'A LOKACIN DA BASHI DA LAFIYA HAKA KUMA ZAI IYA WA WANDA KE TARE DA SHI ADDU'A.

## RUKUNI NA HUDU:

# IMANI DA MANZONNI



IMANI MANZONNI YA KUNSHI IMANI DA GASGANTA SU DA IMANI DA LABARAN DA SUKA ZO MANA DA SU, DA KUMA CEWA ALLAH YA ZABE SU DAGA CIKIN MUTANEN SU, DAN HANKALIN SU DA DABI'UN SU YA BANBANTA DA NA SAURAN MUTANE DON KUMA SU ISAR DA SAKON ALLAH (S.W.T). ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA CE: {BA MU AIKO WANI MANZO BA FACE DA HARSHEN MUTANENSA DOMIN YA BAYYANA MUSU.} [IBRAHIM:4], DA ACE MANZO MALA'IKA NE DA BA A FAHIMCE SHI BA, KUMA BAYA HALATTA AGARE MU MU BANBANCE TSAKANIN WADANNAN MANZONNIN, BA ZA MU YI IMANI DA WASU MU KAFIRCE MA WASU BA, SAI DAI MUYI IMANI DA SU BAKI DAYA, DUKKAN MANZONNI MASU GASKIYA NE A SAKONNIN DA SUKA ZO DA SHI, KAMAR YADDA SUKE MASU BIYAYYA GA ALLAH WAJEN YI MA AL'UMMAR SU NASIHA, BA MASU SABAWA BANE GA ABINDA SUKE ISARWA NA SAKON ALLAH, KUMA BAYA HALATTA MUYI AIKI DA WATA SHARI'A FACE SHARI'AR CIKAMAKIN ANNABAWA MUHAMMAD (S.A.W). DAGA CIKIN ABINDA YA KAMATA A DASA MA YARA A ZUCIYA GAME DA IMANI DA ANNABAWA SU NE:

1. BAYANIN CEWA ALLAH YA AIKO MA KOWACE AL'UMMA DA MANZO DAGA CIKINSU, YANA KIRAN SU ZUWA GA BAUTA MA ALLAH SHI KADAI DA KUMA KAFIRCE MA ABINDA SUKE BAUTA WA KOMA BAYAN ALLAH, KUMA DUKKANIN SU MASU GASKIYA NE MASU GASGATAWA DA BIYAYYA GA ALLAH KUMA MASU SHIRYARWA DA TSORON ALLAH KUMA AMINTATTU.



2. BAYANIN CEWA DA'AWAR SU IRI DAYA CE TUN DAGA NA FARKONSU HAR ZUWA NA KARSHENSU AKAN BAUTA DA TUSHEN TA WANDA YAKE SHI NE KADAITA ALLAH DAGA DUKKAN SAURAN ABIN BAUTA, TARE DA GASGATA HAKAN A ZUCIYA DA FADI A BAKI DA KUMA AIKI, YA KUMA KAFIRCE MA DUK ABINDA AKE BAUTA MA KOMA BAYAN ALLAH.

3. BAYANIN HIKIMAR ALLAH DA YA AIKO SU ZUWA GA MUTANE, DAGA CIKIN WADANNAN HIKIMOMIN AKWAI BAUTAR ALLAH (S.W.T) DA KADAITA SHI, HAKA SHIRYAR DA MUTANE ZUWA GA HANYA MADAIDAICIYA, DA KARANTAR DA MUTANE AL'AMURAN ADDININSU DA DUNIYARSU DA KUMA FITAR DA SU DAGA DUHU ZUWA HASKE, DAGA CIKIN TA AKWAI SHUGABANTAR AL'UMMA DA AIKATA SHARI'AR ALLAH ACIKINSU, DAGA CIKIN TA AKWAI KOYI DA SU DA TAFIYA AKAN MANHAJINSU.

4. SANIN RAHAMAR ALLAH DA KIYAYE SHI DA BAUTAR SHI, INDA YA AIKO MANZONNIN SHI DOMIN SU SHIRYAR DA SU ZUWA GA HANYA MADAIDAICIYA, DA TUNASAR DA SU AKAN GODE MA ALLAH TA'ALA AKAN WANNAN BABBAR NI'IMAR, DA SON MANZONNI DA ANNABAWA DOMIN SUN TSAYU AKAN ISAR DA SAKON SHI DA YIN NASIHA GA BAYIN SHI, DOMIN MUTANE DUK YADDA AKA BASU FAHIMTA DA HANKALI DA WAYO TO BA YADDA ZA A YI SU FI KARFIN HANKULAN SU WAJEN TSARIN ABINDA ZAI ZAMA MASLAHA GA AL'UMMA BAKI DAYAN TA HAR SU ZAMA KAMAR AL'UMMA DAYA WAJEN BAMA ME HAKKI HAKKIN SHI. MANZONNI SUNA KOYA MA MUTANE ABINDA ZAI AMFANE SU NE SU KUMA HANA SU YIN ABINDA ZAI CUTAR DA SU.

5. DASA SON MANZON ALLAH (S.A.W) A ZUCIYAR YARO DON SU IYA YI MAI BIYAYYA SU KUMA BI KOYARWAR SHI KUMA SU GIRMAMA SHI (S.A.W), DON KUMA SU FIFITA SOYAYYAR SHI AKAN TA KOWA DA SON WANDA YAKE SON SHI SU KUMA KI WANDA KE KIN SHI, DAGA CIKI AKWAI GIRMAMA SUNAN SHI DA GIRMAMA SHI A LOKACIN DA AKA AMBACI SUNAN SHI, IN ANCE MUHAMMAD SAI SU CE (S.A.W). DA YIN SALATI A GARE SHI DA GIRMAMA DUK WASU ABUBUWAN DA SUKA KEBANCE SHI DA SANIN FALALAR SHI, SHI NE YAFI KOWA JIN KAI DA TAUSAYI, DA GIRMAMA SHI AWAJEN KABARIN SHI DA MASALLACIN SHI GA WANDA YA SAMU ZIYARAR MASALLACIN SHI YA KUMA SAMU TSAYUWA A KABARIN SHI TA FUSKAR RASHIN DAGA MURYA AWAJEN.

## YAYA ZA MU KOYA MA YARO SON ANNABI (S.A.W)?

1. DOLE A TABBATAR MAI DA CEWA ALLAH TA'ALA YANA SON ANNABIN SHI (S.A.W), ALLAH YA ZABE SHI KUMA YA DAUKAKA SHI AKAN MUTANE BAKI DAYA, KUMA YA WAJABTA MU SO SHI, KUMA MU SANAR DA SHI CEWA SON ANNABI (S.A.W) YANA DAGA CIKIN ALAMOMIN SON ALLAH TA'ALA, WANDA KUMA YA SO MANZON ALLAH (S.A.W) TO YANA SON ALLAH NE SO NA GASKIYA.

2. TUNASAR DA YARO CEWA MANZON ALLAH (S.A.W) YA KASANCE RAHMA NE GA MUTANE TA HANYAR SHIRIYAR DA SU DA KUMA ISAR DA WANNAN ADDININ, KUMA ZAI KASANCE RAHAMA GA MUMINAI TA CETON SU DA ZAI YI A RANAR ALKIYAMAH.

3. KARANTAR DA TARIHIN ANNABI (S.A.W), YARO YA SAN CEWA MANZON ALLAH (S.A.W) MADUBI NE KUMA ABIN KWATANCE NE MAI GIRMA GA DUKKAN MUTANE, A FADA MUSU MU'UJIZOZAN SHI DA DABI'UN SHI MADAUKAKA DA TAIMAKON SHI GA WANDA AKA ZALUNTA DA TAUSAYIN SHI GA TALAKAWA DA KUMA WASIYYAR SHI GAME DA MARAYU, DA IRIN JIN KAN SHI GA MASU RAUNI. KUMA YA KASANCE MUN YI AMFANI DA KALAMAI DAIDAI DA FAHIMTAR YARO, DA KUMA TAKAITUWA AKAN AL'AMURA DA HANKALIN SHI ZAI IYA DAUKA, DON YA IYA FAHIMTAR SU, KUMA MU KULA DA CACCANZA HANYOYIN ISAR DA SAKON DON MU KAI GA ABINDA MUKE SO DA KUMA ABUBUWAN DA AKE BUKATA WAJEN BUNKASUWAN YARO WANDA YA DACE DA SHEKARUN DA YARO KE RAYUWA KUMA A KULA DA BANBANCIN DA KE TSAKANIN YARA TA WAJEN FAHIMTAR ABUBUWA DA SAURAN SU DA KUMA YANAYIN WAJE ZAMAN SU.

4. YARO YA GA GIRMAMA MANZON ALLAH (S.A.W) DA GIRMAMA SUNNAR SHI DA MAGANGANUN SHI TA HANYAR KOYI DA SHI DA BIN ABINDA YAYI UMJRNI DA SHI DA KIYAYE SALATI A GARE SHI DUK SANDA AKA AMBACE SHI TUN DAGA IYAYEN SHI DA WADANDA KE KEWAYE DA SHI. HANYAR DA IYAYE KE BI A AIKACE WAJEN TARBIYYAR YARO NA DAGA

CIKIN MANYAN ABIN DA KE MA YARO TASIRI DOMIN YAFI SAURIN DAUKA. YANZU A MISALI- ALOKACIN DA MAHAIFI YA ZO DA ABINDA YAKE SUNNA NE DA KUMA YIN NAFILOLI SAI YA CE MA 'YA'YAN SHI HAKA MANZON ALLAH (S.A.W) YA KASANCE YANA AIKATAWA, DOLE SUMA ZASU DAUKA. ZAMA ABIN KOYI AWAJEN TARBIYYA NA DA TASIRI SOSAI WAJEN SAMUN INGANTACCIYAR RAYUWA DA AKIDA TSAFTATACCIYA, MANZON ALLAH (S.A.W) SHI NE ABIN KOYI MAFI GIRMA DA IYAYE YA KAMATA SU RIKA KOYI DA SHI TARE DA BIN SHIRYARWAR SHI DA KUMA AIKATA SUNNAR SHI TARE DA 'YA'YANSU.

5. HADDATAR DA YARO WASU INGANTATTUN HADISAI DA SUKE NUNI AKAN CIKAR KAMALA DA KYAWUN MUSULUNCI DA ABUBUWAN DA SUKA SHAFI MANZON ALLAH (S.A.W) DA FALALAR SAHABBAN SHI. HADISAI NADA TASIRIN GASKE WAJEN DASA IMANI DA GYARAN DABI'U DA GINA ZUCIYA. KUMA ANA IYA YI MUSU MUSABAKA, AMMA YA KASANCE WADANCAN GAJERUN HADISAN MA'ANARSU A BAYYANE TAKE BA SAI AN YI DOGON SHARHI BA KUMA YA ZAMANA SUN KUNSHI WASU DABI'U NAGARI MASU MUHIMMANCI AWANNAN MATAKIN SHEKARUN NA YARO. A KULA DA YIN AMFANI DA HANYOYI MASU JAN HANKALI DA KYAUTUTTUKA DA SAKAMAKO.

6. AMBATA MUSU KISSOSHIN SAHABBAI DA YADDA MANZON ALLAH (S.A.W) YAKE GIRMAMA SU DA YADDA SUKE GIRMAMA ANNABI (S.A.W) SUKE KUMA KISHIN SHI, MUSAMMAN MA KISSOSHIN KANANAN SAHABBAI KAMAR KISSAR ANAS BIN MALIK (R.A) DA IRIN KOYIN SHI GA ANNABI (S.A.W). WATARANA WANI MADINKI YA GAYYACI MANZON ALLAH (S.A.W) DAN CIN ABINCI, ANAS (R.A) YA CE: ( SAI NA TAFI TARE DA MANZON ALLAH (S.A.W) DON CIN WANNAN ABINCIN, SAI AKA MATSOMA MANZON ALLAH (S.A.W) DA BIREDI NA ALKAMA DA KUMA ROMO WANDA AKWAI KABEWA DA NAMA BUSASSHE ACIKI, SAI ANAS (R.A) YA CE; SAI NAGA MANZON ALLAH (S.A.W) YANA BIN INDA KABEWAR TAKE ACIKIN KWANON (YANA TSINTA YANA CI), YA CE: BAN GUSHE INA SON KABEWA BA TUN DAGA WANNAN RANAR. SUMAMATA (R.A) YA CE: DAGA ANAS (R.A) YA CE SAI NA RINKA TSINTAR KABEWAR INA TURAWA GABAN SHI.) [BUKHARI: 5439]. DON HAKA MAI TARBIYYA YA KWADAITU DA YIN BAYANIN YADDA SAHABBAN SHI SUKA KASANCE SUNA SON SHI KUMA SUKE SADAUKARWA WAJEN BIN HANYAR SHI (S.A.W) DA KAWO MUSU KISSOSSHI AKAN HAKAN.

7. A SANAR DA SHI TASIRIN DA KE TATTARE DA WANNAN SON NA MANZON ALLAH (S.A.W), DAGA CIKIN TASIRIN HAKA SHI NE HADISIN DA YA ZO DAGA ANAS (R.A) CEWA WANI MUTUM YA TAMBAYI MANZON ALLAH (S.A.W) AKAN TASHIN ALKIYAMA YA CE: (YAUSHE ZA A YI TASHIN ALKIYAMA? SAI MANZON ALLAH (S.A.W) YACE: ((ME KA SHIRYA MATA?)) SAI MUTUMIN YA CE BA KOMAI, SAI DAI NI INA SON ALLAH DA MANZON SHI, SAI MANZON ALLAH (S.A.W) YA CE: ((KANA

TARE DA WANDA KAKE SO.)) ANAS YA CE: MUNYI FARINCIKI DA FADIN MANZON ALLAH (S.A.W) ((KANA TARE DA WANDA KAKE SO.)) ANAS YA CE: NI INA SON MANZON ALLAH (S.A.W) DA ABUBAKAR DA UMAR (R.A) KUMA NI INA SON KASANCEWA TARE DA SU DA WANNAN SON DA NAKE MUSU KO DA BAN YI IRIN AYYUKAN SU BA. ) [BUKHARI: 5439]

8. TAIMAKON YARO WAJEN KIRKIRAR CI GABA GAME DA ABINDA YA SHAFI SON MANZON ALLAH (S.A.W) KAMAR RUBUTA WAKE DA KISSA DA HUDUBA DA RUBUCE-RUBUCE DA SHIRYA GASA KALA-KALA DUKA AKAN ABINDA YA KEBANCI SON MANZON ALLAH (S.A.W)



## RUKUNI NA BIYAR:

# IMANI DA RANAR LAHIRA

IMANI DA RANAR LAHIRA YA KUNSHI IMANI DA CEWA AKWAI MUTUWA DA TASHI BAYAN MUTUWA DA SAKAMAKO DA HISABI DA SIRADI DA MIZANI DA ALJANNAH DA WUTA. YARO ZAI FARA TUNANIN WASU MAS'ALOLI NA RANAR ALKIYAMA BAYAN YA WUCE SHEKARUN DA YAKE IYA TANTANCE ABUBUWA SOSAI. AMMA KAFIN HAKA, ZEYI KYAU YA KASANCE MAGANGANUN DA ZA A FADA MAI SU KASANCE A TAKAICE KUMA A DUNKULE, MU BAYYANA MA YARO CEWA AKWAI RAYUWAR LAHIRA DA KUMA CEWA ALLAH YA HALICCI ALJANNA GIDAN MUMINAI, DA WUTA GIDAN KAFIRAI.

**DAGA CIKIN ABINDA YA KAMATA A TARBIYYARTAR DA YARO WAJEN DASA MAI IMANI DA RANAR LAHIRA SU NE:**

1. YARO YA SAN CEWA ALLAH ZAI TADA MUTANE RANAR LAHIRA DAGA MUTUWAR DA SUKA YI DAN A BASU SAKAMAKON AYYUKAN SU DA SUKA YI A DUNIYA, IN ALKHAIRI MUTUM YA AIKATA ZAI SAMU ALKHAIRI, IN KUMA SHARRI YA AIKATA YA SAMU SHARRI.

2. YARO YA SAN CEWA ALLAH YA SAMAR DA ALJANNA AWANNAN RANAR, ALJANNA GIDAN KARAMCI DA JIN DADI DA TABBATUWA ACIKIN TA HAR ABADA, ALLAH YA HALICCE TA DAN YA SAKA MA MUMINAI DA ITA BISA AYYUKA NAGARI DA SUKA YI, YA KUMA SAMAR DA WUTA DA AKA TANADE TA DAN KAFIRAI MASU SABAWA ALLAH. ZA A NUNA MA YARO HAKAN NE TA HANYAR KWADAITAR DA SHI AKAN IRIN NI'IMOMIN DA KE ALJANNA DA ABUBUWAN DA AKA TANADAR MA MUMINAI ACIKIN TA.

3. TATTAUNAWA DA YARO AKAN MUTUWA DA RANAR ALKIYAMA TA HANYA MAI TAUSHI DA TAKE NUNI AKAN RAHAMAR ALLAH DA GAFARAR SHI DA TAUSAYIN SHI GA BAYI SABODA KAR WASU TUNANUKA KARKATATTU SU ZO MA YARO SU DAME SHI. ANA IYA HADA HAKA, WATO BASHI LABARIN ABUBUWAN DA KE RAYE WADANDA KE WUCEWA MATAKI-MATAKI, MISALI WANE YA FARA RAYUWA TUN DAGA LOKACI KAZA GASHI YAU BA SHI YA MUTU DA IRE-IREN HAKA. SAI DAI SHI MUTUM ALLAH YA BANBANTA SHI TA

HANYAR DORA MAI NAUYE-NAUYE KUMA YA SANYA DUK HALITTU SU ZAMA MASU YI MASHI HIDIMA KUMA SHI DAN ADAM ALLAH YA MAI ALKAWARIN KYAKKYAWAN SAKAMAKO MATUKAR YA KYAUTATA, SAURAN HALITTU KUMA BASU DA WANI SAKAMAKO.

4. AYI MUSU BAYANIN CEWA ALLAH BAYA TABBATAR DA AZZALUMI KUMA BAYA BARIN AZZALUMI BA TARE DA YAYI MISHI UKUBA BA, HAKA BAYA BARIN WANDA AKA ZALUNTA BA TARE DA YA SAKA MAI BA. KUMA BAYA BARIN MAI KYAUTATAWA BA TARE DA YA SAKA MAI DA LADA BA. MU YANZU A DUNIYA MUNA GANIN WANDA KE RAYUWA AKAN ZALUNCI KUMA YA MUTU YANA AZZALUMI, DUKDA WANNAN BA MAKAWA DOLE AKWAI RAYUWAR LAHIRA BAYAN WANNAN RAYUWAR DA MUKE YI YANZU A DUNIYA WANDA ZA A SAKA MA WANDA YA KYAUTATA A KUMA YI MA WANDA YA SABA UKUBA, KUMA A BAMA KO WANE MAI HAKKI HAKKIN SHI.



## RUKUNI NA SHIDA:

# IMANI DA KADDARA



IMANI DA KADDARA YA KUNSHI CIKAKKEN IMANI DA ILIMIN ALLAH DA ABINDA YA RUBUTA TUN A LAUHIL MAHFUZ DA KADDARAR SHI DA RUBUTUN SHI DA MASHI'AR SHI, YARO A LOKACIN DA YAKE SHEKARUN FARKO BAYA IYA FAHIMTAR MENENE HUKUNCIN DA ALLAH YA YANKE DA KUMA KADDARA, WASU NA GANIN BA ZAI YIYU YA GANE MA'ANAR SU BA SAI BAYAN YA KAI SHEKARU TARA A RAYUWAR SHI. AMMA ASALIN MA'ANAR TARBIYYA YA KAMATA A DASA MA YARO ITA CIKIN ABINDA YA SHAFI HUKUNCI DA KUMA KADDARAR ALLAH. DAGA CIKIN HAKA AKWAI:

1. ABINDA YAKE ASALI A WANNAN BABIN SHI NE ABINDA YA ZO DAGA ABIL-ABBAS ABDILLAHI BIN ABBAS (R.A) YA CE: WATA RANA NA KASANCE A BAYAN MANZON ALLAH (S.A.W) SAI YA CE:(( YA KAI YARO ZAN SANAR DA KAI WASU KALMOMI, KA KIYAYE ALLAH ZAI KIYAYE KA, KA KIYAYE ALLAH ZAKA SAME SHI A GABAN KA, IDAN ZAKA YI ROKO TO, KA ROKI ALLAH KUMA IDAN ZAKA NEMA TAIMAKO TO, KA NEMA TAIMAKO WAJEN ALLAH, KA SANI CEWA LALLAI DA ACE AL'UMMAH ZASU TARU DON SU AMFANAR DA KAI WANI ABU BA ZASU AMFANE KA DA KOMAI BA FACE ABINDA ALLAH YA RUBUTA MAKA, HAKA KUMA DA ZASU TARU DON SU CUTAR DA KAI AKAN WANI ABU TO, BA ZASU CUTAR DA KAI DA KOMAI BA FACE ABINDA ALLAH YA RUBUTA AKAN KA, AN DAGE ALKALUMA KUMA TAKARDU SUN BUSHE)) [TIRMIZI: 2516]. WANNAN HADISIN ANA DAUKAR SHI A MATSAYIN MABUBBUGAR TARBIYYA WADDA TA KUNSHI NUSASSHE DA YARO ABU MAI KYAU DAGA ANNABI (S.A.W) ZUWA GA AL'UMMAR SHI WAJEN BADA MUHIMMANCI GA RAINON YARA AKAN AKIDA INGANTACCIYYA.

2. NISANTAR YAWAITA MAGANA AKAN KADDARAR ALLAH TARE DA YARO A IRIN WADANNAN SHEKARUN, ABINDA YA KAMATA A ISAR MA DA YARO SHI NE YIN BAYANI AKAN FADIN ILIMIN ALLAH DA KADDARAR SHI DA MAMAYEWAR SHI GA KOMAI DA HALITTAR SHI DA MASHI'AR SHI, ABINDA YA SO SHI YAKE AUKUWA, WANDA BE SO BA BAYA AUKUWA, TARE DA TABBATAR MAI DA 'YANCIN 'YAN ADAM. DA CIKAKKEN NAUYIN DA KE KAN SHI NA DAGA AYYUKAN SHI ZABABBU, DA HAKKIN BADA LADA GA WANDA YAYI ABIN KWARAI KO UKUBA GA WANDA YA SABA MAI. ZA A MA YARO WANNAN BAYANIN NE A DUNKULE. AMMA IDAN WANNAN YA ZAUNA A KWAKWALWAR YARO YA ZAMA YANA MAI SETI TO YA KAMATA GA MAI TARBIYYA A WANNAN LOKACIN YA FADADA MAI BAYANI AKAI TA YADDA KWAKWALWAR SHI ZATA DAUKA.

3. TARBIYYANTAR DA YARO AKAN ROKON ALLAH BA ROKON WANI BA, KUMA YA DOGARA DA ALLAH SHI KADAI, A SANAR DA SHI CEWA ITA ADDU'A ANA FUSKANTAR DA ITA NE GA ALLAH SHI KADAI, KUMA YIN TAWAKKALI DA DOGARO GA ALLAH SHI KADAI DA KUMA YIN HAKURI AKAN HUKUNCI DA KADDARAR DA ALLAH YA YANKE GA MUTUM.

4. YARO YA SAN CEWA ALLAH BE NUFIN SHI DA KOMAI FACE ALKHAIRI, SANNAN SHI YANA TAFIYA NE ACIKIN RAYUWA BISA KADDARAR ALLAH, DAN HAKA ZUCIYAR SHI BA ZATA SHIGA KUNCI BA KUMA BA ZAI KARAYA BA IN ABUBUWA SUKA FARU DA SHI. HAKAN ZAI SA IN YA FADA CIKIN TSANANI YA SAN CEWA KADDARA CE DA HUKUNCIN ALLAH AKAN SHI, YA SAN CEWA {BA ABINDA ZAI SAME MU FACE ABINDA ALLAH YA RUBUTA MANA} [ TAUBA: 51]


5. YASAN CEWA FARUWAR AL'AMURA A HANNUN ALLAH SUKE, KUMA SHI ALLAH YANA AIKATA ABINDA YASO NE YA KUMA ZABA, DOMIN SHI YANA DA IKON JUJJUYA ABUBUWA A CIKIN MULKIN SHI, WANNAN ZAI SA YA KARA DANFARUWA DA UBANGIJIN SHI DA KUMA KOMAWA GARE SHI KUMA ZAI SA YA MAIDA CIKAR BURIKAN SHI DA ADDU'O'IN SHI DA FATAN SHI GA ALLAH.

6. IMANI DA WANNAN RUKUNIN YANA TABBATAR DA NATSUWAR ZUCIYA DA KUMA AUNA ABUBUWA ACIKIN ZUCIYAR YARO, ALOKACIN DA MUMINI YAKE JIN CEWA DUKKAN ABUBUWAN DA KE FARUWA DA SHI NA ALKHAIRI KO NA SHARRI SHINE ALKAHIRI AGARE SHI, WANNAN ZAI SA YA SAMU NATSUWAR ZUCIYA DA TABBATUWA ACIKIN ZUCIYAR SHI, KUMA HAKAN ZAI SA YA FUSKANCI MATSALOLI DA WAHALHALU DA DAMUWOWIN SHI TA HANYAR MARABA DA HUKUNCIN ALLAH DA KADDARAR SHI, DAGA NAN KUMA ZAI MIKA AL'AMURAN SHI GA ALLAH YAYI RAYUWA CIKIN NATSUWAR ZUCIYA DA TUNANI. DUK WANDA YAYI IMANI DA KADDARAN ALLAH BA ZAI KARAYA BA KUMA BA ZAI YI FUSHI LOKACIN DA MUSIBU SUKA FADO MAI SAI DAI MA YA MIKA WUYA YA NEMA LADA AWAJEN ALLAH YA KUMA TUNA FADIN ALLAH GA WADANDA SUKA YI HAKURI YAYIN DA MUSIBA TA AFKA MUSU. INDA YACE: { KUMA KAYI MA MASU HAKURI BUSHARA (55) WADANDA IN MUSIBA TA FADA MUSU ZASU CE LALLAI MU NA ALLAH NE KUMA LALLAI MU GARE SHI MUKE KOMAWA (56) WADANNAN SUNA DA YABO GA UBANGIJIN SU DA RAHMA KUMA WADANNAN SUNE SHIRYAYYU.} [BAKARA: 155-157 ]


7. ANA IYA BASHI HIKAYOYI DA KISSOSHI NA ABUBUWAN DAMUWA DA SUKA FARU DA WASU NA KADDARAN ALLAH, SANNAN A BAYAN HAKA ALKAHIRAI SUKA SAME SU TA DALILIN KUNCIN DA SUKA SHIGA SUKA YI HAKURI DA KADDARAN ALLAH. AL'AMURAN SU SUKA CANZA ZUWA MAFI KYAWU DUKA ADALILIN HAKAN.

8. A MAI BAYANIN IMANI DA KADDARA A TAKAICE AKAN CEWA ALLAH YA SAN KOMAI A DUNKULE DA RARRABE, YA RUBUTA DUKKAN ABUBUWAN DA ZASU FARU ACIKIN LAUHIL MAHFUZ WANDA YA RIGA YA SAN SU TUN KAFIN YA RUBUTA SU NA DAGA ABUBUWAN DA ZASU FARU GA HALITTUN SHI TUN RANAR DA AKA HALICCE SU HAR ZUWA RANAR TASHIN ALKIYAMAH. KUMA DUKKAN HALITTU DA SAURAN ABUBUWA BA SA KASANCEWA FACE SAI DA NUFI NA ALLAH.






# AMSAR TAMBAYOYI



# LALLAI

LALLAI ALLAH MAHALICCI-MADAUKAKI - YA CUSA WA YARO SON BINCIKE; DOMIN HANKALINSA CIKAKKIYAR FAHIMTA DA BAYANAI, YARINTA ITA CE MATAKIN BINCIKE, KASANCEWAR KUSAN YAWANCIN MAGANGANUN YARO A WANNAN MATAKIN TAMBAYOYI NE, DON HAKA YARA SUNA JIN CEWA BASU SAN KOMAI GAME DA ABUBUWAN DA KE KEWAYE DA SU BA, KUMA TUN DA JAHILCI YANA HAIFAR DA TSORO; SUNA HANZARIN KOYO DA DUKKAN KARFINSU, DON HAKA MUKAN SAMI YARO ƊAN SHEKARA UKU YANA TAMBAYAR IYAYENSA DA MANYAN ‘YAN UWANSA TAMBAYOYI DA YAWA A KOWACE RANA, KUMA BABU WATA SHAKKA CEWA AMSOSHINSU SUNA SHAFAR SHI, DA SAUYAWA DAGA WANNAN JIHAR ZUWA WATA DANGANE DA SHAIDAR CANZA TSARIN TAMBAYA DA KUMA MAS’ALOLIN DA AKE MAGANA AKAI AKAI, A KULLUM ZAKA JI KALMOMI DAGA GARE SHI KAMAR: MENENE? INA YA KE? TA YAYA WANNAN YA FARU? DAGA INA YA FITO? MENENE? WACECE? SHIN KA SAN? YANA SO YA SAN DUK ABUBUWAN DA SUKE JAN HANKALINSA, YANA SON FAHIMTAR ABUBUWAN DA YA GANI KUMA YA JI GAME DA SU, ZAI IYA FAHIMTAR AMSAR, WATAƘILA BAI FAHIMCE TA BA, YANA IYA JIRAN AMSA NA ISASSHEN LOKACIN, KUMA BA ZAI SAURARA BA.

YARON YA BAMBANTA DA SON SANI, KUMA WANNAN NA IYA ƘARUWA GWARGWADON YANAYIN INDA YAKE RAYUWA, KUMA GWARGWADON DAMAR DA YAKE DA ITA, KUMA DON HAKA; ZA MU YI MAMAKI IDAN MUKA KWATANTA TAMBAYOYINMU A YARINTARMU DA NA SU A YAU; SABODA BANBANCIN LOKACI, WURI DA KUMA CI GABAN KIMIYYA, BABU WATA TANTAMA CEWA HANYAR ILIMANTARWA DA MASU ILMANTARWA SUKE AMFANI DA ITA KARARA TANA SHAFAR FADADAWA KO RIKITA BATUN AL'AMARIN TAMBAYOYIN YARA. MAI TARBIYYAR DA KE BA DA DAMA KUMA CIKIN FARIN CIKI YANA KARƁAR ABIN DA YARA SUKE TAMBAYA, KUMA YA TSUNDUMA CIKIN TUNANINSU, YAYIN DA WANDA BAYA HAƘURI DA TAMBAYOYIN SU KUMA YA ƘI SU KO YA YI MUSU IHU BA ZAI SAMI WANDA ZAI TAMBAYE SHI WANI ABU BA, KUMA DUK DA CEWA MUN YARDA CEWA YIN HAKAN BA MASLAHA BANE KO KARƁAƁBEN ABU GA YARA A CE SUN SAN KOMAI, AMMA YANA DA MAHIMMANCI: KADA YARA SU JI TSORON TAMBAYA GAME DA WASU LAMURAN DA SUKA SHAFI RAYUWARSU, KUMA YANA DA MAHIMMANCI YARA KADA SU JI CEWA KAMAR BASA NAN KO KUMA ANA BOYESU, KUMA SU BA ABIN AMINTA BA NE, KUMA MAFI MAHIMMANCI: YA KAMATA SU JI DADIN MAGANA DA AHALINSU.

## DALILAN YAWAITAR

# TAMBAYOYIN YARA



**MAFI MAHIMMANCIN DALILAI DA SUKE SA YARO YAYI TAMBAYA MAI YAWA ZA A IYA TAƘAICE SU KAMAR HAKA:**

1. KWADAYIN YARO WAJEN SON YA YI BINCIKE DA GANOWA A MATSAYIN HANYAR BIYAN BUƘATUN CI GABAN HANKALI.
2. BUKATAR YARA ZUWA GA SU FAHIMCI DUK WASU ABUBUWA DA SUKA DABAIBAYE SU.
3. DAMUWA DA TSORON YARA, DA KUMA; RASHIN ƘWAREWAR DA TA GABATA A RAYUWARSHI, MISALI: YARO YANA TSORON DABBOBI KO DA KUWA BA SU KAWO MASA HARI BA, DON HAKA; YANA TAMBAYA KUMA YANA YAWAITA TAMBAYA DOMIN YA SAMI KWANCIYAR HANKALI.


4. BUNKASAR ILIMIN HARSHE NA YARA, IDAN YA DINGA JERO TAMBAYOYI DAYA BAYAN DAYA; WANNAN BA WAI DON SUNA SHA'AWAR NEMAN AMSA BANE FACE SHA'AWAR SA NA YIN YARE DA NUNA ƘWAREWARSA DA KUMA BUƘATUN SA NA ZAMAN JAMA'A.

5. DAMAR SADARWAR DA TARAYYA DAABINDA KE ZUCIYA TSAKANIN IYAYE DA YARA.

6. INGANTA AMINCEWAR YARO GA KANSA DA IYAYENSA DA KUMA GIRMAMA SHI.

## YANAYIN TAMBAYOYI

## A GURIN YARA



DOMIN FAHIMTAR TAMBAYOYIN YARO DA KYAU; DOLE NE MU RARRABE TSAKANIN TAMBAYOYIN HANKALI DA NA YARE, DA TAMBAYOYIN TUNANI. GANIN CEWA A NAU'I NA FARKO YARO YANA KOKARIN SANIN WANI ABU, KO KUMA MAGANA GAME DA WANI ABU, KUMA A NAU'I NA BIYU, MURADINSA SHI NE TABBATAR DA HALAYYAR MUTUM, KUMA AMSAR BA TA NUFIN SHI DA KANTA, KUMA YA ZAMA DOLE A TABBATAR DA WATA HUJJA TA ASALI, WANDA ITA CE: CEWA TAMBAYOYIN SUNA DA MAHIMMANCI, SABODA HAKA BA ZAMU IYA KIMANTA DARAJAR TAMBAYAR BA, KO FAHIMTAR TA DA MA'ANARTA BA, SAI DAI TA HANYAR TAKAMAIMAN HALIN DA YA SA YARON YIN TAMBAYAR, DOMIN TAMBAYA BATA DA WATA KIMA A KARAN KANTA, AMMA TANA SAMUN ƘIMA, MUHIMMANCI NE YAYIN DA TA DACE DA YANAYIN DA KE KEWAYE DA SHI DA KUMA HALIN DA YAKE CIKI .. TAMBAYOYIN YARA SUNA DA MAHIMMAN AYYUKA GUDA UKU, SU NE:

1. CIMMA DAIDAITUWAR HALAYYA GA YARO, KAMAR YADDA MAFI YAWANCIN TAMBAYOYIN YARON DAGA ZUCIYARSHI SUKE

2. TUNANIN FITAR DA WANI ABU, INDA YARO KE KOKARIN ISA GA SABON ILIMI, DOGARO DA WADATAR BAYANAN DA YA GINU KO KUMA YA KULLA ALAKAR SU.

3. KOYO GAME DA YANAYIN DA KE KEWAYE DA SHI, DA MAHIMMAN LAMURRAN RAYUWA; CIKI HAR DA GANO ƊABI'U DA HALAYYA DA KE CIKIN TSARIN AL'ADU DA ZAMANTAKEWAR DA YARO KE RAYUWA A CIKI.

## NAU'IN

# TAMBAYOYIN YARA





YANA DA AMFANI A YI KOKARIN RARRABA TAMBAYOYIN DA YARA SUKE YI, KAMAR YADDA AMSOSHIN WAƊANNAN TAMBAYOYIN SUKA BAMBANTA GWARGWADON BANBANCINSU, KUMA ZA A IYA RARRABA TAMBAYOYIN YARA A CIKIN WAƊANNAN RUKUNONI MASU ZUWA:

1. TAMBAYOYI NA DABI'AR HARSHE: KAMAR: ME YASA AKA SANYAWA ABUBUWA WADANNAN SUNAYEN? ME YASA BAZA MU CANZA LAKABI BA? ME YA SA BA ZAMU KIRKIRI WANI HARSHEN BA?
2. TAMBAYOYI NA SAMUWA: KUMA A CIKIN SU AKWAI TAMBAYOYI: DAGA INA MUKA ZO? INA ZA MU? TA YAYA AKE SAMUN YARA? ME AKE NUFI DA MUTUWA? DUNIYA FA? ... DA DAI SAURANSU
3. TAMBAYOYI NA TAWAYE: SUN TA'ALLAKA NE DA RA'AYI: ME YASA BA A YARDA YARA SU YI ABIN DA AKA YARDA MANYA SU YI BA? SUNA ZUWA NE TA HANYAR YUNƘURIN KWAIKWAYON MANYA MAIMAKON TA HANYAR TAMBAYOYI.
4. TAMBAYOYIN GWAJI: WADANNAN TAMBAYOYI NE DA YARA SUKE YI DON GWADA IYAWAR IYAYE DA KUSHE ABIN DA SUKE GANI RAUNIN IYAYEN NEWANNAN NA DA ALAKA DA TAKWARORIN YARON, KUMA WAƊANNAN TAMBAYOYIN GALIBI SUNA KASANCEWA NE GAME DA HALIN IYAYEN NA DUKIYA DA KUMA JIKINSU.

5. TAMBAYOYIN DAMUWA NA ƘURUCIYA: YARA SUNA YIN TAMBAYOYIN DA KE MAYE DAMUWAR DA SUKE CIKI, KUMA DAGA CIKIN TAMBAYOYIN DAMUWA DA KE YAWAITA A CIKIN YARA: TAMBAYOYI GAME DA RASHI MAHAIFA KO WASU ALAMU NA YIN WATSI DA SU.

6. TAMBAYOYIN BINCIKEN JIKI: A SAMAN TAMBAYOYIN DA YARO YA GABATAR A MATSAYIN HANYAR BINCIKE SUNE: TAMBAYOYI MASU ALAƘA DA BAMBANCIN ZAHIRI TSAKANIN JINSIN MACE DA NAMIJI.

IRIN WANNAN NA IYA TAIMAKA WA IYAYE SU FAHIMCI ASALIN TAMBAYAR DA 'YA'YANSU SUKE GABATARWA, BA WAI SUNA YIN WAƊANNAN TAMBAYOYIN BA NE SABODA KARAN KANSU , SAI DAI KAWAI SUNA YIN SU NE A DON KOKARIN FAHIMTA.

## ME YASA IYAYE SUKE YIN BIRIS DA TAMBAYOYIN YARA?!

YIN WATSI DA TAMBAYOYIN YARA DA KAMEWA DAGA GARE SU WANI LOKACI BA SHI DA NASABA DA KARANCIN ILIMIN AMSAR DA MAHIMMANCIN TA, DA KUMA RASHIN SANIN MATSAYIN TA NA TUNANI DA ILIMI, AMMA HAKAN NA FARUWA NE SABODA WASU DALILAI, WATAKILA MAFIYA MAHIMMANCINSU SU NE:

1. JIN BANBARAKWAI GAME DA TAMBAYAR YARON, KO RASHIN KIMA KO RASHIN KULAWA, HAKAN YA SANYA SHI BA SHI DA SHA'AWA KO RASHIN KULAWA DA SHI; MANYA NA FAƊAWA CIKIN RAMI NA ƘETARE HAƘƘIN YARA DON YIN TUNANI TA HANYAR SU, WANDA KE TATTARE DA SAUƘI DA TSABTA, KUMA WANNAN ƘETARE WAKILTAR WANI NAU'I NE NA KAKA-GIDA A TUNANI WANDA MANYA KE YI, SUNA MANTAWA DA CEWA YARON YANA YIN TAMBAYOYIN MASU SAUƘI NE DOMIN YANA SO YA FAHIMTA DA SON SAMUN ILIMI, KO GANO DUNIYAR DA KE KEWAYE DA SHI. GAME DA MAƘASUDIN TUNANIN GAGGAWA NA TAMBAYARSA; MAIDO DA DAIDAITACCEN TUNANIN YARON YA KUDURCE GAME DA WANI ABU.

2. SANIN MANYA GAME DA WAHALAR TAMBAYAR DA YARO YAKE YI; LOKACIN DA TAMBAYA TAKE DA ALAƘA DA WANI ƁANGARE NA ZAMANTAKEWAR JAMA'A KO ƊABI'A A CIKIN WANI TSARIN AL'ADU, WANDA BA A YARDA A YI MAGANARSA BA SAI A WASU SHEKARU. WAHALAR TAMBAYOYIN YARA YANA SA MANYA JIN KUNYA SU RIKICE, KUMA DAGA NAN YA ZAMA DOLE GA MANYA SU SHIRYA KANSU DA KYAU, WANDA HAKAN ZAI BA DA GUDUMMAWA GA WAJEN BADA INGANTACCIYAR AMSA GA WAƊANNAN TAMBAYOYIN.

**3.** TAMBAYOYIN DA YARA SUKE YAWAN YI, KUMA YAWAN YIN SU LOKACI BAYAN LOKACI DALILI NE NA SAKACI DA YAKE BAYYANA DAGA WURIN MANYA, KUMA IDAN MANYA SUKA FAHIMCI MAHIMMANCIN TAMBAYOYIN YARA TA MAHANGAR TUNANINSU, ZASU SAMI WATA MATSAYA WADDA ITA CE KARFAFAWA DON YARA SU CI GABA DA YIN TAMBAYOYINSU, KAMAR SUNA YIN TUNANI DA MURYAR DA AKE JI.

**4.** DAGA CIKIN DALILAN DA YASA MANYA BA SA KULAWA DA TAMBAYOYIN YARA DAIDAI GWARGWADO SHI NE CEWA WASU DAGA CIKIN WADANNAN TAMBAYOYIN SUNA ZUWA A FAKAICE BA KAI TSAYE BA.

**5.** KAUCEWAR IYAYE GAME DA AMSAR YARA NA IYA ZAMA SABODA RASHIN SANIN ABIN DA YARA SUKE SO SU SANI NE, DON HAKA MUKE CE MUSU: YA KAMATA KU NEMI AMSAR TAMBAYOYIN YARANKU, KUMA KU GAYA MUSU GASKIYA DA GASKIYA.

**6.** TAMBAYOYIN YARA SUN WUCE IYAKOKIN HANKALINSU NA KWAKWALWA WAƊANDA KE BUƘATAR AMSOSHI WAƊANDA BA SU DA MATSALA KUMA SUNA DA WAHALA, DON HAKA IYAYE ZA SU FARA TUNANIN YADDA YARO YA ISA ZUWA GA WANNAN TAMBAYAR, SAI SU YI WATSI DA AMSAR TA.



## YAYA IYAYE ZA SU YI MA`AMALA DA TAMBAYOYIN YARA?

SU HALITTA CE DAGA CIKIN HALITTUN ALLAH, AN HALICCE SU NE DAGA HASKE, ALLAH YA HALICCE SU NE KAFIN MUTANE, SUNA DA NUFI, DA TUNANI DA FUKA-FUKAI, KUMA YANAYIN HALITTARSU NA DA KYAU, KUMA SUNA DA IKON KWAIKWAYON SURAR MUTANE, BA SA CI BA SA SHA, KUMA SU BAYIN ALLAH NE WADANDA SUKE AIKATA ABIN DA AKA UMARCE SU, KUMA MATSAYI-MATSAYI SUKE DA SHI , SHI JIBRILU AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI - AN BA SHI AIKIN ISAR DA WAHAYI GA MANZANNI - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SU - KUMA AKWAI MIKAEL, ISRAFIL DA SAURANSU, DAGA CIKINSU AKWAI MASU KULA WAƊANDA AKA ƊORA WA ALHAKIN KIYAYE AYYUKAN BAYI A KOWANE LOKACI, KUMA AKWAI ADADI MAI YAWA NA MALA`IKU, KUMA KOWANE DAGA CIKIN MALA`IKU YANA DA AIKINSA WANDA DOLE NE YA AIWATAR DA SHI.

## YAYA SUNAYEN MALA'IKU?

MALA'IKU NA DA YAWA, KUMA ALLAH - MAI ALBARKA DA DAUKAKA - NE KADAI YA SAN ADADIN SU. DAGA CIKIN SUNAYEN SU: JIBRIL, MIKA'ILU, ISRAFIL, RADWAN, DA MALIK.

- AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SU -, KUMA AKWAI MASU RIKE DA AL`ARSHI, DA MASU KIYAYE AYYUKAN BAYI, DA SAURANSU.

## SABODA ME ALLAH YA HALICCE SU?

ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA HALICCI MALA'IKU. DON AIKATA ALHERI, GABA DAYANSU ALHERI NE BASA AIKATA MUGUNTA BASU MA SANTA BA, KUMA MALA'IKU TUN ASALI SUNA SAMA, SAI DAI SAUKOWAR MUTUM ZUWA DUNIYA YA SANYA DOLE NE SAUKOWAR MALA'IKU ZUWA GURINSUDOMIN YIN WASU AYYUKAN DA ALLAH YA UMURCE SU DASU, NA DAGA KIYAYEWA, KULAWA, LURA, SADARWA, TAIMAKAWA, NEMAN GAFARA, HALARTAR TARUKAN ZIKIRI, DA SAURAN AYYUKA, KUMA ANA IYA FADAWA YARO CEWA MALA'IKU SUNA DA MANYAN AYYUKA GUDA BIYU : BAUTA WA ALLAH MADAUKAKI, DA TAFIYAR DA AL'AMURAN DUNIYA.

## ME YASA BAMA GANIN MALA'IKU?

'YAN ADAM BA SU DA IKON GANIN MALA'IKU A CIKIN SURAR DA ALLAH YA HALICCE SU, SABODA HAKA; MALA'IKU SUNA ZAMA SURAR MUTUM; DON MUTANE SU GANSU SU YI MU'AMALA DA SU, KAMAR YADDA MALA`IKA JIBRILU - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI YA ZO A SIGAR BALARABE, KAMAR YADDA YAKE A HADISIN KARANTAR DA AL'AMURAN ADDINI.

## SU WAYE ALJANU?

HALITTA CE DAGA CIKIN HALITTUN ALLAH, ALLAH YA HALICCE SU DAGA WUTA, KUMA AN DORA MASU NAUYIN YIN BIYAYYA GA UMARNI DA HANI, KUMA SU HALITTA NE DA KE MUTUWA KAMAR SAURAN HALITTU, BA ZA MU IYA GANIN SU BA KUMA BA MU DA IKON YIN HAKAN, KUMA ALLAH YA HALICCE SU DA ABUBUWAN DA SUKA BAMBANTA DA NA MUTUM, DON HAKA ZA SU IYA TASHI, SU YI SAURI, KUMA SU IYA SAUYAWA, KUMA HALITTAR ALJANU TA BANBANTA DA TA MUTANE. DOMIN AN HALICCI MUTANE DAGA YUMBU, ALHALI KUWA ALJANI AN HALICCE SHI NE DAGA WUTA.

## WANENE YA FI KARFI: MALA'IKU KO ALJANNU?

MALA'IKU HALITTACE MAI ZARCEWA, KUMA BASA MUTUWA HAR SAI RANAR DA ZA A BUSA KAHO, AMMA ALJANNU, SUNA MUTUWA GABANIN HAKAN, SABODA SUN KASANCE A HAKA. MALA'IKAN MUTUWA SHI NE WANDA YAKE KARBAR RAYUKA DA UMARNIN ALLAH MADAUKAKIN SARKI IDAN YA YANKE HUKUNCIN MUTUWARSU: (ALLAH YANA KARBAR RAYUKA YAYIN MUTUWARSU) (AZ-ZUMAR: 42), DON HAKA MALA'IKU SUN FI KARFI A WANNAN BANGARE, KUMA KODA A RAYUWAR DUNIYA CE. ALJANU SUNA TSORON MALA'IKU, KAMAR A YAKIN BADAR LOKACIN DA SHAIDAN YA GA MALA'IKUN DA ALLAH YA AIKO DON TALLAFAWA MUMINAI. YA CE WA KAFIRAI: "NI BARRANTACCE NE DAGA GARE KU, DOMIN NA GA ABIN DA BA KWA GANI NA JI TSORON ALLAH KUMA ALLAH MAI TSANANIN UKUBA NE" (AL-ANFAL: 48)

## SHIN MALA'IKU SUNA MUTUWA?

E, MALA'IKU HALITTA CE DAGA HALITTAR ALLAH, KUMA KOMAI YANA MUTUWA FACE ALLAH - TSARKI YA TABBATA A GARE SHI DA BUWAYA - DOMIN SHI RAYAYYE NE KUMA TSAYAYYE, (KOMAI MAI MUTUWA NE FACE FUSKARSA) (ALKASAS: 88). DON HAKA DUK MUTANEN DUNIYA ZASU MUTU, HAKA MA NA SAMA ZASU MUTU SAI WANDA ALLAH YASO, KUMA BABU WANDA ZAI WANZU SAI ALLAH MADAUKAKI, DOMIN SHI RAYAYYE NE WANDA BAYA MUTUWA.

# TAMBAYOYI DA SUKA

# SHAFI LITTATTAFAI

## WADANNE NE LITTATTAFAN DA ALLAH YA SAUKAR?



LITTATTAFAI NE WADANDA ALLAH YA SAUKAR DA SU GA MANZANNIN SHI, TSIRA DA AMINCI SU KARA TABBATA A GARE SU. DON SU ISAR DA SAƘO DA HUKUNCE-HUKUNCEN DOKOKI, DON SHIRIYA NE GA HALITTA KUMA RAHAMA CE A GARE SU. DAN SU RABAUTA A DUNIYA DA LAHIRA, WADANDA LABARI YA SAME MU CEWA: ALLAH YA SAUKARWA IBRAHIM - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI - TAKADDU, DA KUMA ANNABI DAUDA - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI AN BASHI - ZABURA, KUMA ANNABI MUSA - AMINCI YA TABBATA A GARE SHI AN BASHI - ATTAURA, ANNABI ISA - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI - KUMA AN BASHI -INJILA, DA KUMA ANNABINMU MUHAMMAD - ALLAH YA YI TSIRA A GARE SHI KUMA AN BASHI - ALQURANI.

## ME YASA MUKE BUKATAR ALQURANI? KUMA ME YASA KUR'ANI YA KASANCE MU'UJIZA TA HAR ABADA?

IDAN INJI MAI SAUƘI DA ƊAN ADAM YA KERA YANA BUƘATAR LITTAFIN JAGORA WANDA KE KOYA MANA YADDA ZA MU YI AMFANI DA SHI DA KYAU; TO MUTUM - WANDA HALITTAR ALLAH NE - YANA BUKATAR LITTAFIN SHIRIYA DA SHIRYARWA WANDA KE KARANTAR DA SHI HANYAR CIN NASARA, CI GABA DA ADALCI A DUNIYA DA LAHIRA. ALLAH MADAUKAKI YA CE: (SHIN BAI SAN WANDA YA YI HALITTA BA, SHI MAI TAUSASAWA NE KUMA MASANI) (MALIK: 14). KASANCEWAR ALKUR`ANI MU`UJIZA CE SABODA ANNABI MUHAMMAD - TSIRA DA AMINCI SU TABBATA A GARE SHI - SHI NE KARSHEN ANNABAWA, SABODA HAKA DOLE NE MU'UJIZARSA TA CI GABA DA KASANCE HAR ABADA. SABODA BABU WANI ANNABI A BAYANSA, TILAS NE HUJJA KAN HALITTA TA KASANCE A TSAYE KUMA KALUBALEN DOLE NE YA CI GABA HAR TASHIN KIYAMA, KUMA HUJJOJIN MU'UJIZAR ALKUR'ANI SUNA DA YAWA MATUKA, MAFI MAHIMMANCI DAGA CIKINSU

SHI NE GAGARA TA FUSKAR HARSHE DA MAGANA, WANDA SHINE ABIN DA ALLAH YA KALUBALANCI LARABAWA WADANDA SU NE MAGABATA WAJEN IYA BAYANI DA KAIFIN HARSHE CEWA SU KAWO IRIN WANNAN ALKUR'ANI MAI GIRMA, KUMA WANNAN ALAMA CE TA ASALIN ALKURANI CEWA DAGA ALLAH YAKE.

## ME YASA ALLAH BAIYI ALKAWARIN KIYAYE LITATTAFAN DA SUKA GABATA BA?

ALLAH - MADAUKAKI - YANA AIKATA ABIN DA YA GA DAMA, KUMA YANA DA HIKIMA DA MUKA SAN WASU DAGA CIKINSU KUMA BA MU SAN WASU BA, AMMA BAYYANANNUN HUJJOJI SUN NUNA CEWA LITTATTAFAN DA SUKA GABATA BA MU'UJIZA BA NE, DON HAKA BA A BUKATAR CI GABANSU, HUKUNCINSU NA ƊAN LOKACI NE DON WASU MUTANE IYAKANTATTU.

## MECECE HUJJAR CEWA BA ABINDA YA CANZA DAGA KUR'ANI?

IRIN WANNAN TAMBAYAR GALIBI WAƊANDA SUKE MAKARANTAR SAKANDARE NE DA GABANTA NE KAWAI SUKE GABATAR DA ITA, SABODA HAKA; YA KAMATA MU YI MASA BAYANI CIKIN NUTSUWA DA MAHANGAR HANKALI DA KE TABBATAR DA INGANCIN KUR'ANI, DON HAKA SAI MU CE MASA: IDAN ABUBUWA SUN MAIMAITA TABBATA SUKE YI, KUMA IDAN SUKA YADU SUKAN TABBATA, TO ALKUR'ANI «AN RAWAITO SHI NE TA HANYAR TAWATIRI, SAI MU YI MASA BAYANIN MA'ANAR TAWATIRI- WANDA SHI NE ISAR DA SAKO DAGA WATA JAMA`A WACCE BA ZATA HADU WAJEN YIN KARYA BA – WANDA MALAMAI DA GAMA-GARI KOWA YA SAN WANNAN SAKON. KUMA MUSULMAI SUKA GAJE SHI DAGA ZURIYA ZUWA ZURIYA, SUNA NAZARIN SA A CIKIN TARON SU, SUNA KARANTA SHI A CIKIN ADDU'O'IN SU, KUMA SUNA KARANTAR DA SHI GA YAYAN SU, KODA KUWA A CEWA WANI DATTIJO MAI DARAJA DA GIRMA, IDAN YAYI KUSKURE A CIKIN SAKON, WANI YARO ZAI MARTINI A GARE SHI TUN KAFIN MANYA HAR SAI YA ISO ZUWA GARE MU TSARKAKAKKE DAGA ƘARI, ABIN KAREWA DAGA TAWAYA DA KUMA CANJI, KODA KUWA ZA A IYA MUSUN WANNAN DALILIN; DON KAIWA GA MUSUN TABBATATTUN HUJJOJI, KAMAR SAMUWAR ANNABI DA SAHABBAI MASU DARAJA, DA WADANDA SUKA SHAHARA A TARIHI, TO DUKKAN MASU HANKALI BA ZASU KARBI WANNAN BA, HAKA KUMA, A CIKIN KUR'ANI ALLAH YA KALUBALANCI MUTANE DA ALJANNU SU ZO DA WANI ABU MAKAMANCIN SA KUMA AMMA SUKA KASA, KUMA KUR'ANI DUK DA YAWANSA BA SHI DA WANI SAƁANI, KO CIN-KARO KO TAWAYA, SABODA ABIN DA YA ƘUNSA NA MU'UJIZOZI A LABARAI, DA DOKOKI, DA HUKUNCE-HUKUNCE DA MAGANGANU .. YANA NUNA CEWA BABU WANI CANJI DAGA MUTANEN DA AIKINSU DA MAGANGANUNSU SUKE CANZAWA. TO SHI DAGA ALLAH YAKE, KUMA ALLAH YA NE YA DAU GABARAR KIYAYE SHI..

# TAMBAYOYI AKAN MANZANNI

## SU WAYE ANNABAWA DA MANZANNI?

SU MUTANE NE DAGA CIKIN'YAN ADAM, ALLAH YA SAUKAR MUSU DA ANNABCI KUMA YA UMURCE SU DA ISAR DA SAKO GA MUTANENSU, KUMA YA KIRA SU ZUWA GA BAUTAR ALLAH SHI KADAI, NA FARKONSU SHI NE ANNABI ADAM - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI - KUMA NA KARSHEN SU SHI NE ANNABI MUHAMMAD ((S.A.W)) - KUMA SUNA DA YAWA. DOMIN ALLAH YA AIKE SU ZUWA GA DUKKAN AL'UMMAR DUNIYA DA SUKE RAYE A KANTA, KAMAR YADDA A KOWANE MATAKI NA TARIHI AKWAI WANI ANNABI DAKE KIRAN MUTANENSA YANA SHIRYAR DA SU HANYAR SHIRIYA.

## ME YASA ALLAH YA AIKO MANZANNI?

ALLAH YA AIKO MANZANNI; RAHAMA GA MUTANE DA SHIRIYA A GARE SU DA ISAR DA SAKON UBANGIJINSU ZUWA GARE SU, DOMIN MANZO MUTUM NE WANDA MUTANENSA SUKA SAN SHI KWARAI DA GASKE SUKA KUMA YI MASA SHAIDA NA ALHERI KAFIN A SAUKAR DA WAHAYI ZUWA GARE SHI, KUMA ALLAH YA SANYA MANZANNI SU ZAMA ABIN MISALI GA MUTANE, YANA KARANTAR DA SU HALAYE DA DABI`U, SUNA BAYYANA MUSU ABIN DA ZAI AMFANE SU KUMA NISANTAR DA SU DAGA ABIN DA ZAI CUTAR DA SU, DON HAKA AIKO MANZANNIN DON SU KAFA HUJJA GA HALITTU SUNA HADA MUTANE AKAN ADDINI DAYA, WANDA SHI NE BAUTAR ALLAH SHI KADAI, DON HAKA MUTANE SUNA BUKATAR MASU SHIRYARWA DA ZA SU SHIRYAR DA SU ZUWA GA HANYA MADAIDAICIYA DA KUMA YARENSU, SABODA HAKA; ALLAH YA SAUKAR DA LITTATTAFAI GA WADANNAN MANZANNI DA YAREN MUTANENSU, DON A ISAR DA SAKON A FILI.

## SHIN ANNABAWA MA'ASUMAI NE?

ANNABAWA BANGARE NE NA MUTANE, KUMA SUNA DA DUKKAN WASU MA'ANONI NA MUTANE. ALLAH NE YA KARE SU GAME DA ABINDA YAKE DA ALAKA DA SAKON DA YA BASU, KUMA YA KARE SU DAGA ABINDA ZAI YI BATANCI CIKIN HALAYENSU KO KYAWAWAN DABI'UNSU, DON SU ZAMA KYAKKYAWAN MISALI GA MUTANE SU KUMA GAMSU DA MAGANGANUNSU DA AYYUKANSU, KUMA DON KADA A SAMI HANYAR SHIGAR ƁATANCI CIKIN ISAR SAKONSU, AMMA - DUK DA WANNAN – SUMA MUTANE NE WAƊANDA SUKAN IYA FAƊAWA CIKIN KUSKURE NA AL'ADA HAKAN BA ZAI CUTAR DA SAKONSU BA, KAMAR SU: KUSKUREN KIMANTA WURI MAFI DACEWA GA AIKIN GONA KO YAKE-YAKE, KO KIMANTA GURIN DA YA KE KWADAYIN DA`AWA.

## WANENE ANNABI MUHAMMAD, AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI?

SHI NE KARSHEN ANNABAWA DA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA AIKO WA BAYINSA, KUMA SUNANSA SHI NE: MUHAMMAD BIN ABDULLAH BIN ABDUL MUTTALIB AL-HASHEMI AL-QURASHI, AN HAIFE SHI NE A MAKKA RANAR LITININ A CIKIN WATAN RABI 'AL-AWWAL A SHEKARAR GIWA, MAHAIFINSA YA RASU ALHALIN YANA CIKIN MAHAIFIYARSA, MAHAIFIYARSA KUMA TA RASU YANA DA SHEKARA SHIDA, SAI KAKANSA ABDULMUDDAIB YACI GABA DA RAINONSA SHI MA YA RASU SHEKARUN MANZO - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI TAKWAS SANNAN BAFFANSA ABU TALIB YA DAUKI NAUYINSA, ANA CE MASA MAI GASKIYA DA AMANA. YA KASANCE MAI KYAWAWAN HALAYE - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI -, AN AIKO SHI YANA DA SHEKARU ARBA'IN, KUMA YA TASHI YANA KIRAN MUTANENSA A MAKKA TSAWON SHEKARU GOMA SHA UKU ZUWA GA MUSULUNCI, SANNAN LOKACIN DA CUTARWARSU TA TSANANTA SOSAI. YA YI KAURA ZUWA MADINA YA ZAUNA A CAN NA TSAWON SHEKARU GOMA, YA KULLA YAN`UWANTAKA TSAKANIN MASU HIJIRA DA MUTANEN MADINA, KUMA YA KAFA DOKA DA HUKUNCIN ALLAH, KUMA YA RASU A SHEKARA TA GOMA SHA DAYA TA HIJIRA BAYAN YA ISAR DA SAKO KUMA YA SAUKE AMANA.

## MENENE HUJJAR TSARKIN GASKIYAR MANZON ALLAH - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI?

HUJJOJIN ANNABCIN ANNABI MUHAMMADU - SALATIN ALLAH DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI - SUNA DA YAWA, MAFI MAHIMMANCI DAGA CIKINSU SHI NE ALKUR'ANI MAI GIRMA. WANNAN LITTAFIN MAI BAN AL'AJABI YANA CI GABA DA BA MUTANE MAMAKI DAGA TSARA ZUWA TSARA DA TASKARSA DA LU'LU'UNSA WADANDA KE BIRGE HANKALIN MUTANE. DAGA CIKIN HUJJOJIN GASKIYARSA ITA CE: TARIHIN RAYUWARSA DA KYAWAWAN HALAYENSA WADANDA ABOKAN GABANSA SUKA BAYYANA KAFIN MASOYANSA, DON HAKA AKE KIRANSA DA AL-AMIN MAI GASKIYA, KUMA DAGA CIKIN ALAMUN TGASKIYARSA: IT ACE SHARI`AR MUSULUNCI WACCE TAKE CIKE DA KAMALA DA KYAU, KUMA DAGA CIKIN ALAMUN GASKIYARSA: BUSHARAR DA LITATTAFAN DA SUKA GABATA SUKA FITAR, KUMA DAGA CIKIN HUJJOJI - MA -: WANNAN CI GABA DA YADUWAR ADDININ MUSULUNCI A KOWANE LOKACI DA WURI, KUMA DAGA CIKIN ALAMUN GASKIYARSA: BADA LABARI GAME DA AL'UMMOMIN DA SUKA GABATA DA AL'AMURAN DA KE ZUWA.

### TA YAYA MANZON ALLAH - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI - YA HAU ZUWA SAMA A CIKIN DARE GUDA?

AN TAFI DA ANNABI - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI – CIKIN DARE AKAN BURAKA HAR ZUWA KUDUS, SANNAN YA HAU SAMA TARE DA JIBRILU - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI -, KUMA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YANA DA IKON YIN KOMAI BA ABINDA KE GAGARARSA A DUNIYA KO A CIKIN SAMA, KUMA KAMAR YADDA MUKE GANI A YAU: TA YAYA NE MUTUM MAI RAUNI YA IYA A CIKIN TUNANINSA YA ƘIRƘIRI JIRGIN SAMA WANDA YA ZARCE SAURIN SAUTI, KUMA YA ƘIRƘIRA KAYAN WATSA HOTO MASU ƁANGARORI UKU, WANDA KE SANYA MUTUM YA ZAMA A  SAMA DA WURI GUDA A LOKACI GUDA; ALLAH SHI NE MAFI GIRMA, DA DAUKAKA, KUMA MAFI GIRMAN IKO SAMA DA HALITTARSA.

### ME YASA ANNABI MUHAMMADU ((S.A.W)) YA ZAMA KARSHEN ANNABAWA?

HAKIKA LAMARIN AIKO MANZANNI YANA DA NASABA DA HIKIMA - WACCE ITA CE SHIRIYA DA NUNI - KUMA TUNDA LITTATTAFAN DA SUKA GABATA SUN FUSKANCI RAGI, KUMA AN JIRKITA SU BAYAN MUTUWAR MANZANNI; HIKIMAR ALLAH TA BUKACI YA AIKO MANZO DA LITTAFI WANDA BA ZAI FUSKANCI WANNAN RAGIN BA. MAIMAKON HAKA, ALLAH YA TABBATAR DA CEWA ZAI KIYAYE SHI HAR ZUWA TASHIN KIYAMA, KUMA TUNDA NA DAGA CIKIN MU'UJIZAR ALKUR'ANI.-CEWA  LITTAFI NE BAYYANANNE KUMA HUJJA CE WACCE TA TABBATA TA KUMA TSAYA AKAN DUKKAN HALITTA. YANA DAGA CIKIN HANKALI CEWA MANZO - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI - SHI NE KARSHEN ANNABAWA DA MANZANNI.

### ME YA SA YA WAJABTA MU KAUNACI MANZON - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI?

SABODA SOYAYYAR ANNABI – ((S.A.W))- TANA DAGA CIKIN SHIKA-SHIKAN IMANI, A MAIMAKON HAKA, IMANI DA ALLAH MADAUKAKIN SARKI BA YA CIKA SAI DA WANNAN KAUNA, KUMA AN HADA KAUNAR ANNABI – ((S.A.W)). TARE DA KAUNAR ALLAH MADAUKAKIN SARKI, KUMA SABODA ALLAH MAI GIRMA DA DAUKAKA YA ZABE SHI DAGA CIKIN MUTANE DON ISAR DA WANNAN SAKON MAI GIRMA, ALLAH YA ZABI MAFI KYAWUN MUTANE TA HANYAR NASABA, DABI'U, MAGANA DA AIKI. DOMIN ALLAH MADAUKAKI YA FI KOWA SANIN WANDA YA BA AMANAR SAKONSA, TO MUDDIN ALLAH

YA ZABE SHI CIKIN DUKKAN MUTANE DON WANNAN BABBAN AIKI. HAKKINMU NE MU ZABE SHI A MATSAYIN MASOYI SAMA DA DUKKAN MUTANE. DOMIN SHI NE WANDA YA SANAR DA MUTANE UBANGIJINSU, KUMA SHI NE MAFI ALHERIN MANZO DAGA CIKIN AL'UMMARSA, KUMA MAFI RAHAMAR ANNABI GA AL`UMARSA, DOMIN BABU WANI MAI BAIWA BAYAN ALLAH GA MUTANE SAMA DA SHI - TSIRA DA AMINCIN ALLAH SU TABBATA A GARE SHI - KUMA SHI ANNABI- AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI - YA JURE CUTARWA DOMIN KIRAN MUTANE ZUWA GA ADDINI DA KYAUTATAWA, HAR KIRJINSA ((S.A.W)) YANA YIN KUNCI, IDAN WANI BAI YI IMANI BA IDAN YA KIRA SHI ZUWA GA ADDININ ALLAH SABODA TAUSAYI A GARE SU NA SHIGA WUTA, ALLAH MADAUKAKI YA CE: (KANA NEMAN KA HALAKA KANKA A BAYANSU IDAN BA SU YI IMANI DA WANNAN ALKUR`ANIN BA SADODA BAKIN CIKI) (AL-KAHF: 6), SABODA WANNAN DALILI. ANNABI - TSIRA DA AMINCI SU TABBATA A GARE SHI - YA KASANCE MUTUMIN DA YA FI CANCANTA DA KAUNARMU BAYAN ALLAH.



# TAMBAYOYI MASU ALAQA DA RANAR LAHIRA





## MECECE RANAR LAHIRA?

RANA CE DA ALLAH KE TAYAR DA HALITTU DOMIN A YI MASU HISABI, KUMA ANA KIRAN TA RANAR KARSHE; SABODA BABU RANA A BAYANTA, KUMA ANA KIRANTA RANAR HISABI. DOMIN ALLAH YANA YIWA MUTANE HISABI AKAN ABINDA SUKA AIKATA A WANNAN DUNIYA, SABODA HAKA DUK WANDA YAYI ALHERI KO YAYIWA ALLAH BIYAYYA. ZAI SHIGA ALJANNA, KUMA DUK WANDA YA AIKATA MUMMUNAN AIKI KUMA YA SAƁA WA ALLAH; ZAI SHIGA WUTA, WACCE ITA CE RANAR DA RAYUWAR DUNIYA ZATA KARE, KUMA ANA KIRANTA DA RANAR TASHIN ALKIYAMA, WATAU RANAR DA MUTANE ZASU TASHI DAGA KABARINSU SU NUFI SAMA DOMIN HISABI.

## YAUSHE NE RANAR KIYAMA? ME YASA AKA ƁOYE MANA WANNAN RANAR?

BABU WANDA YA SAN LOKACIN TASHIN KIYAMA.ALLAH MABUWAYI DA DAUKAKA YA CE: **KUMA SUNA TAMBAAR KA GAME DA SA`A YAUSHE NE MATABBATARTA?** (42) ME YA HADA KA DA AMBATONTA? (43) ZUWA GA UBANGIJINKA KARSHEN AL`AMARINTA YAKE (44) KAI MAI GARGADI KAWAI NE GA MAI TSORONTA (45) (AL-NAZI'AT: 42-45), ALLAH YA YA BOYE MANA ITA. DON MU DAGE WAJEN AIKI DA KASANCEWA CIKIN SHIRI DOMIN WANNAN RANA A KOWACE RANA, TA HANYAR AIKATA ALHERI DA BARIN SHARRI, DA ACE KUWA MUTUM YA SAN WANNAN RANAR; DA BAI TUBA BA SAI JIM KADAN KAFIN KAFIN LOKACIN YA CIKA, DA KUMA DUNIYA TA CIKA DA FASADI FIYE DA YADDA TAKE.

## MENENE HISABI?

SHI NE ALLAH YA TARA NA FARKON DA NA KARSHE ALLAH MADAUKAKI YA CE: (KA CE: HAKIKA NA FARKO DA NA KARSHE (49) ZA A TATTARA SU ZUWA WANI LOKACI NA WANI YINI SANANNE) (AL-WAQI'AH: 49-50). SAI YA NUNA MUSU AYYUKANSU, SANNAN YA SAKA MUSU, KOWA GWARGWADON AIKINSA, WANDA YA AIKATA ALHERI ZAI SAMI ALHERI, WANDA YA AIKATA SHARRI ZAI SAMI SHARRI, ALLAH MADAUKAKI YACE: (WANDA YA AIKATA GWARGWADON NAUYIN ZARRA NA ALHERI ZAI GANSHI (7) WANDA YA AIKATA GWARGWADON NAUYIN KWAYAR ZARRA NA SHARRI ZAI GANSHI)) (ZALZALAH 7-8)

## MECECE MUTUWA?

YARO YANA ƊAN SHEKARA SHIDA ZUWA ƘASA - GALIBI - BA ZAI IYA YA FAHIMCI CIKAKKIYAR MA'ANAR MUTUWA DA TASHIN MATATTU BA, KUMA MUTUWAR ITA CE ƘARSHEN DA BA MAKAWA GA DUKKAN 'YAN ADAM, AMMA YARO DAGA SHEKARA SHIDA ZUWA TAKWAS. YAWANCIN LOKACI YANA IYA FAHIMTAR MA'ANAR MUTUWA DA AUKUWARTA GA DUKKAN MUTANE, KUMA YARO DAGA SHEKARA TAKWAS ZUWA GOMA; YANA IYA FAHIMTAR MUTUWA DA TASHIN MATATTU, KUMA YARO NA IYA MUTUWA A CIKIN DANGI, KUMA WANNAN SHINE FARKON HADUWARSA DA MUTUWA, KUMA BA MU SAN IRIN TUNANIN DA ZAI JI BA LOKACIN DA YA JI WANI ABU GAME DA MUTUWA DA KABARI. SABILI DA HAKA, DOLE NE MU ƊAUKI MATAKIN BAYYANA MA'ANAR MUTUWA GA YARO BA TARE DA YI MASA ƘARYA BA DA ƘOƘARIN SHAWO KANSA CEWA MUTUMIN DA YA MUTU YA YI TAFIYA NE DAGA GANE GASKIYA DAGA WASU.

ZAI FI KYAU – KAFIN YARO YA SAMI KANSA A YANAYIN MUTUWAR WANI A CIKIN DANGI - A NUNA MASA MATACCEN TSUNTSU, MATACCEN ITACE, KO MATATTUN KWARI. DOMIN WANNAN YANA NUNAWA YARON MA'ANAR MUTUWA A AIKACE, SANNAN KUMA MUNA ƘOƘARI MU BAYYANA WA YARON CEWA MATATTU ZASU TAFI SU ZAUNA A WATA DUNIYA, KUMA CEWA DUKKANMU ZAMU MUTU LOKACIN DA MUKA GIRMA ZAMU HAƊU DA DUK WAƊANDA SUKA MUTU A GABANMU, KUMA MU ZAUNA TARE DA SU A SAMA, IN ALLAH YA YARDA, KUMA YANA DA MAHIMMANCI: CEWA YARON YA SAN CEWA BA MUTUWA NA NUFIN ƘARSHE BA, TAFIYAR MUMINI CE ZUWA KYAKKYAWAR RAYUWA, DA KUMA TAFIYAR MUGU ZUWA GA SAKAMAKONSA, KUMA IDAN ALLAH YA KASHE MU, WANNAN BA YANA NUNA CEWA BAYA KAUNAR MU BANE, A'A SAI DAI YA KASHE MU NE DOMIN MU RAYU A KUSA DA SHI, A CIKIN LALJANNATU MASU KYAU, WADANDA BA ZA MU IYA SURANTA KYAWUNSU BA.

## ME YASA WASU YARAN KE MUTUWA TO?

YARA GABAƊAYA BASA AIKATA SHARRI, KUMA BASA GANGANCIN AIKATA ZUNUBI, SABODA HAKA; ALLAH YANA KARBAR WAƊANDA SUKA MUTU DA RAHAMARSA KUMA YANA SHIGAR DA SU ALJANNA, KUMA IDAN MUTUM YA MUTU YA ZO KARSHEN RAYUWARSA. RUHINSA YANA NAN DARAM, YAYIN DA RANSHI YAKE HAWA ZUWA GA MAHALICCINSA TO KYAWAWAN AMBATONSHI DA KYAWAWAN AYYUKANSA ZASU DAUWAMA A ZUKATAN MUTANE, DON HAKA; DOLE NE MUTUM YA SHIRYA HADUWA DA UBANGIJINSA TA HANYAR KYAUTATAWA TARE DA BIN KOYARWAR SHARI'AR MUSULUNCI.

## INA MUKE ZUWA IDAN MUKA MUTU?

LOKACIN DA LOKACINMU DA ALLAH YA SANYA MANA A WANNAN DUNIYA YA ƘARE; MUNA MATSAWA NE ZUWA KABARI - WANDA SHINE WURIN DA AKA TANADA DON MATATTU -, KUMA KABARIN ZAI KASANCE DAUSAYI DAGA CIKIN DAUSAYIN GIDAN ALJANNA GA WANDA YAYI IMANI DA UBANGIJINSA KUMA YAYI MASA DA'A KUMA YAYI AIKI NAGARI YAYIN RAYUWARSA A WANNAN DUNIYA. , DON YA SAMI NI`IMA KAFIN ALKIYAMA TA TSAYA.

## SHIN MAMACI YANA JI KUMA YANA GANI? TA YAYA YAKE NUMFASHI A ƘARƘASHIN KASA? KUMA YANA CI, DA SHA DA BACCI?

E, MUTUMIN DA YA MUTU YANA JIN SALLAMA A LOKACIN DA MUKA YI MAI, KUMA IDAN MUKA YI MASA ADDU'A TANA ISA GARE SHI, AMMA BA YA NUMFASHI KAMARMU. SABODA BA YA BUƘATAR NUMFASHI, YANA CIKIN WATA RAYUWAR DA BA TA DACE DA RAYUWARMU TA DUNIYA BA, DON HAKA; RAYUWAR LAHIRA, TA FARKO ITA CE RAYUWAR BARZAHU, TANA DA DOKOKI DA YANAYI DABAN, DON HAKA BABU NUMFASHI, KO CI, KO SHA, KO BACCI, KO AIKI, SAI CI GABA DA NI'IMA KO AZABA.

## MECECE ALJANNAH KUMA MENENE A CIKINTA?

ALJANNA GIDAN AMINCI NE, KUMA WURI NE MAI KYAU, KUMA TANA DA DUK ABIN DA KAKE FATA, DA KUMA DUK ABIN DA KAKE SO. ALJANNA WURI NE DA ADALAI DA SUKA YI AIKI MAI KYAU SUKE ZUWA, TANA DA ƘOFOFI GUDA TAKWAS, MATAKI-MATAKI NE, WANDA MUMINAI SUKE SHIGA DAIDAI GWARGWADON RABON KOWANE DAYA DAGA CIKINSU NA KYAWAWAN AYYUKA DA RAHAMA. MAI AYYUKAN KIRKI DA YAWA MATSAYINSA YAFI NA MAI KYAWAWAN AYYUKA KADAN, AMMA KOWA YANA RAYUWA CIKIN NI'IMA, DA GAMSUWA DA NI'IMAR, A CIKIN ALJANNA ZA MU RAYU CIKIN FARIN CIKI, BA ZA MU YI RASHIN LAFIYA A CIKINTA BA KUMA BA ZA MU GAJI BA, KUMA ZA MU GA ALLAH - TSARKI YA TABBATA A GARE SHI – MANZONMU ((S.A.W)) DA ANNABAWA, TSIRA DA AMINCI SU

TABBATA A GARE SU DA DUK WADANDA MUKE SO, INSHA ALLAH , KUMA A CIKIN TA AWAI DUK ABIN DA MUKE SO KO MUKE KAUNAR SHI DAGA ABINCI, KO ABIN SHA, DA JIN DAƊI DA NI'IMA.

## MECECE WUTA KUMA ME YASA ALLAH YA HALICCE TA?

WUTA GIDAN AZABA NE, KUMA WURI NE DA ALLAH YA TANADA DON AZABTAR DA DUK WANDA YA AIKATA SHARRI KO CUTAR DA MUTANE, YA SABAWA ALLAH KUMA BAYA BIN UMARNIN SA.

## -MENE NE MAKOMAR DABBOBI - SHIN ZASU SHIGA ALJANNA NE KO WUTA?

DABBOBI BA SU DA HUKUNCI A KANSU, MAIMAKON HAKA SU MA HALITTU NE DA ALLAH YA HALICCE SU SABODA DAN ADAM, DON HAKA BABU HISABI KUMA BABU WANI HUKUNCI A KANSU, KUMA A RANAR KIYAMA DUKKAN DABBOBI ZA SU TATTARA A GABAN ALLAH SANNAN YA YI HUKUNCI A TSAKANINSU, ZAI HUKUNTA TUNKIYA MAI KAHO DA TA TUNKUYI MARA KAHO, IDAN ALLAH YA GAMA HUKUNCI A TSAKANIN DABBOBIN, SAI YACE MUSU, KU ZAMA TURBAYA, SAI SU ZAMA.



# TAMBAYOYIN DA KED A ALAKA DA KADDARA



## ME AKE NUFI DA HUKUNCI DA KUMA KADDARA?

HUKUNCIN ALLAH DA KUMA KADDARA RUKUNI NE DAGA CIKIN RUKUNAN IMANI, ALLAH MADAUKAKI YA CE: (KUMA YA HALICCI KOMAI, KUMA YA KADDARA SHI KADDARAWA) (AL-FURQAN: 2) KUMA MA'ANAR HUKUNCIN ALLAH DA KADDARARSA SHI NE: ALLAH YA SAN YAWAN ABUBUWA KAFIN SAMUWARSU, YA KUMA RUBUTA SHI, DA GANIN DAMARSA, YA KUMA HALICCE SU DA ITA KADDARAR.

## TA YAYA ALLAH YAKE SANIN ABIN DA ZAI FARU TUN KAFIN YA FARU?

ZA A IYA CE MASA DA MISALI MAI SAUKIN FAHIMTA: CEWA WANI MAI KERA ABIN WASA DA YAKE WASA YA SAN ABIN DA WASAN ZAI HAIFAR TUN KAFIN YA YI SHI; DOMIN SHI NE WANDA YA KIRKIRE SHI KUMA YA KAYYADE AIKIN KOWANE ABU KARAMI DA BABBA A CIKIN WANNAN WASAN, DOMIN YA SAN CIKAKKEN BAYANI GAME DA WANNAN WASAN DA WURAREN DA ZAI IYA MOTSAWA, KUMA ALLAH SHI NE WANDA YA HALICCI WANNAN MUTUMIN DA YAKE DA IKON WADANNAN ABUBUWA, DOMIN ALLAH SHI NE MAFI GIRMAN IYAWA, MAFI YALWAR ILIMI KUMA MAFI KAMMALA, ALLAH YA KEWAYE DUK ABINDA YA HALITTA DA ILIMINSA TUN KAFIN YA HALICCE SHI, DA YAYIN HALITTAR SA, DA KUMA BAYAN YA HALICCE SHI, TO ALLAH SHI NE WANDA YA HALICCI MUTUM, DA LOKACI DA WURI,



DOMIN ALLAH YA SAN ABIN DA YA KASANCE, ABIN DA YAKE KASANCEWA DA ABIN DA ZAI KASANCE BAYAN HAKAN.

### SHIN AN TILASTA MANA NE? SHIN MUTUM YANA DA ZAƁI A CIKIN AYYUKANSA?

AN TILASTA WA MUTUM CIKIN WASU ABUBUWA, KUMA AN BASHI ZAƁI A CIKIN WASU ABUBUWA, SABODA AN TILASTA MANA HAIHUWA DA MUTUWA, DA KUMA TSAWON RAYUWA, KUMA BAMU DA ZABI AKAN SUWANENE IYAYENMU DA KAKANNINMU, KUMA AN TILASTA MANA SADA ZUMUNCI DA DANGINMU, YAYIN DA AKA BAMU ZABIN MUYI SALLA KO KAR MUYI, IMANI KO KAFIRCI, KUMA DUK DA WANNAN ZABIN; NUFINMU YANA CIKIN NUFIN ALLAH; DA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YANA SO YA HANA MU ZABI, DA YA YI, KUMA DA YANA SON HANA MU KIN YIN WANI ABU, DA YA YI HAKAN, AMMA YA HUKUNTA CEWA MUTUM YA YI ZABI SANNAN KUMA ZA A YI MASA HISABI KAN WANNAN ZABIN, KUMA WANNAN ITA CE MA'ANAR FADINSA MADAUKAKI: (KUMA BA ZA KU SO BA, FACE ABINDA ALLAH UBANGIJIN TALIKAI YA GA DAMA,) (AT-TAKWIR: 29), KUMA ANA IYA BAYANIN BATUN TILAS DA KUMA ZABI A AIKACE: DON HAKA MAI BADA TARBIYYAR SAI YA KAWO KOFIN GILASHI YA CE WA YARON: SHIN ZA KA IYA JEFAR DA WANNAN ƘOƘON A ƘASA KA FASA SHI? YARON ZAI AMSA: TABBAS: ZAN IYA. MAI BADA TARBIYYAR ZAI FARA YANA MAI TAMBAYA: ME YA HANA KA? YARO ZAI BA DA AMSA: WANNAN BA DAIDAI BA NE KUMA BAI KAMATA A YI HAKA BA, DON HAKA MALAM SAI YA YI TSOKACI YANA MAI CEWA: ALLAH - MADAUKAKI - YA SANI TUN A DA CEWA BA ZA KA FASA WANNAN ƘOƘON BA. SABODA KAI YARO NE NAGARI, KUMA YA SAN - HAR ABADA - CEWA YARON BANZA ZAI FASA WANNAN KOFIN, SHIN WANI NE YA HANA KA JEFAR DA WANNAN KOFIN A ƘASA? KO KUWA WANI NE YA TILASTAWA FITINANNEN YARON YA FASA KOFIN? WANNAN SHI NE YADDA SHIRIYA DA BATA SUKE, SANNAN SAI A CE MASA: MUTUM BAI SAN ABIN DA ALLAH YA RUBUTA A KANSA BA, KUMA BA A BUKATAR KA SAN ABIN DA AKA RUBUTA, AMMA ANA BUKATAR KA YI IMANI DA CEWA SANIN ALLAH SHI NE CIKAKKE KUMA KAMMALALLE, DAGA CIKI HARDA RUBUTUN KADDARA, KUMA KAI KE DA ALHAKIN NUFINKA DA KUMA GWARGWADON BIYAYYARKA DA UMARNI DA BARIN HARAMTATTUN ABABE, WANNAN NA KARKASHIN DAMARKA DA NUFINKA.

### ME YASA YA SHIRYAR DA WASU MUTANEN BAN DA WASU?

ALLAH MADAUKAKI YA SHIRYAR DA DUKKAN MUTANE SABODA FADINSA - MADAUKAKI -: (KUMA MUN SHIRYAR ZUWA HANYOYI BIYU) (AL-BALAD: 10), KUMA MA'ANAR WANNAN SHIRIYAR ITA CE: TSAKANIN SHIRIYA NE DAKE BAYYANE GA MUTANE KUMA YA YI MU SU BAYANI GAME DA MADAIDAICIYAR HANYA, DON GASKIYA TA BAYYANA KUMA KARYA TA BAYYANA, KUMA ALLAH YA BAR 'YANCI GA MUTANE. AKWAI WADANDA SUKA ZABI HANYA MADAIDAICIYA KUMA AKWAI WADANDA SUKA ZABI HANYAR DA BA DAIDAI BA.

## IDAN HAR ALLAH TUN ASALI YA KADDARA CEWA A CIKINMU ZA A SAMI MASU ZUNUBI DA ƁATA TO ME YASA ZAI HUKUNTA MU?

WANNAN ILIMIN ILIMI NE NA ALLAH, KUMA DAN ADAM BASHI DA WANI ILMI GAME DASHI, KUMA ABINDA SUKE DASHI KAWAI ZATO NE, DA JAHILCI, SABILI DA HAKA MUTUM YANA DA HISABI AKAN ABINDA YA AIKATA A RAYUWARSA TA DUNIYA, KUMA BABU YADDA BAWA ZAI SAN GAIBI WANDA ALLAH YA SANI HAR SAI YA AIWATAR DA AIKIN SA YA GAMA SANNAN YA SAN SHI. DON HAKA KADDARAR DA AKA RUBUTA BA HUJJA BACE AKAN ABIN DA YA GABATA BA WAI ABINDA ZAI ZO A NAN GABA BA. HAKA KUMA, SAI A CE MASA: ALLAH YA RUBUTA MUKA AL'AMURAN DUNIYA ... DON HAKA ME YASA KAKE AIKATA ABINDA ZAI AMFANE KA KUMA KA BAR ABINDA ZAI CUTAR DA KAI?! ZAI IYA BA SHI MISALI YA CE: IDAN MUTUM YANA SON TAFIYA ZUWA WATA ƘASA, KUMA WANNAN ƘASAR TANA DA HANYOYI BIYU, ƊAYANSU TANA DA AMINCI, ƊAYAR KUMA BA TA DA AMINCI, TO WACCE DAGA CIKINSU ZAI ZAƁA? TABBAS, ZAI ZABI HANYA TA FARKO, TO HAKA ABIN YAKE WAJEN TAFIYA ZUWA LAHIRA, MUTUM YANA ZABAR HANYA MADAIDAICIYA DON ISA ALJANNA - WACCE ITACE BIN UMARNI DA NISANTAR HANI – DA ACE KUWA KADDARA HUJJA CE GA WANI DA BAMU IYA KAMA MASU LAIFI BA; SABODA ZA SUN BADA HANZARI DA KADDARA GAME DA AYYUKANSU, SABODA HAKA; WAJIBI NE MUTUM YA YARDA KUMA YA MIKA WUYA GA ALLAH MADAUKAKI, DOMIN ALLAH (BA A TAMBAYAR SA GAME DA ABIN DA YAKE AIKATAWA SU KUMA (MUTANE DA ALJANU) ANA TAMBAYARSU) (AL-ANBIYA': 23), DON HAKA HALITTA HALITTARSA CE KUMA AL'AMARI AL`AMARINSA NE - TSARKI YA TABBATA GA SHI.

## ME YASA ALLAH YA HALICCE MU? MENENE ASALIN HALITTA? ME YASA AKA HALICCI DABBA

ALLAH MADAUKAKI YA CE: (KUMA BAN HALICCI ALJANNU DA MUTANE BA SAI DON SU BAUTA MIN) (AZ-ZARIYAT: 56). AN HALICCE MU NE DON WATA MANUFA WACCE ZA TA AMFANE MU - WACCE ITA CE BAUTA MASA, TSARKI YA TABBATA A GARE SHI, DA KUMA SAMUN SAKAMAKO A LAHIRA GWARGWADON AYYUKANMU. ALJANNA TA MASU KYAUTATAWA CE KUMA ITA WUTA TA MASU MUNANAWA CE, KUMA WANNAN DUNIYA GABA DAYANTA ALLAH MADAUKAKIN SARKI NE YA HALICCE TA, DOMIN AN YI TA NE DA DAIDAITO DA ILIMI. YA HALICCI SAMMAI DA KASSAI YA KUMA YADA TAURARI A CIKI, AN HALICCI TAURARI DON SU ZAMA ALAMU DA IZINA DA KWALLIYA, AN HALICCI RANA DOMIN BAMU DUMI DA ZAFI DA KUMA BADA GUDUMMAWA GA TSIROWAR TSIRE-TSIRE DA KAWAR DA KWAYOYIN CUTA, AN HALICCI DABBOBI DOMIN MUTUM YA CI DA SU KUMA DAUKE SU ALLAH MADAUKAKI YA CE: «KUMA DAWAKAI, DA ALFADARAI, DA JAKUNA, DOMIN KU HAU SU NE DA KUMA ADO , KUMA YANA HALITTAR ABIN DA BA KU SANI BA." (AN-NAHL: 8). SHIRYA KASA DOMIN ZAMA

DA KUMA KIRKIRAR WADANNAN ABUBUWA KAFIN HALITTAR MUTUM. LAMARI NE NA GIRMAMAWA DA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA YI WA MUTUM, BUGU DA KARI KAN CEWA DUKKAN WADANNAN ABUBUWA SUNA YABON ALLAH MADAUKAKIN SARKI, ITA KANTA WANNAN BAUTA CE A KANSU. . (BABU WANI ABU FACE YANA TASBIHI DA GODIYA A GARE SHI, AMMA KU BAKWA FAHIMTAR TASBIHINSU, DOMIN SHI YA KASANCE MAI HAKURI NE KUMA MAI GAFARA) (AL-ISRAA: 44).

## SHIN ALLAH ZAI BINCIKI WADANDA MANZO BAI ZO MUSU BA?

SUNA ƘARƘASHIN HISABI DA LISSAFI. SABODA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA BA SU HANKALI, DON HAKA NE ALLAH ZAI JARRABE SU RANAR TASHIN KIYAMA KUMA YA UMARCE SU. IDAN SUKA YI BIYAYYA, ZASU SHIGA ALJANNA, IDAN KUMA BASU YI BIYAYYA BA, ZASU SHIGA WUTA.

## ME YASA AKE SAMUN SHARRI?




WANNAN DUNIYA GIDAN JARRABAWA NE, KUMA ITA KAMAR FARKON BABIN LABARI NE WANDA YAKE DA FASALAI GUDA BIYU, ITA KUMA LAHIRA ITA CE GIDAN SAKAMAKO DA HISABI, DA KUMA FITAR DA HAKKI DAGA AZZALUMAI ZUWA GA WADANDA AKA ZALUNTA, KUMA ITA CE A MATSAYIN BABI NA BIYU NA LABARIN, KUMA DON WANNAN; KASANCEWAR FAJIRAI DA RASHIN AZABTAR DASU A WANNAN DUNIYA JARRABAWA CE A GARE SU, KUMA WANNAN BA YANA NUFIN KARSHEN LAMARIN BANE, A'A YA ZAMA DOLE KOWA YA TASHI RANAR TASHIN KIYAMA TA YADDA KOWANE MUTUM ZAI SAMI LADAN AYYUKANSA. ALLAH MADAUKAKI YA CE: «WANDA YA YI AIKI KODA NAUYIN KWAYAR ZARRA NE ZAI GAN SHI (7) KUMA WANDA YA YI AIKI NA SHARRI KODA NAUYIN KWAYAR ZARRA NE ZAI GAN SHI.» (ZALZALAH: 7-8).

## ME YASA ALLAH YA HALICCI MASU SHARRI?

ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA HALICCI MUTANE KUMA YA BASU 'YANCIN ZABAR AIKATA ALHERI KO SHARRI, DOMIN ZAKA IYA ZAMA MAI LADABI, KUMA ZAKA IYA NUNA RASHIN LADABI, AMMA DOLE NE KA KARBI SAKAMAKO, KUMA WANNAN WATA NI'IMA CE DAGA ALLAH DA HIKIMA. MIYAGU ZA SU IYA ZAMA MASU KIRKI KUMA AIKINMU SHI NE MU TAIMAKA MUSU A KAN HAKAN, AMMA IDAN SUKA ƘI KUMA SUKA NACE KAN MUGUNTA; HAKKINMU SHI NE MU HANA SHARRINSU ISA GA

MUTANE. DON ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA SO MU KUMA YA BAMU LADA, KUMA ALLAH MADAUKAKIN SARKI SHI NE MAHALICCIN KOMAI A WANNAN RAYUWAR, KUMA WANNAN RAYUWAR GIDAN FITINA CE DA JARABAWA, ALLAH MADAUKAKI YACE: (WANDA YA HALICCI MUTUWA DA RAYUWA DON YA JARRABA KU WANENE DAGA CIKINKU YA FI KYAN AIKI) (ALMULK: 2), KUMA NA DAGA JARRABAWA: SAMUWAR SHARRI A TSAKANIN SHEDANU DA FANDARARRU DAGA CIKIN MUTANE.

### ME YASA WASU MUTANE AKE HAIFAR SU DA MUNI KO NAKASA?

ALLAH YANA JARRABAR WASU DA RASHI DA CUTA. DON SU YI HAKURI SU YAWAITA AYYUKANSU NA ALHERI, KUMA DON ALLAH - MADAUKAKI YA TUNATAR DA MU NI'IMAR DA YA YI MANA TA SAMAR DA MAFI YAWANMU LAFIYA, DON HAKA MUNA GODE MASA A KAN HAKA, KUMA DON TUNATAR DA MU RAUNINMU TA FUSKAR IKONSA, DON KADA MU YI GIRMAN KAI, SAI DAI MU YI TAWALI'U DA TAIMAKON JUNA, KUMA BAYAN RANAR SAKAMAKO: WAƊANDA SUKA AIKATA NAGARTA ZA SU YI RAYUWA TA HAR ABADA, CIKIN KOSHIN LAFIYA AALJANNATAI NA NI'IMA - INSHA ALLAH.

### ME YASA AKE SAMUN MASU WADATA DA MATALAUTA? KUMA :ME YASA WASU DAGA CIKIN MUTANEN BANZA SUKE ZAUNE A FADOJI KUMA WASU DAGA CIKIN MUTANEN KIRKI SUNA ZAUNE A BUKKOKI?

DUK WANNAN A RAYUWAR TA DUNIYA DAGA ALLAH NE, TSARKI YA TABBATA A GARE SHI, KUMA ALLAH YANA JARRABAR BAYINSA, WANI LOKACI KUMA YANA AZURTA MUTUMIN KIRKI. DON GWADA KARAMCINSA GA WASU, WANI LOKACIN KUMA YANA HANA SHI WADATA; DON YA GWADA HAƘURINSA JURIYARSA WAJEN GANIN BA ZAI YI SATA BA KO YA KULLACI WANI, DUK LOKACIN DA MUTUMIN KIRKI YA RAYU A WANNAN RAYUWAR NA ƊAN LOKACI YA YI HAƘURI; TO LADANSA MAI GIRMA NE A RANAR LAHIRA, AMMA MUTUMIN DA AKA BASHI BASHI ARZIKI KUMA BAI BA WASU BA KUMA YA WULAKANTA SU. ZA'AYI MASA AZABA ARANAR ALQIYAMAH. DOMIN BAI YABA DA ALHERIN ALLAH BA.

KUMA MUNA IYA CE MASA: HAKIKA ALLAH - TSARKI YA TABBATA A GARE SHI - YA HALICCI MUTANE MASU DARAJOJI DABAN-DABAN - WASU DAGA CIKINSU TALAKAWA WASU KUMA ATTAJIRAI. DON MASU ARZIKI SU TAUSAYA WA TALAKAWA, KUMA MASU KARFI SU TAIMAKI MASU RAUNI. HIKIMAR ALLAH TA HUKUNTA CEWA MUTANE SU ZAMA DABAN A CIKIN KOMAI, HARSUNAN SU SUN BAMBANTA KUMA LAUNUKAN SU SUNA DA YAWA. SUN KASANCE A LAUNIN FATA DA YANAYI MABANBANTA NE, MASU KUZARI DA MALALATA, MASU FIFITA WASU DA MASU SON KAI, MASU KARIMCI DA MAROWATA. WADATA JARRABAWA CE, TALAUCI MA



JARRABAWA CE, ANA JARRABAR ATTAJIRAI:SHIN ZAI CIYAR? SHIN ZAI BA DA SHIN ZAI YI ZAKKA? SHIN ZAI YI KARAMCI? ZAI BADA SADAKA? TALAKAWA ZA A JARRABAWA SU: SHIN ZAI YI HAƘURI? SHIN ZAI SHA WAHALA? SHIN ZAI NEMI HANYOYIN NEMAN ARZIKIN DUNIYA? SHIN ZAI BADA CIN HANCI? ZAI YI SATA? DUK WANNAN JARRABAWA CE, AMMA AKWAI GARANTI GA DUKKAN BANGARORIN BIYU: CEWA RAYUWA TANA GA ALLAH MADAUKAKIN SARKI, KUMA DUKIYA DA TALAUCI BA SU HANA SHIGA ALJANNA DA WUTA, DON HAKA ANA CAJIN KOWA GWARGWADON ABIN DA YA MALLAKA, DA ACE KUWA MUTANE AJI DAYA NE MASU KUDI. DA BASU YIWA JUNA HIDIMA BA, DA KUMA BASU BUKACI JUNA BA, ALLAH MADAUKAKI YA CE: (DON WASU SASHEN SU DAUKI WASU SASHEN A MATSAYIN ABIN IZGILI) (AL-ZUKHRUF: 32), MA'ANA, SU YI WA JUNA IZGILI, KUMA DA WANNAN NE YANAYIN RAYUWAR YAKE JUYAWA, AMMA A YANAYIN AJI DAYA, TO RAYUWA ZATA TSAYA.

## ME YASA MUKE RASHIN LAFIYA? ME YASA MUTANE KE FADAWA MASIFA?

ALLAH YANA JARRABAR KOWANE MUTUM; SHIN ZAI YI HAKURI KO KUWA ZAI YI FUSHI? KUMA ALLAH MADAUKAKIN SARKI ZAI SAKA WA WADANDA SUKA YI HAKURI DA LADA MAI YAWA, KUMA MUMINI ZAI YI FARIN CIKI DA SHI A RANAR TASHIN KIYAMA, CUTA, DA BALA'I, DA RADADI SU NA DAGA KADDARAR ALLAH DA SU YAKE DAUKAKA DARAJOJI DA TSARKAKE ZUKATANMU DA DABI'UNMU DAGA GIRMAN KAI, JIJI-DA-KAI DA GIRMAN KAI, KUMA A CIKINSU MUMINI YAKAN KUSANCI UBANGIJINSA DA ADDU'A DA HAƘURI, DON HAKA IMANINSA DA KYAWAWAN AYYUKANSA SU ƘARU, KUMA UBANGIJINSA YA SO SHI, KUMA MUTUM YANA SANIN ƘIMAR LAFIYA DA KUMA NI'IMA, KUMA ZA MU IYA BA SHI MISALI DA MOTA, DON HAKA SAI MU TAMBAYE SHI: ME YA SA AKA ƘIRƘIRA MOTAR? DON TA YI TAFIYA,

KO BA HAKA BA? DON HAKA; TO ME YASA MASANA'ANTAR MOTAR TAKE MATA BIRKI? SHIN WANNAN BAI CI KARO DA MANUFAR YIN MOTAR BA NA TA DINGA TAFIYA? YIN AMFANI DA BIRKI YA ZAMA DOLE DOMIN KARE LAFIYARTA, AN SANYA MOTAR GUDU, SAI BIRKI YA TSAYAR DA ITA A LOKACIN DA YA DACE DON KAR A HALAKA MAI ITA, KAMAR YADDA ALLAH - MADAUKAKI - YA HALICCE MU DON YA FARANTA MANA A CIKIN BAUTARSA DA NI'IMOMINSA A KANMU, DON HAKA ALLAH MADAUKAKIN SARKI YA HALICCI BALA'I DON TUNATAR DA MUTUMIN MAI SHAGALA GAME DA BABBAN AIKIN DA AKA HALICCE SHI DOMIN SHI, DON HAKA YA DAINA SHAGALARSA DA SAKACINSA, YA TINA UBANGIJINSA, KUMA YA DINGA NEMAN GAFARA DA HAKURI DA NEMAN LADA.

## SHIN ALLAH NE YA HALICCI DABBOBI DA KWARI MASU CUTARWA?

ALLAH SHI NE MAHALICCIN KOMAI, KUMA SHINE UBANGIJIN KOMAI, DAN HAKA YA HALICCI WADANNAN HALITTU, DAN HAKA YA HALICCE SU DA HIKIMARSA - KUMA -. DOMIN SHI MAI HIKIMA NE, MAI ILIMI, WANDA YA SAN WASU AL'AMURAN NASU DA BA MU SANI BA. DOMIN ILIMINMU DA ILIMIN DA ALLAH YA HORE MANA KADAN NE DANGANE DA ILIMI DA HIKIMAR ALLAH, SABODA HAKA; ALLAH MADAUKAKI YANA CEWA: (KUMA BA A BA KU ILIMI BA FACE KADAN) (AL-ISRAA: 85) BA ZA MU IYA SANIN DUK HIKIMOMIN DA YASA ALLAH YA HALICCI WADANNAN DABBOBI BA, DAGA CIKIN HIKIMAR HALITTAR IRIN WADANNAN HALITTU: BAYYANA



KYAN HALITTAR ALLAH A CIKIN HALITTUNSA DA GUDANARWARSA - TSARKI YA TABBATA GA ALLAH. KUMA MAFI YAWA - A CIKIN HALITTUNSA, DUK DA YAWANSU, YANA RAYA SU DUKA, HAKA KUMA, ALLAH DAUKAKA TA TABBATA A GARE SHI, YANA JARRABAR BAYI DA SU KUMA YANA SAKA WA WAƊANDA SUKE CUTU DAGA SU KUMA SUNA NUNA ƘARFIN HALIN MUTUM WAJEN KASHE SU, HAKA NAN KUMA YANA NUNA RAUNI DA DA JIN ZAFI NA MUTUM DA RASHIN LAFIYARSA SABODA WATA HALITTA DA TAKE ƘASA DA SHI A CIKIN HALITTA, KUMA YA BAYYANA TA HANYAR LIKITANCI DA GWAJE-GWAJE: CEWA DA YAWA DAGA CIKIN MAGUNGUNA MASU FA'IDA ANA FITAR DA SU NE DAGA GUBAR MACIZAI DA MAKAMANTANSU, KAMAR YADDA MACIJIN YAKE CIN BERAYEN GONAR DA SUKE LALATA AMFANIN GONA, SANNAN KUMA DA YAWA DAGA CIKIN WADANNAN DABBOBIN MASU CUTARWA ABINCI NE GA WASU DABBOBI MASU FA'IDA, WANDA YAKE SAMAR DA DAIDAITAR YANAYI A DABI'A DA MUHALLIN DA ALLAH YA KYAUTATA HALITTARSA.

## ME YASA A KULLUM DOLE SAI NA YI SALLA SAU BIYAR A DARE DA RANA?



IBADUN DA ALLAH YA DORA AKANMU WATA HANYA CE TA TSARKAKE RUHIN MUMINI DA INGANTA RUHINSA, DUK DA KANKANTAR KOKARIN DA YAKE YI, BAN DA ALHERIN DA YAKE SAMU DAGA GARE TA, KUMA TUNDA SALLA TA KUNSHI KARATU, ZIKIRI DA ROKO, KUMA TA HADA DUKKAN BANGARORIN BAUTA A MAFI CIKAR HANYA. ITA KADAI TA FI DUKKAN WANI KARATU, ZIKIRI, DA ADDU'A; DON TA TATTARA SU DUKA TARE DA SANYA SAURAN GABBAI IBADA.

MUMINAI SUNA YIN FARIN CIKI DA SALLA; SABODA SUNA TARE DA ALLAH - TSARKI YA TABBATA A GARE SHI A CIKIN TA -, SUNA ROKON SHI DA DUK ABIN DA SUKE SO KUMA YANA AMSA MUSU, KUMA MUNA YIN SALLA; DOMIN ALLAH - MADAUKAKI - YA UMURCE MU DA YIN HAKA, KUMA A KODA YAUSHE MUNA SON YIN ABIN DA ALLAH YA UMURCE MU DA AIKATAWA, DON HAKA MUKE BAUTA WA ALLAH. DOMIN SHI NE MAHALICCINMU KUMA MAI AZURTA MU, KUMA SABODA YA CANCANCI A BAUTA MASA SABODA YAWAN BAIWAR DA YA YI MANA, ALLAH MADAUKAKI YA CE: (KUMA IDAN KUKA KIRGA NI'IMOMIN ALLAH,

BA ZA KU IYA LISSAFE SU BA) (AN-NAHL: 18) . HAKIKAWANNAN BAUTAR ITA CE KE NUNA KAUNARMU DA GODIYARMU GA ALLAH MADAUKAKIN SARKI DA KUMA TABBATAR DA BUKATARMU IZUWA GARE SHI, DON YA KIYAYE LAFIYARMU DA TAIMAKA MANA ZUWA GA ALHERI DA KIYAYE SHARRI DAGA GARE MU, KUMA ALLAH BA YA BUKATAR HAKAN. SABODA SHI MAWADACI NE DAGA GARE MU DA KUMA AYYUKAN MU KUMA BASA AMFANAR SA, KASANCEWAR IBADA UMARNI NE DAGA ALLAH WANDA YAKE SO MU BAUTA MASA TA YADDA ANNABIN SA MUHAMMAD ((S.A.W)) YA ZO DA ITA. HAKA NAN, WADANNAN IBADUN WATA HANYA CE A GAREMU DON SAMUN LADA MAI GIRMA WADANDA SUKE SABABIN SHIGA ALJANNA, HIKIMAR ALLAH TA HUKUNTA CEWA BA ZAA BA MUTUM LADA BA SAI DA AIKI, SABODA HAKA: ALJANNA KAYAN ALLAH NE MAI TSADA, KUMA TANA BUƘATAR FARASHI MAI GIRMA - WANDA SHI NE BIYAYYA.

## NA TA YIN ADDU’A A CIKIN SALLATA DON IN GIRMA DA SAURI, AMMA ALLAH BAI AMSA MIN BA?

ADDU’A TANA DA LADUBBA WADANDA DOLE NE A KIYAYE SU, KUMA DAGA CIKIN LADUBBAN ADDU’AR AKWAI CEWA MAI ROKO YA GIRMAMA DOKOKI DA KA`IDOJIN DA ALLAH MADAUKAKI YA SANYA DOMIN TAFIYAR DA WANNAN DUNIYA, KUMA MUNA ROKON ALLAH ALHALI SHI, TSARKI YA TABBATA A GARE SHI YANA YIN ABINDA ZAI ZAMA ALHERIN NE A GARE MU. KANA TAMBAYAR MAHAIFINKU KA YI WASA DA KEKE A HANYA, AMMA YA ƘI; SABODA YANA KAUNAR KA KUMA YAYI IMANI CEWA RASHIN BIYAN BUKATAR KA SHI NE MAFI ALHERI A GARE KA, KUMA DAGA KARIMCIN ALLAH MADAUKAKIN SARKI CEWA ADDU`AR MU TANA DA HALAYE UKU; NA FARKO: ALLAH YA AMSA MANA YA KUMA CIKA MANA ITA, NA BIYU KUMA: ALLAH YA DAUKE WATA MUSIFA DA WANI MUMMUNAN ABU DA ZAI SAME MU, NA UKU: ALLAH ZAI ADANA MANA ITA HAR SAI RANAR TASHIN KIYAMA. DON CIMMA ABIN DA YA FI TA A CIKIN ALJANNA.

## ME YASA BA ZAN IYA ZAMA KYAKKYAWA KAMAR KAWATA BA?

DOMIN ALLAH –MAI GIRMA DA DAUKAKA - YA HALICCI KOWA DA IRIN SURAR DA TAKE BAMBANCE SHI DA WANI, DON HAKA DUKKAN HALITTUN ALLAH SUNA DA KYAU, KAMAR YADDA ALLAH MADAUKAKI YAKE CEWA: (MUN HALICCI DAN ADAM A MAFI KYAWUN YANAYIN TSAIWA) (AL-TIN 4) . KUMA KOWANE MUTUM ANA RARRABE SHI DA TA BANGAREN IRIN HALITTARSA, WANDA ALLAH YA HALICCE SHI DA KYAWU DOLE NE YA KARA GODEWA ALLAH, WANDA KUWA BA HAKA BA DOLE NE YA YADDA KUMA YA KARBA, KUMA DUK WANDA YAYI GODIYA KUMA YA YI HAKURI YANA DA DARAJA DA LADA MAI GIRMA.

## IDAN ALLAH YANA SON MU TO ME YASA MIYAGUN ABUBUWA SUKE SAMUN MU?

ALLAH YANA JARRABAR MU; DON RARRABE MAI KYAUTATAWA DAGA MAI MUNANAWA, KUMA ALLAH YANA IYA JARRABAR MUTUM DON YA NEMI MAFAKA A GARE SHI KUMA YA KUSANCI ALLAH A KOYAUSHE, DON HAKA JARRABAWA GWAJI NE DAGA ALLAH GA ƘAUNATATTU BAYINSA. DON GWADA SU DA HAƊAKA MATSAYIN SU: DON SU ZAMA ABIN KOYI GA WASUNSU; DON WASU SU YI HAQURI SU YI KOYI DA SU. SHI YASA ANNABI ((S.A.W)) YA CE: «WADANDA SUKA FI SAURAN MUTANE TSANANIN SHIGA JARRABAWA SU NE ANNABAWA, SAI WADANDA KE KASA DA SU SAI WADANDA KE KASA DA SU.» (SAHIH AL -JAMI` (992)). SANNAN ANA JARRABAR MUTUM NE GWARGWADON ADDININSA, IDAN ADDININSA NA DA KARFI SAI JARRABAWARSA TA YI YAWA, SHI YA SA ALLAH YAKEWA ANNABAWA BABBAR JARRABAWA, AN KASHE WASU DAGA CIKINSU, WASU DAGA CIKINSU AN CUTAR DA SU, WASU KUMA DAGA CIKINSU SUN KAMU DA RASHIN LAFIYA MAI TSANANI KUMA MAI TSAWO KAMAR ANNABI AYUBA - AMINCIN ALLAH YA TABBATA A GARE SHI - KUMA ANNABINMU - YARDAR ALLAH TA TABBATA A GARE SHI - YA SHA WAHALA MAI GIRMA A MAKKA DA MADINA, KUMA DUK DA WANNAN HAKURIN –AN ANNABI TSIRA DA AMINCI SU TABBATA A GARE SHI – BABBAN ABIN NUFI SHI NE: CUTARWA TANA FARUWA NE GA MA’ABUTA IMANI DA TSORON GWARGWADON TSORON ALLAHNSU. DA IMANINSU, TO YA ZAMA DOLE A YA TABBATA A ZUCIYAR YARON: CEWA ALLAH - MADAUKAKI - YANA AIKATA ABIN DA YA GA DAMA KUMA YANA ZARTAR DA ABIN DA YAKE SO, KUMA BA A TAMBAYAR ALLAH MAI ALBARKA DA DAUKAKA GAME DA ABIN DA YAKE AIKATAWA. DOMIN SHI NEMAFI KYAUTATAWAR MASU MULKI.



**WAƊANNAN SU NE TAMBAYOYIN DA AKA FI TAMBAYA, KUMA MUNA MARABA DA KU DA KU TUNTUBE MU TA E-MAIL DON NEMAN AMSOSHIN WASU TAMBAYOYIN KO DON BA DA SHAWARWARI HANYA MAFI KYAU TA BAYAR DA AMSA (JRAKAF@GMAIL.COM).**

# KAMMALAWA

A ƘARSHE, GA WASU SHAWARWARI WAƊANDA MUKE GANIN MAHIMMANCIN SU A FAGEN ILIMI:

- YAKAMATA A KARA HIMMA WAJEN ILIMANTAR DA IYAYE; DOMIN SU NE GINSHIKAI MASU MAHIMMANCI DON SAMAR DA NAGARTACCIYAR AL`UMMA TARE DA INGANTACCEN ILIMI DA WAYEWA, TA HANYAR SHIRYA KWASA-KWASAI MASU YAWA WADANDA SUKA CANCANTA.

- TSARAWA DA SHIRYA SHIRYE-SHIRYEN KAFAFEN YADA LABARAI DA FINAFINAN KATUN DA KE DAUKE DA GINSHIKAN MUSULINCI WADANDA KE TAFIYA DAIDAI DA FASAHARSU MASU INGANCI A MATAKI NA DUNIYA DA AKE BUƘATA MASU DAUKE DA FASAHA DONIN KALLO.

- KARFAFAWA DA GUDANAR DA TARUKA DA BINCIKE A FAGEN SHIRYE-SHIRYEN KAFOFIN YADA LABARU DOMIN YARA, DON BAYAR DA GUDUMMAWA WAJEN SAMUN ABABEN DA SUKA DACE DAMU DA ASALINMU, DA KUMA SAMAR DA NISHAƊI.

- TSARA SHIRYE-SHIRYEN HORO A FANNIN ILIMIN ADDINI GA YARO, DA KUMA CANCANTAR MASU HORARWA DA MASU BA DA SHAWARA A WANNAN FANNIN NA MUSAMMAN, DON HAKA WAƊANNAN SHIRYE-SHIRYEN AN TSARA SU NE GA MALAMAI DA MASU BADA TARBIYYA A MATAKAN ILIMI DABAN-DABAN NA YARO, LA'AKARI DA ABUBUWAN DA KE CIKI BANBANCIN SHEKARU NA KOWANE RUKUNIN TARBIYYA DAILIMI.

- INGANTA TSARIN ILIMI NA HUKUMA TA YADDA ZAI HAƊA DA ABUBUWAN ILIMI TARE DA ƘWAREWA TA YADDA ZASU MAGANCE MATSALAR TAMBAYOYIN ZAMANI A BANGAREN IMANI A CIKIN INGANTACCIYAR HANYA TA ZAMANI.



مركز أصول
OsoulCenter
www.osoulcenter.com

osoulcenter
+966504442532
www.osoulcenter.com

عرض تعريفي عن مركز أصول
ومجالاته ووحداته.. مشاهدة ممتعة لك

9001
حاصل على شهادة
الاعتماد من الآيزو

حاصل على جائزة التميز
في العمل الخيري

`YA`YANKU YA KU TARON IYAYE AMANA NE AWAJENKU, ALLAH YA MUKU WASICI AKAN SU DA KU TSAYA KU KARE ABINDA ZAI AMFANE SU A ADDINI DA DUNIYA, KU KARANTAR DA SU KU LADABTAR DA SU KU KIYAYE SU DAGA BARNA KU YI MUSU UMURNI DA YIN BIYAYYA GA ALLAH DA LAZUMTAR TSORON ALLAH A KOYAUSHE. KAMAR YADDA ALLAH ((S.W.T)) YA CE: {YAKU WADANDA SUKA YI IMANI KU KARE KAWUNAN KU DA NA IYALAN KU DAGA WUTA} [AL-TAHRIM:6]. AN YI MA IYAYE WASICI AKAN `YA`YAN SU, KODAI SU TSAYU AKAN WANNAN WASICIN KO KUMA SU BAR SU SU FADA WUTAMAI RADADIN AZABA DA UKUBA TA TABBATA A KAN SU, WANNAN NA NUNI AKAN CEWA ALLAH ((S.W.T)) YAFI RAHMA SAMA DA BAYINSA, KUMA FIYE DA IYAYE SABODA YAYI WASICI GA IYAYE AKAN `YA`YA DUKDA TAUSAYIN SU AKAN SU.

IDAN TARBIYYAR YARO TA KASANCE TA INGANTA TUN ACIKIN GIDA TO ZAI IYA MU`AMALA DA MUTANEN WAJE TA FUSKA MAI KYAU,SANNAN DUK LOKACIN DA AKA SAMI WATA TAWAYA A BANGAREN TARBIYYAR YARO TA IMANI WACCE AKA GINA SHI AKANTA ZA`A SAME SHI DA RASHIN DABI`U NAGARI. TARBIYYA BA ITA CE GYARAN KUSA-KURAI BA, A`A ITA CE KOYAR DA YARO HALAYYAR ADDINI DA HUKUNCE-HUKUNCEN SHARI`A DA YIN AMFANI DA HANYOYI DABAN-DABAN WAJEN ASSASSA MAI YADDA AKE SURANTA ABUBUWA DA TABBATAR DA SU ACIKIN KWAKWALWARSA. YANA DAGA CIKIN TARBIYYA MAI BADA TARBIYYA YA ZAMA MUDUBI YA KUMA RINKA YIN WA`AZI KO NASIHA TARE DA BADA KISSOSHI NA MUTANE NAGARI DA ABUBUWAN DA SUKA FARU A ZAMUNAN BAYA DOMIN A FITAR DA INGANTACCEN MUTUM A RAYUWA.

9 786038 249369

9001

osoulcenter

www.osoulcenter.com

To Download This Book, please Visit:

OSOUL osoulstore.com